[9/7, 12:35 AM] Xarah Bukar: *Zυмa*
saι da wυтa

na
©xaraн вυkar

®Nagarтa Wrιтers Assocιaтιon {NWA)

specιal тнanкs тo sa'eed вeвejι

specιal greeтιngs тo мy вeloved sιsтo Samrah (кιna raιna кυllυм, ιlysм❤)

ғans кυyι нaкυrι da gajerun pages da zagυ ganι.

(01)

Su hud'u ne zaune cikin had'add'an office dinsa. Ko wanne sanye da kayan yan sanda, saishi na biyar dinsu dake sanye cikin Charcoal Gray and navy blue suit, kakkyawa ne mai cikar zati, kalan fatar sa wankan tarwad'a, ak'alla zai kai kimanin shekaru talatin da bakwai a shekaru. Tattauna issues suke game da ta'addanci da satan mutane dake addaban kasar gabadaya.

Sun jima suna tattaunawa, daga bisani mik'ewa sukai had'e damai sallama suka bar office din. Guntun Tsaki yaja hade da kallon wayarsa dake ruri kusan awanni da suka shud'e, hannu yakai kan desk din yadau wayar hade da dubawa, miss call biyar yagani na Aunty B da na Hajiyar su. Dafe kai yayi cike da tsananin takaicin sanin dalilin kiran. Tsaki ya saki had'e da janyo side drawer na desk din ya fiddo file mai rubuce da sunan Ummi ajiki da stamp din missing daga sama, bud'e file din yayi yanai dubawa yaji an turo kofar office d'in, bai dago ba yacigaba da zabgarsa.

Kyakyawan saurayine mai kimanin shekaru talatin da uku ya shigo, bai karasa ciki ba ya tsaye bakin k'ofar, fuskar sa ba walwala.

"Morning sir"

Ya furta atakaice.

Ba tare daya dago ba.

"Salim Abbas right ?

"Yes sir"

Salim ya amsa cike da haushin yadda ya ambaci sunanshi cikin salon rainin wayo.

Saida ya jima sannan ya Dago ya kallesa, wani mugun kallo ya aikawa mai.

"hope you're clean, kasan i dislike working with drunkard"

Kasa magana Salim yayi zuciyar sa na tafasa, ya mugun tsanan Ogan shi ba kad'an ba, banda 3 weeks suspension daya bashi ya dawo kuma yana neman wulakantashi.

Bai hankalta ba yaji ya cigaba da magana. "kana iya komawa position dinka, amma kasani next time it won't be 3 weeks but a whole life time".

Juyawa Salim yayi ya fice daga office d'in batare dayace kanzil ba banda tafarfasa da zuciyar sa yake.

Shi kam gogan cigaba yayi da duba file din, hotunan Ummi dake ciki yad'au yanai dubawa, kallon k'urilla yakema hoton da tunanin ina zai nemota, asalima she is 10 years a hoton. Acewar hajiya kuma zatakai 19 by now. Saidai babban takaicin sa bai wuce ta ina xan fara binciko taba, a iya sanin sa a Gombe ta b'ata ba Abuja inda yake aiki ba. Rufe file din yayi hade da maida ta cikin drawan sannan ya mike ya fice daga office din. Inda maajiyar motarsa kirar formatic 350 ya nufa ya shiga sannan yama Aunty B text msg na gayanan zuwa. Jan motar yayi bai zarce ko ina ba sai gidan su dake Asokoro na cikin garin Abuja.
***
Shingid'e dattijuwa Hajiya Laurat take bisa lausassiyar doguwar kujeran palon, hannuta rike da waya tana sauraran kiran d'anta da tun daxu take danna mai kira baya picking. Babbar diyarta Aunty Bilkisu ta fito daga kitchen hannunta rike da mug tanai kurban shayin dake ciki, karasa shiga palon tayi tanai kara duban agogon hannuta hade da takaicin rashin karasowa Mujahid, gashi kuma tana da patience dake jiranta a asibiti.
Zama tayi kusa da Hajiya hade da kwantar da murya tace,
"Hajiya a hakura kawai, wanan wahala ce kawai zaki d'aurawa Mujahid, yarinyar nan fah dakanta tabar gidan Ubanta, babu wanda ya koreta, gaskia nidai banga amfanin nemo taba.."
Mugun kallo da Hajiya ta watsa mata yasa tayi azaman tsuke kalamanta.
"Bilkisu ki kiyayeni, na dauka kece babban mai hankali ashe baki da hankali, shiyasa duk cikin ku Jafar yafi yemin, shine kadai ke fahimta ta"
Shuru Aunty B tayi ba tare da tace kanzil ba, saima tsumu tsumu da tayi kamar wace aka tsamo cikin ruwa. tasan halin tsohuwar su yanzu saita dau zancen da zafi ta inda take shiga ba tanan zata fita ba.
Daidai bakin k'ofar palon ya tsaya chak sakamakon kalaman Hajiya na karshe daya tsinkawo a kunnuwansa, sallamar daya ke kokarin yi kasawa yayi jin tanai magana cikin daga murya da fusata.
"Muddin bai nemo Ummi ba saina mugun b'ata masa rai, tun yaushe mukai zancen dashi amma har yau babu feedback kuma lokaci na tafiya burina kawai ta bayyana na hadashi aure da ita"
Tashin hankali da firgici ne suka bayyana a fuskarsa, ji yayi gabadaya jikin ya sank'ame kamar jini bai zagayawa cikin jijiyoyin jikinsa. Dakyar samu karfin motsawa,
ahankali ya fara taku baya sannan ya juya da azama ya koma inda yayi parking motarsa ya tsaya hade da dafe kanshi.
Ruwane ya cinye Aunty B da mamakin kalaman Hajiya, Ummi data baiwa iskanci baya shine Hajiya take kokarin kakkab'awa kaninta, duban hajiya tayi, ganin lailai ba wasa take ba yasata fara kirkiro murmushin dole.

Dafe yake da kanshi kaman xaiyi kuka, gabad'aya Hajiya ta daura mai zafi, bai taba yadda Hajiya batason shi ba sai yau dayaji abunda take shirin aikatawa. Sai dai yayi alwashin hakan bazai faru dashi ba, harga Allah yana da niyya nemo Ummi saidai kudirin Hajiya yasanya bazai nemo taba saidai ma yayi fatan duk inda take a dosar kasar kar ta bayyana. Hannayan sa biyu ya hada had'e dakaiwa glass din motar noushi cikin fusata yanai huci. Horn din mota dayaji yasanya shi waigawa kallon motar data danno kai cikin gidan.
"Ya salam, from one Problem to another" ya fadi aranshi hade da saurin kawar dakai gefe tamkar bai ganta ba, cikin ranshi addu'a yake Allah yasa karta iso garesa.

[9/7, 12:37 AM] Xarah Bukar: *Zuma*
sᴀɪ da wᴜтa

na
©xaraн вᴜкar

{02}

Murmushin jin dad'i ta saki sakamakon ganin shi da tayi, taso su hadu da safe kafin ta tafi skull saidai tuni ya rigata sammako.
Gefen motarsa tayi parking motar ta kirar corolla xL sanna ta fito, jikin ta sanye da uniform din Premiere acedemy, short gray skirt da white long sleeve mai hade da maroon necktie.
Da murmushi ta doso shi, ganin ba fuska ya sanya ta shan jinin jikinta, gabanta na dukan uku uku.
"Ina kwana ya Mjay
Mugun kallo ya aikamata tare da kara shan magani.
"Da ban kwana ba zaki ganni anan"
Tsura mata idanu yayi jiran amsarta.
Kai ta girgiza.
"Naga kaman ranka abace.." Tayi shuru idonta ya ciko da kwallah
Gyara tsayuwar sa yayi hade da kokarin bude kofar motar yana fadin.
"bana hanaki shiga hurumi naba, waiku matan nan miye matsalan kune".
Guntun saki yaja cike da takaici yadda mata ke bada kansu, balle yar karamar yarinyar dake tsaye gaban sa, shiyasa har ilah baiga perfect woman data dace dashi ba.
Marairace murya tayi tace "yaya kayi hakuri, am not happy da yadda na ganka ne.
Tsaki yaja, tsayawa mata magana bata lokaci ne, shigewa yayi motar hade da janta yabar ta nan tsaye jiran tsammani.
Sakin baki tayi tanai kallon motar harta fice daga gidan, Kaman zatayi kuka ta wuce Jiki sanyaye ta fara takawa cikin gida. Duk a gaban ido Jafar, daga windon saman dakinsa ya hango draman su, tabe baki yayi, aranshi yanai fadin duk shishigi da takemai bashi zai hana ya gwasaleta taba, cusa kai ba kwarjini. Daukar wayar sa yayi ya fito daga dakin hannusa rike da briefcase da suit jacket, cikin sauri ya sauko daga stair din, inda Hajiya take ya nufa hade da mata sallama daman tuni tasan da tafiyar sa kaduna akan wani case dinsu can na kare hakkin mutane, addu'ar saukar lafiya da fatan alkhairi tahau zuba mai, Aunty B kuwa shuru tayi gudu kartace wani abun tasha fada.
"Aunty kina nan ashe baki wuce ba" Jafar ya fadi.
"Yayanka ya shanyamu, nima tashi xan na wuce" Mikewai tayi tana ci gaba da fadin "hajiya nikam na wuce aiki, sai wani zuwan"
"A sauka kalau, ina gaida yaran" acewar hajiya cikin kota kula da yanayinta.
Daidai Bakin kofar sukayi kicibis da ita zata shigo, ganin aunty B yasata sakin fara'a hade da gaidata.

Cike da faraa ta amsa mata hade  dacewa "Junaina harkun tashi so early"
"Aunty yau bamu da exam, chilling da friends ya kaini skull, gajiya nayi na dawo, mun kusa ma gama Waec din"
Aunty B tace "Allah ya baku saa.." Cikin saurin tayi maganar sakamakon wayarta data shiga ruri, hannu ta daga mata hade da ficewa tanai kokar daukan call din, Sai sannan ta lura da Jafar dake tsaye yanai kallonta, da alamun bashi da shirin yi mata magana.
"ya Jafs sai ina haka rike da briefcase" ta fadi hade da karasawa ciki, zama tayi kusa da hajiya cikin salon yauki da shagwabe fuska..
Yace "idan kinason sani ki kirani awaya" ficewa yayi batare daya jira cewar taba.
Kaman xatayi kuka ta kalli Hajiya tace "Hajiyata waini miyasa su yaya keson kwasaleni, ya jaf da mukafi shiri saikiga wataran ya canxa min".
Dariya hajiya tayi.
"banda ke Auta idan sun kwasaleki, saiki fita batun sun kema ki sharesu"
Kai ta girgiza.
"Gaskia bazan iya share Ya mjay ba koda ma ace zaiina dukana kullum"
K'ura mata ido Hajiya tayi cike da mamakin abunda Junaina ta fad'a.
Aranta tace "Auta mujahid ya miki nisa, wannan yarinta gwara ki ajiyeshi gefe".
Afili tace "bansan shirme tashi maza kije ki cire uniform" shagwabe fuska tayi hade da turo baki.
"Kai hajiyata daga magana sai korata awayance"
Harara hajiya takai mata ba shiri ta mike ta wuce dakinta dake nan kasa.

****

Reckless driving da take bisa titin ya sanya mutane da dama da suka san ciwon kansu matsawa gefe sunai bata guri. Gudu take shantakawa iya san ranta hade da kyalkyale dariya ganin yadda kowa ya bata sarari, daidai data karaso traffic light ya nuna red, dogon tsaki taja tayi gaba ba tare data tsayar da motar ba.  Bata ankara ba kiris ya rage ta bugi motar data danno, cikin kota kula da abunda ya faru ta fizgi motar at 360. Gudu take sosai can ta lura da motar data kusan bigewa na biye da ita, tsoro ne ya kamata kasancewar last week kadai Daddy ya gargadeta da reckless driving,  bata daddara ba kuma takeyi, fatan ta Allah yasa ba yan road safety bane, dan dakyar daddy ya amso mata motar ta da sukayi seizing kwanakin baya.

Yadda take sharara gudu haka yake binta a baya, baisan waye acikin motar ba amma yayi alwashi koyawa koma waye lesson, dama ranshi a bace yake yasamu scape goat dazai huce haushi akanshi. Ringing din wayarsa ce ta katse mai hanzari, murmushi ya saki ganin wacce take kira, dauka yayi hade da sakawa a speaker.
"Fa'iza am driving, zan kira ki later.
Tace "Mjay karka manta by 2pm zaka zo dauka na".
Bata rai yayi yace "you know am not your driving, kuma am not a jobless man, bazan iya zuwa ba ki shiga cab" katse call din yayi but deep down yasan dole yaje yayi picking dinta bayason tana shiga motar haya. Kaman kiftawar ido yaga wayam  babu motar dayake bi, dukan sitiring yayi hade dayin U turn ya kama hanyar komawa office.

Ajiyar zuciya ta sauk'e ganin motar dake binta tayi gaba, ahankali tayi reverse ta fito daga

supermarket inda ta shiga tayi parking, da gudu ta kuma fizgar motar, Karar shigowan msg wayarta tayi, da azama ta duba.
"Salma kiyi sauri, Malama Fa'iza ta karaso, da alamun zata dau Attendance"
Dogon Tsaki taja hade da duba tym, 12 to 2 suke da lecture dinta, amma dan maita stupid malamar harta shiga hall just 12.05, koda yake daidai take da ita. Wani mugun wuta ta baiwa motar, bata zarce ko ina sai gwagwalada Abuja.

Cute xara'u 😘
[9/7, 12:37 AM] Xarah Bukar: [18/07 12:25 PM] aυnтy cute xaraн :
*Zuma sai da wuta*

~na~
©ӽaraɧ bųkar

Masu k'orafin pages sunyi kadan kumin uxuri, kuyi manaji da iya abunda xan iya baku. Idan nasamu lokaci zan kara hannu.

*Wannan shafin Naku ne House of novella da dandalin makaranta, Nagode matika da kaunar ku, ILYA*❤

3 - 10

Parking tayi daidai multi purpose hall inda suke da lecture. jakar ta dake ajiye gefe ta dau ta fiddo kayan kwalliya ta kara gyare fusk'ar ta dashi sannan ta bud'e kofar ta fito, cikin tsadaf ta fada ajin gudun kar Malama Fa'iza taji shigowarta kasancewar gabad'aya hankalin ta na bisa allon datake rubutu, kallon banza yan matan ajin suka bita dashi, bata damu ba ta karasa inda maza sukafi yawa ta zauna a sit dinta da tuni sun kama mata.
Murya kasa kasa, abokinta na gefen ta yace
"Salma yau mutumiyar ki rashin kirki take ji, ta hana kowa rubutawa wani attendance"
Ajiyar zuciya ta sauke, zatayi magana kenan, Fa'iza ta juya tanai fadin sunan topic dinsu na yau, hada ido sukai tayi saurin mazewa kaman ta jima da shigowa ajin.
Cikin rashin damuwa da ganinta Fa'iza ta cigaba da lectures dinta, tana gamawa tahau kiran attendance d'aya bayan d'aya bayan ta gargardi kar wata shegia ko shege ya bita office k'orofi, tana gamawa ta fice daga ajin.
Dariyan takaici Salma tayi, sam bataji haushi ba saidai shegia data ambata yay mugun b'ata mata rai tasan kuma babu tantama da ita take, tunda kowa was present banda ita.
Ko hira bata tsaya yi da abokanta ba, ta koma motarta taja ta at 360, department dinsu ta zarce ta fito tashiga ta tsaya bakin kofar office dinta. Hannu takai bisa kofar taji ta a bude, tsulem ta fada tanai karewa ko ina kallo sannan ta zauna tanai kallon hoton wani guy dage jikin frame

akan table din. Hannu takai zata dauka taji motsi mukuli a kofar, adan tsorace ta duka kasa hade da boyewa under table.
Tsaki fa'iza tayi
"garin sauri ashe ban rufe kofar ba" ta fadi.
Turo kofar tayi ta shigo ta ajiye jakarta sannan ta shiga toilet dauro alwala.
Mik'ewa tsaye salma tayi cikin sauri tadau biro dake gurin ta rubuta "ba wani shege kowa da uban" ajikin wata takarda dake gurin sannan ta sure frame din hoton tayi waje ahankali, da gudu ta karasa cikin motar ta hade da sauke numfashi tanai kallon hoton, guy din bai wuce 36 ba, saidai kuma yayi wa Fa'iza yaro idan ma ya girme ta kadan ne
"Shi kuma wanan ya rasa waxai aura sai tsohuwar nan, lailai malama dole kanki yayi hayaki"
Surutai tahau yi ita daya.

Bangaran fa'iza kuwa, tana fitowa sallaya ta shimfud'a tahau sallahn azahar bayan ta idarne ta koma kujera ta zauna saidai wayam babu hoton data saba kalla akullum idan ta zauna, baza ido tayi tana nema taci karaf da abunda ke rebuce, mamaki sosai ya kamata tahau cigaba da duban hoton, zuciyarta na zargi wani abu rashin tabbatar wa yasa ta kawar da tunanin.

Karfe 2 da minti goma ya karasa makarantar, parking yayi a gaban department dinta sannan yadau waya kokarin kiranta.

Jakarta ta zuge ta cilla frame din ciki, sannan ta juya yin reverse, Motar dazu dake binta tagani ya rufe mata baya, guntun tsaki taja hagonsa zaune cikin suit batare da jacket dinsa ba, kansa sunkuye yanai duban wayarsa.
"kut ashe ma ba officer bane, naketa kokarin boye kaina, am sure sona yake datx y yaketa bina, aikuwa xan koyamai hankali"
Dogin tsaki taja had"e da bud'e kofar afusace.
Yana zanune yaji ana buga mai glass, bai dagoba sai wining glass kasa da yayi dan gabadaya hankalinsa nakan nambar Faiza dayake kokarin turama sakon ya iso.
"Uban wayace ga dinga bina duk inda na ratsa, ko an gayama so dolene, ko kuma ma dai ince Saceni kekeson yi dan kasamu kudi"
Ta fada cikin karaji da zare idanu,
Chak yayi da wayan ahannu, bai iya dagowa ba saboda kalamanta dayaji bambara kwai wai So, shi idan akwai abunda ya tsana bai wuce kalmar so va balle soyayya, who d hell is she dazai ma sota balle ya bibayeta, bai gaba zancen zuci ba yaji tana fadin.
"Kodayake nasan maganin ka, am calling the police saina ga ubanwa ya tsaya ma" wayarta dake aljihun wandon ta tadauka tafara dailing namba.

Shikam gabadaya ya gaba fusata, ba namijin daya taba mai cin zarafi irin haka balle mace, mata daya daukesu kanana k'wari wanda daga kuka banza sai shagwaba suka iya, murmushin dayasan munafarsa ya saki, sannan ya turawa faiza sakon ta fito nan da 30 min, dan kuwa zaman jiran dan sanda da zaizo arresting dinsa xaiyi.

Matsawa gefe Salma tayi tana wayan.
"Ya salim dan Allah karka jima, kayi sauri ka karaso kafin ya gudu.
Yace "Pretty  karki damu, yanxu zaki ganni, make sure kiyi keeping dinshi bizi kafin naxo".
"I'll' tafadi.
ta katse wayan.
Maida dubanta  tayi garesa, saidai har yanxu ta kasa tantance fuskasa dake duk'e, kuma window ma yayi wining dinta sama.
"Laila ma mutumin nan, mugun nan rainin wayo ne, tayama xanyi keeping dinsa busy alhalin baima kallo ni" tsaki taja tahau safa da marwa a gurin.

"Bari ma dai na kalli useless girl dinnan"
ya fadi aransa, juyawa yayi ya kalle ta, yarinya ce da iyakacinta 18 to 19, kyakyawa black beauty, jikinta sanye da white pencil jean da red top, da rad hulan yemi alade daure bisa kanta, kai komo take tanai duban agogon hannuta.
Mugun tsaki yaja hade da dauke kansan, he cnt believe abunda ke faruwa, amma yarinyar ta gaba dashi da irin insult data mai.

Tana ganin Motar Salim ya iso ta sauke numfashi, fitowa yayi tayi sauri karasawa gareshi, hade da kaimai hug
"Thank God yaya ka iso on tym" ta fade cike da murna.
Janyeta yayi yace "keda waye, miya faru ?
Hannu tasa natai nuna mai motar tana tab'e baki.
Duban motan yayi, atake yasha jinin jikinsan ganin motan Ogan sane.
"La'ilah mai salma ta tsokano mai yanxu" ya fadi aranshi.

Shikam Mujahid ganinsu ta side mirrow yasa shi kara daure fuska hade da fitowa yana masu mugun kalloi, hararar sa Salma tahauyi sai sannan tagano Guy din cikin frame din ne, mijin tsohuwa Fa'iza atunanin ta, saidai dalilin dayasa yake binta shine bata sani ba, kallon Salim tayi da tuni yayi tsuru tsuru tace
"what are you waiting for, kayi arresting dinshi mana"
Karasa wa gurinsa Salim yayi, hade da risinawa yace
"Sir kayi hakuri, kanwa tace ay mata uxuri"
Girgiza kai Mujahid yayi yace,
"atunanin you are d useless person a family dinku ashe dai kana da kanwa data fita zama useless and shameless"
Shuru Salim yayi yasan hakan zata kasance.
Salma kam tagama fusata da abunda yace, tace "i tink you're d shamless person here, jibeka sanye da suit kaman mutum arziki,
Sauri rufe mata baki salim yayi
"Plz salma kiyi shuru
Cire hannusa tayi cikin masifa tace "haba yaya kanaji yana xagin mu, who the hell is he, dan kawai shida matarsa suna aiki saisu nemin raina mutane, or do they tink d world revolve around them"

Janye ta salim yayi sauri yi, yanai bawa mujahid hakuri, saidai kasan zuciyan shi yaji dadi yadda Salma ta mayar mai magana, suna cikin haka Fa'iza ta karaso
"Mjay make faruwane"
Nuni yay mata da hannu ta shiga motar sannan shima ya shiga, ran shi ya gaba bacci.
"Ban taba sani apart from student akwai dabbobi anan ba"
Kallon Salma tayi dake tsaye gefe Salim na bata baki,
tace "miya faru"
Yace "stupid gal din ta dauka sonta nake, dan kawai munyi crossing path daxu da yanxu"
Tsaki faiza taja tace "Salma Abbas maccido, ai sam yarinyar bata da kunya ga bin maza, ina zargin ma barauniya ce
Tayar da motar yayi yace "mita sace maki"
Shuru Fa'iza tayi dan kuwa bata da evidence tunda bata ganta ba, amma tana zargin itace.
Tace "haka naji wasu student na fadi.
Tsaki yaja ya figi motar hade da buda masu kura ya wuci, rikota Salim yayi yace "salma cool down mana, so kike yasaki a prison, babban police nefa".
Kaman xatayi kuka tace "and so, wana law ne yace yamin rashin Mutunci".
Masifa sosai salma tahau dakyar Salim ya lallbata ta shiga motar ta taja yanai biye da ita a tasa motar har suka isa gida hadaddan gidansu dake Asokoro.
Suna isa momy ta iske zaune a palo, da gudu ta karasa gurinta fuska ba walwala.
"Yau kuma wace tsokana kika iyo"
Gunguni tahau yi
Salim yay mata bayani.
Haushi ne ya kama Mom tahau ta da fada, "nikam nagaji da fitinar ku, yau salim kaine gobe kuma itace, bari dai Daddy yadawo".
Hankalin Salma ne ya tashi tana mugun tsoro fadan Daddy, shiyasa akodayaushe take kaffa kaffa, hakuri tahau ba Momy kamn xatayi kuka, dakyar mom tA hakuri tanai tsokanan ta maganinta Daddy.

Banda Zagin salma ba abunda Fa'iza take a motar har suka isa gidansu dake Garki 2,
ya ajiyeta
Yace ki tabbata motar ki an gyara nagaji da zama driver dinki".
Murmushi tayi tace "ba damuwa sai munyi waya"
Bye tamai sannan yaja ya koma office shidai Gida nedai bazai jeba.,( ni xarah nace xaka hadu da Hajiya)

Tana shiga Gida, Umma ta fake ta da Ido alamun tuhuma, sanna tace
"Faiza idan yaron nan sonki yake ya turo ayi magana, nagaji da wannan dangantakar taku, kusan shekaru ashiri kuna tare kinyi aure harkin fito kuma still kuna tare idan sonki yake ya turo.
Shuru Fa"iza tayi, ita kanta tarasa meke cikin zuciyar Mujahid, tun suna secondary skul suke tare as friends har yau kuma banda wanan bataga alamu love ba, tace
"Umma bafa saurayina bane abokina ne, kuma ma shifa babu so aranshi"
Kwafa umma tayi
"Karyan banza, duba fah yadda yake ji dake, ko gidansu ansanku tare, wa zaku rainawa

hankali"
Faiza kam bata iya cewa komai ba ta wuce ciki, Allah yaga zuciyanta tun kafin auranta na farko takeso mujahid ganin bashi da niyya yasa tayi auranta gashi ta fito ba abunda ya canxa.

***
[9/7, 12:37 AM] Xarah Bukar: *Zuma sai da wuta*

~na~
©ӽaraђ bųkar

Happy birthday *Billy Galadanci*, Wishing you more perfect years ahead, its you day Have fun 🎈

*Wannan shafin naku ne, Hauwa shehu, maman safara da Aisha ture nagode matika da soyayyar ku gareni*

Wishing you safe trip to Birnin shehu, Feedoh Deedoh (Aunty yar ficika 😜), kina isa kuma ki aikomin da Matata gimbiyata, Sannan ki biyo ta gida Muci Rengem 😋😋😋😋😋

11 - 14

**
Cikin kayan yan sanda yayi shirin sa tsaf sannan ya sauk'o k'asa, jin shuru a palon yasanya shi ficewa waje da azama gudun kar hajiya tasan da fitar sa dan kuwa wasan b'uya yake da ita, adaran jiya ma cikin tsadaf ya shigo gidan yaci sa'an Hajiya ta jima da bacci.
Duk akan Idon Junaina dake tsaye ta window kitchen tana kurban tea, jikin ta tsaye da uniform na makaranta. Ajiye mug din tayi tama mai aikin su Lami sallama sannan ta fito waje haraban gidan inda motar ta ke ajiye, shi kuma alokacin yake kokarin tayar da tasa.
Murmushi yayi ya dubeta.
"idan bazaki damu ba kizo nayi dropping dinki"
Kallon gefen ta tayi dan kuwa batai tunanin da ita yake ba, ganin ita dayace yasa ta gano da ita yake.
Farin cikine ya cikata.
"Da gaske yaya.."
Kai ya d'aga mata, da sauri ta zagaya ta shiga ta zauna fuskar ta dauke da murmushi.
"Yaya ina kwana"
Ta fad'i.
Bai amsa ba yace,
"Hajiya bata ce maki komai jiya ba"
Kallon rashin fahimta tamai.

"wana abu kenan"
Daure fuska yayi yace ba komai sannan yaja motar.
Tace,
"ya Mjay zaka dawo daukana kenan
"A'a"
Ya fad'i atakaice.
Kallon shi tayi kaman zatayi kuka, aranta tanai takaicin gwanintarsa na kaita skull alhalin ba dawowa daukar ta zaiyi ba, kodayake ta riga ta gano shi, bata da wani amfani agurin sa sai yana neman information gurinta yake bata fuska.
Basu kara magana ba har suka isa premier Academy babu wanda yace uffan.
Sauka tayi motan, kafin takai ga mai magana yaja motar yayi gaba.
Guntun tsaki taja.
"Baima damu da yadda zan koma gida ba" aranta tayi maganar.
Murya k'awayanta taji abaya sunai kiranta, sauri sakin fuska tayi hade da sakin murmushi ta juya kallon su, kawarta Hameeda tace
"wow badai shine sweetheart dinki ba, gaskia ya hadu acikin uniform".
Dariya Junanai tayi aranta tana tunanin yadda zaici ubanta idan yasan da sunan sweetheart dinta kawayanta ke mai nuni.
Share zancen tayi taja hannusu suka shiga ciki.

Yana isa NPF (Nigeria police force Q), parking yayi ya fito k'arasawa dept dinsu ya hadu da abokin sa kuma abokin aikinsa Mubarak. Gaisawa sukayi har zai wuce ya tsaya yace.
"Mubarak nasan kasan manyan mutane agarin nan".
Dariya Mubarak yayi yace "ka shirya aure kenan, diyar wace ce yanzu nama hanya"..
Tsaki Mujahid yayi.
"Kaima kasan babu wanan a lissafina, kasan wani babban mutum Alhaji Abbas Maccido a agarin nan ? Ya fada, dukda baisan waye Alhajin ba yasan mai kudi ne ganin motar da shameless daughter dinsa ke driving.
K'ad'a kai Mubarak yayi yace
"nasan shi, babban dan canji ne (Burea de change) mai kudin gaske wanda anjima ana damawa dashi"
Numfashi Mujahid ya sauke.
"Good, inason details din komai game da family members dinsa, And plz make it Quick".
Cigaba yayi da tafiyan sa batare daya jira cewar Mubarak ba.
Dariya Mubarak yayi ya wuce, aranshi yana adduan ko abokinshi ya fara sanya So aranshi.

***
Yau lecture free day, ko wanka batayi ba ta fita palo yin breakfast, wanda k'idar gidan ne dole by 8am a hadu dining yin breakfast kafin nan kowa ya wuce zabgogin sa.
Kayan bacci ne jikinta riga da wando cotten,  gashin kanta baje babu kallabi, Su biyu ta tarar zaune kan dinning taja kujera ta zauna hade da yin mik'a da salati sannan ta kalli iyayan hade da k'ok'arin fara had'a tea.

"Dad n mom good morning"
Kunnan ta Mom ta rik'o tace,
"Salma bana hanaki fitowa da Nyt wear ba, idan Salim ko wani ya ganki haka fah".
"Kai mom bacci fah xan koma idan na gama"
Katse su Daddy yayi da cewa, "yau baki da lectures ne ko wani bak'in halin kikayi aka koroki " fuska daure yayi maganan.
Shagwabe Fuska Salma tayi, aranta tanai fadi "Daddy dai zancen shi kullum makaranta, kuma ma babu wanda ya isa ya koreni, i can defend myself".
Afili tace "Daddy bamu da lec yau, sai gobe muke da Math 105"
Yace "Good, make sure kiyi revising kafin kiyi bacci".
"Yes, Daddy" ta fada tanai dariya kasa kasa.
Mik'ewa Daddy yayi sannan ya kalle ta yace "ki zauna a gida, banso na dawo daga office naji labarinki in some kind of trouble"
"Okay Dad, Allah ya dawo dakai lafiya"
Ta amsa.
Murmushi yayi sannan ya wuce, mik'ewa Mom tayi hade da kai mata duka tace "kin daiji abunda yace wlh Salma ki kiyaye ni"
Dariya tayi.
"Momy mi nayi kuma".
Harara mom takai mata sannan ta juya da azama tabi bayan Daddy rakashi bakin mota.

Kad'an ta iya cin abinci ta tashi ta koma Daki, jakarta ta jiya ta fiddo daukan handout dinta taga frame din hoton sa, Dogon tsaki taja, harga Allah ta manta da hotonsa a jarkarta, wani mugun haushin sa taji tunawa da yadda ya zage su jiya. Daukan Frame din tayi ta ajiye shi kan Console daidai inda hotonta dana Momy ke ajiye, harara hoton tahau yi taji an turo kofar dakin an shigo, da sauri ta kife frame din sannan ta juyo adan tsorace, ganin wanda ya shigo yasa ta daure fuska.
"Ya Salim miye haka, jifa yadda ka tsorata ni ko sallama babu ka fadomin daki"
Karasawa yayi ya tsaya gabanta hade da kai hannu bisa gashin kanta yanai shafawa.
Yace "ai nanma dakina na, yaushe kuma kika tsiro da sai nayi sallama zan shigo"
Hannu yakai kan habarta hade da dago fuskan ta sunai fuskanta juna, yacigaba "Miye kike boyewa bakya so nagani, kinsan dai no Secret tsakanin mu"
Janyota yayi jikinsa yanai kokarin hade bakinsa da nata, tayi sauri matsawa gefe hade da kara tamke fuska
"Oh yaya plz stop it, you're getting too close"
Hannu ta ya riko yace
"Just a kiss saina tafi, kinga babu wanda ya ganmu".
Takaici ne ya kamata
"Why cnt you understand, i don't have any feelings for you, tayama zan yadda kayi kissing dina cikin gidan iyayena adakina for dat matter"
Idon shine ya fara sauya launi, yace "karya kike salma, duk yadda kike hugging dina muke holding hands sannan kice baki da feelings, i know you love me kawai bakya son nuna wane".
Dafe kai tayi cike da takaicin abunda yace.

"I swear i dont love you kaman yadda kake tunani, d only people i love sune Daddy, mom n you, plz ka bini ahankali kar love din yan'uwantaka da nake ma ta koma Hatred"
Kaman zaiyi kuka yake kallan ta, yace "Salma ina sonki"
Dauke kai tayi gefe, yayi gaba zai wuce tayi saurin rikon hannu shi ya juyo suna fuskanta juna.
Tace "yaya am sorry, babu so araina dan Allah karka ji haushi na"
Murmushi dabai kai zuciya ba ya kirkiro yace "ba komai, i hope randa kikasa so aranki ni zaki so".
Dariya tayi, dan abune ne mai wuya, tace "yaya by 9pm idan ka dawo aiki, zamuje Officers club chiiling, zaman gida ba dadi"
Ware ido yayi, yace "ba ruwana, kinsan dai Daddy ya hanaki fitan dare"
Shagwabe fuska tayi tace "don't worry satar fita zanyi yadda bazai gane ba, ko kuma nazo part dinka na boye idan yayi bacci sai muje"
Dariya yayi yace "nice idea, nizan wuce office, am getting late"
Hannu shi ta saki tace okay bye"
Sannan ya fita sukayi kicibis da momy a palo, kallon tuhuma tamai dan tuni ya riga kowa breakfast yace ya tafi ashe yana nan.
"Mom agogona dana bata ajiye naje karb'a" ya fadi cikin muryan marasa gaskia.
K"wafa Mom tayi batace komai ma ya fice cikin sauri.

****

Bayan Magrib Mubarak yasamu daman harharda Details din, zaune yake a office din yana dannan laptop din gabansa saidai rabin hankalinsa yayi gida, sarai yasan yama Hajiya laifi amma taurin kai bazai barshi yaje ya fuskan ceta ba.

Knocking Mubarak yayi ya shigo bayan anmai izini, zama yayi kujeran bak'i yana murmushi ayayinda Mujahid ya daure fuska yanai mai kallon dami kazo.
"Kwantar da hankalin ka nasamo ma komai akan Family din Alhaji Abbas Maccido"
Gyara zama Mujahid yayi yanai duban sa.
Mubarak yace "Alhaji Abbas matar sa daya Hajiya Zaituna da kuma diyar su tilo Salma, da wani saurayi da suke rike dashi a gidan tun yana yaro Salim ne sunan shi"
Anzo gurin, k'ad'a kai Mujahid yayi, sai yanxu yagane ashe Salma da Salim ba siblings bane, saidai akwai wani abun dake tsakanin su ganin yadda sukai ta mannewa juna jiya.
Duban Mubarak yayi yace "baka da komai akan Salma".
Kashe mai ido Mubarak yayi yace "kodai kana ciki ne, kaga yar kyakyawa ka susuce"
Tsaki yaja, aranshi yanai mai zaiyi da Bak'ar karuwa.
Afili yace,
"baka amsamin tambaya taba"
Nisawa Mubarak yayi "Ba wani abu akanta, tayi secondary skull dinta a London, uban nata yaso tayi jamiar acan taki zama fir ta gudo Nigeria, uban nata sam baya wasa da karatun ta, yanxu dai nan gwagwalada take 100 level"
Jinjina kai Mujahid, yayi yanai zancan zuci.
"Tabbas biri yayi kama da mutum, sam yarinyar batta da tarbiyya amma yayi alkawari koya

mata hankali da samun tarbiyyan da ubanta bai bata ba"
Sun jima suna magana daga bisani Mubarak ya fice daga office din.
Mikewa Mujahid yayi ya tattare komai gefe sannan ya fito, parking lot ya nufa ya hadu da Salim shima zai shiga motarsa, wani kallon suka aikawa juna dani kaina ban tantance kallon miye ba sannan kowanne su ya shiga motar sa yaja.

Tuk'i Mujahid yayi yana tunanin yadda xai rama wulakanci da Salma tamai, danya lura ma kallon banxa Salim yamai daxu duk akan rainin da salma tamai agabansa.
Sallah ishai da yaji ake kira yasa yayi parking a gefe hanya ya shiga masallacin dake gurin, bayan ya fito ne ya tuna da Junaina, wayarsa ya fiddo ya kirata, alokacin kuwa tanai zaune tare da Hajiya a Palo suna hira taji kirar sa.
Dauka tayi ta mike hade da matsawa can gefe da ita
"Yaya kana ina, daxu naji Hajiya da Aunty Bilkisu suna waya, kuma kaman zancen kane, hajiya nata fada.
Dafe kai yayi, yace "kin dawo gida ne "
Haushi ne yakamata, sai yanxu ya tuna da ita, tace "eh nadawo".
Katse call din yayi ba tare dayace komai ba, kallon wayar tayi kaman tayi ihu, jiki sabule ta koma ta zauna.

Tsaki yaja hade da kallon agogon sa, takwas da rabi na dare, muddin yaje gida yanxu xai hadu da Hajiyarsa, shawara ya yanke na zuwa Officers Club kafin sha daya ya koma gida, yasan by dat tym tuni Hajiya tayi Bacci.

Nima xarah nace na tayi yin wanka kafin mu hadu Officers Club🏊🏾‍♀️🏊‍♀️🏊‍♀️🏊‍♀️
[9/7, 12:37 AM] Xarah Bukar: *Zuma Sai Da Wuta*

~na~
©ӽaraɧ bųkar

®NAGARTA WRITERS ASSOCIATION

Fatan Alheri gare ku Nagartattu.
Benaxir Omar
Lubie maitafsir
M jabo
Futha lurv
Biebee Isa

Queen miemee
Jeedah Aliyu
Fiddausi Sodangi
Miemee bee
Mom Fatee
Khadeeja Candy
Pharty BB
Mr umar
Mamu
Deeja Abdul
Asee B Aliyu
4 Stars
Raz
Safha
Da duka wanda ban ambata ba.

*Jinjina Ga kawata Zuwairat (Umm Maryam) Allah ya kara basira da kaifin Ido*.
*Ayusher*
*Sumayya Salees Sadeeq*
*Billyn Abdul*
*#Ana tare*🙌🏿

*Wannan Shafin naki ne Shuwah Darling, ilysm* ❤❤

15 - 20

Tafi mintuna ashiri da shiryawa cikin fitinannan matsatsan english wears riga da wando da sukayi mutukar fiddo da azahirin shape din jikinta, kai komo take a tsakar dakin tanai saka da warwaran neman hanya fecewa. Lek'awa tayi ta k'ofa ta hange Daddy da mom zaune parlour suna hira, susucewa tayi ta koma ta zauna hade da latsar nambar Salim.
Yana tsaye bakin mota yanai jiranta ganin call dinta yasashi azaman dauka.
"Kayan da kika shanya sun bushe" Ya fad'a cike da takaici zaman jiranta da yake.
"Ya salim am sorry kaban tym kadan, narasa yadd zan fito, su Daddy sun babbake apalo"
"Minti biyar nabaki idan baki fitowa zan koma daki na kwanta"
Tsaki tayi ta kashe wayan.
"harshi zai bata minti biyar waye shi" Aranta ta fad'i.
Wardrope ta bude tadau dogon hijab dinta mai hannu ta sanya sannan tadau wipes to goge red lipstick dake shafe bisa sexy lips dinta. Math textbook dinta ta dauka da biro sannan ta fita zuwa palon, kusa da Mom ta zauna tana dubu textbook din sannan ta kalli Daddy fuska shagwabe tace "Daddy nayi misplacing calculator dina gashi kuma ina da assignment dazanyi"
Murmushi Daddy yayi jin diyar shi taci serious da karatu, yace
"ki duba dakina cikin drawer bazaa rasa ba"
Mikewa tayi da azama, cikin sauri tace "yauwa Daddy, nagode, Mom gud nyt" ta karasa

maganar hade da sauri fad'awa dakin Daddy.
Dariya Mom tayi suka cigaba da hirar su.

Kaman munafuka tadau calculator din ta fito, sad'af ta wuce hanyar kitchen ba tare da iyayan sun lura ba, cabinet ta bude ta ajiye textbook da cal din da hijab din jikinta sannan ta bude k'ofar ahankali ta fice waje bayan ta rufe da mukulli.

Salim dake tsaye yana kallon tahowar ta susucewa yayi, gabadaya ta rikitamai tunani wani abu yaji yana tsikaran shi da azalzalan zuciyan shi.
Bai ankara ba yaji ta gabansa yana shakar kamshi dake tashi jikinta.
Harara takai mai tace "wannan kallon fah, kasan dai i hate it, ka kama kanka"
Sose keya yayi baice komai ba ya bude mata motar ta shiga sannan shima yaja.

Officers Club...

Sun iso yayi parking, tura kofar Salma tayi ta jita gam...
Bata rai tayi ta dubeshi
"Miye haka".
Kallon ta yayi, gabadaya idanunsa sun sauya launi, hannu yasa ya fizgo ta jikinsa sannan yace "ki bani chance Salma, ina mutuwar sonki"
Kallonsa tayi cikin ido ba tare da tayi yunkurin dagowa daga jikinsa ba saima murmushi ta sakar mai hade da kai fuskan ta daidai fuskar shi suna jin numfashin junan su, kallon ta yake yanai tunanin kota amsa mar soyayyar ganin yadda ta sakar mai jiki, da kuma bakin junan su dake daf da hadewa, kallon lips din yayi, yana gaf da daura nasa yaji ta bugu uban tsaki hade dakai hannuta bisa lock tayi unlocking motar, janye jikinta tayi ta bude kofar ta fito ta zagaya bangaran sa ta window tace "kasan dai halin Daddy, karma ka fara" wuce wa tayi ba tare data jira cewar saba.
Numfashi ya sauke mai dauke da tari wahala da shaawa data motsomai, kallon joystick dinsa yayi ya ganta tsaye k'ekam, saidai ba yadda ya iya mafitar sa daya yasa hannu karkashin sit yadau kwalba mai dauke da barasa (giya) ya fara tuttulawa bakinsa.

Cikin takun isa da takama ta shiga gurin mai dauke da disco light, hadaddan gurine na watayawa, kowa da abinda ya shafe shi, ba ruwan wani da wani, wasu mazan na gefe suna rawa da yammata wasu kuma zaune suke gurin wine bar, wasu kuma makale da yammata su suna shan minti, wasu kuwa chess game sukeyi.
Fara taku tayi gurin Wine bar taji wani a bayanta,
"Yammata..
Juyawa tayi
Yace "kin hadu fah, da irinku yadace aje Dubai hutawa.
Yak'e tayi hade da fari da Ido, aranta tace da uwarka zakaje Dubai hutawa badai dani ba, shege mai kan kwakwa.
Afili tace
"Dagaske" cikin nuna farin ciki, wayarsa ce tayi ringing yadauka hade da jan hannuta suka

karasa gurin hade da zama kan long backless chairs dake gurin...

Daga can Gefe yake zaune, yana kallon abunda ke gudana agurin, agogon hannusa ya duba yaga goma ta cika, guntun tsaki yaja hade da gyara zama, ya dubi bartender dake guri..
"Bani sigari guda daya".
"Yes sir" bar tender ya fadi hade da mai lightening sannan ya mika mar.
"Sir do you need wine or beer ?
Kallon banxa da Mujahid ya wulla mai yasashi tsuke baki.

Cikin kwarewa ya fara zugarta juyawan da zaiyi ya hangota tanai kokari saka hannu cikin aljihun wanda suke zaune tare, ware ido yayi yana tuna abunda fa'iza tace mai akan yarinyar barauniya ce.
Shikam ya shagala da waya, Salma ta ciro wallet dinsa dake ajiye, budewa tayi taciro dari biyar biu dake wallet din.

Mugun tsananta Mujahid yaji hade da saurin dauke kai gareta.
Tsaki taja tana fadin "matsiyaci ko kudin kirki baya shi" maida kudin tayi cikin wallet din sanan ta maida mai abarsa ta mike tsaye, saurin riko hannuta yayi yanai mata nuni da karta tafi, harara takaima sannan ta fizge hannun tayi gaba.

Cike tsananin bacin rai Mujahid ya gama yiwa sigarin zukan Allah tsine uwar hegu, sannan ya mika hannu gurin bartender yana fadin karomin daya"
Mikomai bartender yayi, hannusa yasa zai amsa yaji hannu wata bisa nashi tanai shirin amsan sigarin saidai kafin yakai ga amsa ta rigashi amshewa.
Saurin Duban ta yayi dan ganin wace yar iskan ce da karfin halin shiga tsabgarsa.
"Kallamu ka gama kallo..." Ta fada cikin salo rainin wayo, kallon ta yayi saidai mamakin ganin tasa sigarin abakinta yasa shi sank'amewa gurin...
Dariya tayi ta cire sigari daga bakin ta
tace "i never knew the decent and useful policemen smoke, much less a indoors inda babu wanda zai gansu"
Shikam ya gama kulewa da ita, tashi yayi ya canza guri dan bazai iya tanka taba yadda yake mugun jin tsananta da haushinta.
Matsawa tayi inda ya canxa tanai kuma darawa, tace "karka damu your secret is save with me, am sure irinku ke claming goods guys a gida"
Tsaki yaja aranshi yace "shameless bitch"
Karaf a kunnan ta baisan ma ya fada fili ba.
Ranta yadan sosu, sai yanxu ta gane kallon dayake mata, murmushin dole tayi tabar gurin. Fita tayi ta wurgar da sigarin sannan tahau goge bakinta, abunda bata tama yiba asalima taimakon shi tajeyi, saidai inya san wata bai san wata ba, hannuta dake dunkele ta bude kallon agogonsa data zare ba tare da sanin saba, murmushi tayi ta cusa a bra dinta sannan tahau nema Salim su koma gida. Can lungu daga baya taganshi da azama ta karasa gareshi ganin baya cikin hayyacin shi banda barasa dayake ta kokarin sha, idon ji jajir.
"Na shiga uku, yaya miye haka" ta fada cikin tsoro, rikoshi tayi da niyya dagoshi suka fadi kasa

tare ayayinda yake ta suburbuda surututai game da yadda yake sonta.
Tsaki taja, duk ya shafa mata giya ajiki, barin gurin tayi neman temako.

Mikewa tsaye yayi ya kai ido kan hannusa dan duba tym saidai wayam yagani ba agogo, k'asan gurin yahau dubawa saidai wayan, mamaki yayi dan daxu ma ya duba agogon,
"Kodai.. Ya fadi aransa, ba tantama itace amma how cms, can ya tuna daxu hannusa da nata sun hade.
"Yarinyan nan wasa take dani" ya fada, fitowa yayi waje, kicibis sukayi xata shiga yayi saurin finciko ta hade da manne ta jikin bango, hannusa daya shake bisa wuyanta.
Zare ido tayi tanai kallon yadda ya koma mata kamar zagi, murya sheke tace "sake min wuya...
Kara shaketa yayi, ya matse ta tsam har suna shakan numfashin juna, cikin zare ido "dan ubanki, idan kina karuwancin ki, sata da rashin kunyar ki, ki tsayar can gurin k'ananan k'wari da kika saba yi suna kyale ki, dont you dare ki kusanto gareni, am not one of those useless men da kike toying around dasu, Understand?
Harara takai mai ta kuma cewa "kasakeni ?
Sakinta yayi, yana kara kallon shegen kayan jikinta, sannan yace "ina agogona ?
"Ka bani ajiye ne"
Kara daure fuska yayi
"Tunda kinyi shaye shayan da kika saba ai dole kice haka" kara matseta
Yayi, jikinsu na gogan juna ya kuma tambayanta.
Wani irin yanayi taji da tunda taxo duniya bata taba jinsa ba, d'an matsar da jikinta daga nashi tayi ya kara matseta, daurewa tayi ta kallesa cikin dakewa gudin karya gano komai tace "bansani ba" hade da daure fuska, jikinta yahau dubawa baiga komai ba, can idanuwasa sukayi caraf akan boobs dinta, kallon su yahau yi, xaikai hannu tayi sauri sa hannunta ta tokare shi, bige hannu yayi yanai mata mugun kallo yace "Worthless prostitute kin dauka dason raina jikina ke goguwa da naki, banxa marar tabiyya" bai jira cewarta ba ya tumbula hannu cikin yar top din jikinta yafara laluban agogon shi, sai gashi ya dauko.
"Banxa barauniya" ya fada hade da tureta gefe.
Ranta ya gama bacci, saidai bazata bari yaci galaba akan taba, dariya tayi tace "ai ban cika barauniya ba tunda baka da guts din arresting dina, dan iska kawai"
Murmushin da shika d'ai yasan manufarshi yayi yace,
"We will see about that, useless girl, bani da lokacin ki" tafiyarsa yayi yabarta nan tsaye.

"Salma karki ma banxan nan kuka, you're strong" ta fada aranta, jiki sabule ta juya ciki takira maza biyu sukasa Salim a mota taja su sukayi gida zuciyar ta dauke da tunani iri irin. Tana isa gida dakyar tasamu ta rike Salim zuwa part dinsa danta lura sam baya cikin hankalinshi sannan tabi ta kitchen ta shiga part dinsu cikin sand'a ta gudun cikin dakinta.

Hankali kwace yasa mukulli ya bude palon gidan ya shiga, jin shuru yasa shi sauke ajiyar zuciya tare da kokarin haurawa sama.
"Mujahid.... "
Yaji kiran sunan sa tamkar saukar aradu, gabansa ne ya fadi ya juyo, Hajiya yagani sanye fuska babu annuri.

"Daga ina kake, wato ni mahaifiyar kake wasan buya da ita, ko kuwa dai ni saar kace ??
Cikin fusata ta jeromai tambayan tare da karasa wa gabansa suna facing juna.
D'aure fuska yayi yace "aiyuka sukamin yawa"
"Aiyukan banxa da haryau ka kasayin simple aiki dana saka"..
Kallan mamaki yay mata, "wai simple aiki, nemo mutum daya bata for 7 years ne simple, kuma ma just 3 month back aka san she is missing"
Afili yace "hajiya sorry to say, ya kamata ki manta da so called yarinyan nan, cox nayi iya kokarina ban ganta ba.."
Wani mugun mari Hajiya ta watsa mai kafin ya ida magana, cikin huci tace "diyar kanwar tawace so called, Mujahid ni kake gayawa maganan nan, yarinya da uwarta taci kashinka da fitsari kake kira da so called, atleast idan baka nemo ta dan niba ko adan yadda uwarta ta raineka ai ka nemo ta"
Idon shi sosai ya canxa launi, yace "shikenan Hajiya zan ajiye aikin, sai anemi wanda xai nemota amma bani ba, tunda duk kokarin da nake baa gani, narasa miyasa bakya kaunata acikin gidan nan, kowa zaiyi abunda yake so amma banda ni kuma tunba yauba kike treating dina haka" kaman xaiyi kuka yayi maganar, wuce warsa yayi ba tare daya jira cewar taba.
Jikin hajiya sosai yayi sanyi, tasan Majahid da taurin kai, tunda ya furta bazai nemo taba toh kuwa bazai ba, tsoro ne ya kamata kar ya ajiye aikin.
Zancen Abban su Mujahid ta tuna.
"Salamatu ki rage daukan zafi akan Mujahid, shi yaro idan yayi laifi baa mai duka ko zagi dan kuwa zai iya zama tsegararre, hakan da kikeyi yasa yazama mai mugun taurin kai acikin yan'uwan sa" abunda mijinta ke yawan fada mata kenan aduk randa Mujahid yayi mata laifi, Ajiyar zuciya ta sauke tana kara tuno wasu abubuwan da Abban yaranta ya fadi mata kafin rasuwar sa.

Cikin kunci ya karasa dakinsa, ya jima yana saka da warwaran neman mafita dan kuwa bazai yadda kudurin Hajiya ya tabbata akan shi na auramai ummi ba, ga kuma wata can Salma tanai daura mai zafi, tunowa yayi sanda ya matseta jikin sa dawani yanayi daya shiga, saidai abun daya lura ita ko ajikinta da alamun shi kadai ya shiga yanayin, tsaki yaja yace "ta saba da maza no wonder she wont feel anything...
Dogon Ajiyar Zuciya ya sauke, aranshi sunan Ummi Salma ke yawo a kwakwalwan kanshi.

***
Bayan kwana biu...
Mujahid bai kuma fita office ba, kullum yana makale a daki, ko kiran shi akai a office saidai ya dauka yace baya da lapia, hankali Hajiya yayi matuka tashi sosai, saida taje dakanta ta lallabashi bayan tace mai ta hakura da neman Ummi harsai randa Allah ya bayyanata sannan ya saki ranshi.
Ta bangaran Salim ma kusan hakane, mugun Haushi salma yakeji saidai sonta na nan daram aranshi.

Kasancewar yau suke da lectures masu yawa, tun 10 Salma ta shiga skull. Karfe hudu bayan an fito sallah, sukaje faculty ita da abokanta Shehu da Habib submitting wani assignment da aka basu kwanaki baya kowa yayi submitting banda ita.
Zama sukayi kan dakali suna hira da musun Ball, dan kuwa Salma akwai son Ball, Suna cikin yi Malama Faiza taxo da motar ta kirar Civic tayi parking gurin ta fito rike da takardu hannuta, dawowar ta kenan daga lecture data dauki yan level 2.
Dariya Salma tayi ta kalli Habibu tace ka kalli wani film the sugar Mummy.
Shikam Habib ya dauka da gaske take, yace "miya faru, halan film din ya hadu...
"Ina fa ya hadu, wata tsohuwar matace ta auri Yaro koma ince sa'an ta, kaga couple din, ko dacewa basuyi ba, i dunno y old hags dinnan basa respecting kansu su nemi daidai dasu".
Dariya Habib da shehu suka kwashe dashi, tsaf Faiza ta gane da ita Salma take, dakewa tayi ta tsaya duban takardun hannunta duk dan taji karshe cin fuska da Salma ke mata.
Habib yace "indai akwai love ai shikenan"
Tsaki salma taja, "love my foot, kaga kamin submitting din nizan shiga Auditorium nasha Ac, kasan ban saba da zafi ba"
Shehu yace "Salma akwai fa Math 101 yanxu, kodayake Mutumin bai shigowa da wuri"
Yatsine fuska tayi tace "nikam sai 5.30 xan shigo hall, nasan Shirgegen gardin nan ba zuwa xai ba" juyawa tayi ta kara gaba.
Sai sannan su habib suka lura da Faiza dake kallon su, cikin rawar jiki suka gaidata hade barin gurin.
Ran Faiza ya gama baci, tana shiga office dinta tahau tunanin yadda zataci uban Salma.
Salam dai akwai kwakwala balle tabata F a course dinta, tunanin take can dabara ta fado mata, timetable tadau ta duban sunan wanda ke masu Math 102, Malam Dauda ne kuma suna gaisawa, mikewa tayi ta iske shi office zaune baya da shirin fita lectures, rokosan tayi akan ya bata aran space din, ba masu yabata dan kuwa bashi da niyya zuwa.
Office ta koma da azama tadau Test Question papers daya kamata ta masu test next week ta fita dashi.
Securities shida ta kira suka rakata Hall din, dalibai kam tsorata sukai ganin test zaai tuni wasu suka tsure, shehu kam kokarin kiran Salma yahau bata dauka ba, gashi kuma itace mai kokarin, nata suke kwashe idan zaai test.

Da sauri Faiza tahau raba papers sannan kowa ya fara, hankalinta kwance Salma bata hall din.
Sai 5.30 Salma ta fito daga Auditorium, miss call din shehu tagani, bata damu ba ta karasa gaban hall, jin shuru gabanta ya fadi, tana shiga taga kowa yayi wiri wiri da ido, kafin ta ankara taji Faiza tace "Hey Get out"
Tsaye Salma tayi, tsoro yakamata ana test, Daddy kadai take tunawa zaici ubanta idan yaji labarin batai test ba.
"Kumin waje da ita" Faiza ta fadi ma securities din.
Dakewa Salma tayi hade da watsa mata harara sanan ta fita bakin Hall ta tsaya kaman xatayi kuka.
"Zakisan dawa kike" Faiza ta fadi a aranta hade da dailling numban Mjay, yana gida zaune gaban laptop yana dannawa saidai mintuna kadan yakan tuna haduwarsa da Salma.
Daukan wayan yayi, ta fito waje gaban Salma cikoin yauki da kwarkwasa tace

"Mjay ya jikin ka
"Am alright, ya skull ko kin dawo gida ?
"Ina skull dai, hope dai kasha magani... Ta fadi murya a shagwabe
Salma kam kallonta take aranta tana fadi "zaki gane kuran kine"
"Faiza miya faru .. Mujahid ya tambayeta cikin rashin fahimtar yadda cikin sakon daya ta canza salon maganarta a shagwab'e.
"Ba komai" tace
Katse wayan yayi, kunya ta kamata,
Mugun kallo tama salma sannan tace "okay, i love you tooo, bye" cike rangwada ta koma ajin.
Salma kaman ta hadiyi yawu ta mutu, tunowa tayi da worthless prostitute da Mujahid ya kirata dashi, shine ba kunya yake cewa tsohuwar nan i love you.
Haushi ne ya kuma kamata, afusace tabar gurin ta shiga motar ta taja.. Gurin wasu kawayanta area boys ta nufa, sun jima suna magana daga bisani tabar wajan zuxiyar ta fari tas.
[9/7, 12:37 AM] Xarah Bukar: *Zuma Sai Da Wuta*

~na~
©χaraђ bųkar

21__23

Ana gama Test Faiza ta tattare script din gurin daya, zuciyarta fayau dauke da farin ciki, mota ta shiga ta ajiye su gefe sanna taja, ganin hadarin dake garin kuma magrib ta kusanto ya sanyata wucewa gida ba tare data koma office ba.

Wani Mugun Dariya Salma ta face dashi ayayinta take kokari kunna motar ta dake parke gefen titi, kunnawa tayi taja ta at 360 tanai bin motar Faiza abaya, can kuma tafara slowing down kafin daga bisani ta tsaya da motar tana dariya.

Parking Faiza tayi ta fito tanai kallon samari hudu rike da Adda dasuma kallon ta suke fuske babu annuri, da ganin su yan tasha ne.
"Lafiya ?
Ta fada cikin karfin hali nuna rashin tsoho.
Basu tanka taba saima dayan su dayace bude motar duk abunda kuka gani ku kwasa, kaman jira suke suka bude kofar test script din suka dauka hade da handbag dinta dake ciki, budewa sukai babu komai sai gayyar pen da kayan shafa.
Hankalinta ne yatashi tace "dan Allah kuyi hakuri, banda ko sisi takardun nan kuma ba nawa bane".
Dariya sukayi.
"ba matsala, wanan takardar ai kudi ci, muna bawa mai kosai zata siyosu naira hamsi"
Kaman tayi kuka take kallon su, test din da taci buri shine zasu saida hamsin, bata gama

tsorata ba taga sun soka kusa a tire motar ta, dariya sosai suka kwashe dashi sannan suka hau mashi dinsu suka bar gurin.

Salma kam baki har kunne dan dariya, kallon Faiza take yadda gaba daya ta susuce, next plan dinta tayi shirin yi, tayar da motan zatayi ta lura faiza na waya bayan ta gaba kuma ta shiga motar ta zauna hade da tagumi.
"Bari muka wa take jira" Salma ta fada, gyara zama tayi hade da saka earpiece akunne saurara waka.
Mujahid ta kira awayan, baafi 20 minit ba ya karaso gurin, fitowa yayi ya doshi motar ta, tana ganin shi ta fashe da kuka hade da fitowa daga motan.
"Hoo dama shi takira" acewar Salam daga inda take masu eye service, wani irin haushi ne ya mamayeta, kunne motar tayi ta kara gaba daidai inda Mujahid yayi parking sannan ta fito hade da daure fuska.
Faiza kam kokari fadimai abunda ya faru take sukaga Salma gaban su.
"Malama lafiya kike kuka da girman ki"
Dakatar da kukan Faiza tayi ta nunata da yatsa,
"I knew it, kece kikai planing duk abunda ya faru"
Kallon rashin fahimta Salma tayi.
"mai kuma nayi, miya faru ?
Tambaya ta kike, Faiza ta fada hannu dakai hannu zata kwashe ta da mari, Sauri rike hannunta gam tayi, tace "karki kuskara hannuki ya tabani, kuma ki daina accusing dina da abunda ban yiba"
Fize hannuta faiza tayi ta juya yima Mujahid bayanin abunda ya faru tun a makaranta, shikam mujahid bai gane komai ba banda area boys da Salma ta turo, mamaki sosai yake banda bakin halin Salma ashe har yan daba ma harka take dasu.
Suna cikin haka aka fara ruwa, lallaba faiza yayi bayan ya ciro mukulin motarsa ya bata ta yace taje gida zai biyo mata da nata, bataso hakan ba, ba yadda ta iya ta shiga motar cikin rawar darin ruwan daya bugeta, Salma kam tun lokacin da Mujahid ya ciro mukullin motansa ID card dinsa ya fadi ba tare daya lura ba, hannu Salma tasa ta dauka sannan ta arce cikin motar ta, ko kara kallon su batai ba taja motarta tayi gaba.
Mechanic ya kira ya gyara motan sannan ya shiga yaja xuwa gidan su faiza maida motar, nan ya iske zazzabi mai karfin gaske ya diran mata, saida ya siyo mata magani tasha sannan ya dauki tasa motar, Umma sai godiya take tanai shimai albarka.

*****

Washe gari da Mujahid yayi shirin fita aiki, ba inda bai bincika neman Id dinsa ba, atunanin sa a office ya bari, yana zuwa bai gani ba, zama yayi ya fara aikin gabansa.
Karfe sha d'aya na safe Salma ta tashi daga baccin data koma tun bayan da sukayi karin kumallon, wanka tayi tasa blue jean da white long sleve shirt sanna ta zauna latsar wayarta, bata da niyyah fita kasancewar basu da lec aranar, ID din Mujahid ne ya fadowa mata arai, da azama ta mike tadau jarkarta ta zazzage abunda ke ciki tasa hannu tadau ID din, murmushi tayi ta zauna karanta abubuwa dake rubuce akai,, nambar wayarsa dake jiki ta cofe a wayarta

sannan tayi Dailing.
Shikam ya dukufa sosai da aiki gabansa, yana jin ruri wayarsa ya danna hade da sata a speaker yaci gaba da aikinsa,
Dariya tayi tace
"Mujahid Abdulsalam Right ?
Wani iri yaji yadda ta ambaci full name nasa, bai d'ago murya ba saidai zaiso sanin wace ishashiya ce.
"Who are you ? Ya tambayeta.
Tace
"don't worry yanzu zaka ganni, ina da Address din wia you work"
Tsaki yaja had'e da kashe wayan sa, atunanin sa Yahoo girls ne dakeson cin kudinsa, cigaba yayi da aiki gabansa.
Dariya Salma tayi tanai kallon inda marital status dinsa ya nuna single, tabe baki tayi tace ashe ma faizar ba matar sa bace take ta rawan kai akanshi"
Mikewa tayi ta zura Bakar abaya tayi rolling kanta da veil sannan tayi light makeup ta fito, dakin Mom ta nufa ta mata karya zuwa skull sanan ta fito da sauri ta fada motar ta.
Aikinsa kawai yake yama mance da kiranta, yaga ta turo mai text
"Kazo ka shigar dani kafin securities dinnan su gama tattab'ani"
Dariya ma ta bashi, bari dai yaga ikon Allah, wani police ya kira yace yaje ya shigo da ita.

Baa jima ba ta shigo Cikin takun kwas kwas, dagowa yayi ya dubeta cike da mamaki, aranshi yace "alamu yarinyar nan bata da niyyan barin rayuwata, i have to act fast"
Murmushi ya sakar mata yace "ashe kece"
Yap" ta fada, cire abaya tayi ta ajiye gefe sannan ta zauna kujerar dake fuskan tar shi.
Jinjina Too much of confidence dinta yayi aranshi
Tace "hop am save wannan murimshin naka bangane ba"
B'ata rai yayi
"Miya kawo ki office dina..
Karewa hadadan office din kallo tayi sannan ta dube shi tace "i was expecting naga crying baby mama dinka anan"
Mugun kallon yayi yama yace "saboda ke she has fallen sick, what were you tinking da zaki tura mata yan daba"
Tabe baki tayi.
"Am sure kukan banza da tayi yasata zazzabi, koni karama banga abunda zai sani kuka ba, infact banga wanda ya isa na zubdamai precious Hawaye na ba"
Shikam kallon ta yake yana mamaki over confidence dinta, yace "iskanci da kike a titi bai ishe kiba sai kin zomin office tsabar jaraba irin taki"
Murmushin daya fi kuka ciwo tayi sannan ta mike tsaye, idanuwansa akanta tabi gefe table din ta dawo gabansa ta zauna kan table din shikuma a kujera suna fuskan ta juna.
Murya kasa kasa tace "iskancin bai isheni ba, ka taba ganin worthless prositute na iskanci dan kudi ko aji, kaga am all yours kayi abunda kaga dama dani"
Unfasten din  shirt dinta tafara, Yarage white vest dake jikinta.
Bai hana taba saima zubawa jikinta ido da yayi

"Hey, look at mee" tace hannu tasa ta tallafo fuskansa, ganin hankalin sa gabadaya baya tattare da ita, yasata duban direction da idanuwa sa suke, wani birthmark mai shape din triangle dake saman boobs dinta yake kalla..
Lumshe ido yayi, yace
"Miye wanan ?
"I dunno nima haka nagani"
Tashi yayi fusace, adan tsorace ta kalli sa, yace tashi ki fice min a office"
Harara shi tayi tace "baka min abunda nakeso ba"
Finciko hannuta yayi da karfin gaske ta fada jikinsa, kansu yana garuwa da juna, nace ki fice min kafin nasaki kuka yanxu nan.."
Magana xatayi aka turo kofar aka shigo, Salim ne ya shigo rike da wasu takardu hannusa, ransa ne ya baci ya tsaya kallon su, daure fuska Mujahid yayi yana huci, Salma kam dariya tayi ta ajiye mai Id dinsa tadau jallabiyar ta tayi waje batare data dubi salim ba.
Mugun kallo Mujahid yamai yace "baka iya knocking kofa ba ?
Daure wa yayi yace "sorry sir, banyi tunanin kana da company ba" ajiye Files din yayi ya fice zuciyarsa na zafi.
Dukan table din Mujahid yayi cike da takaici yadda ta zubar mai da mutunci, "dan iskan yaron nan raina ni xaiyi, ya dauka son budurwarsa nake" azuci yayi magana.

Salma na kokarin kunna mota Salim ya bude ta afusace, fuska ba walwala yace "miya kawo ki nan, make tsakanin ki da dan iskan nan ?
Tsaki taja, "ina ruwan ka" cigaba da kokarin kunna motar tayi, haushi yasashi finciko ta waje.
"Salma sonshi kike kenan Cikin masifa tace "Allah ya sauwake naso shi, dan Allah ka kyaleni karka batamin rai.
"Toh miye kukeyi dana ganku, are you trying to seduce him or what?
Tsaki taja ta harara shi hade da fincike hannuta, "i don't own you any explanation duk abunda kake tunani hakane" shiga tayi zata rufo kofar ya kuma riketa, Salma am sorry, kawai bansan ganinku tare, dat man is full of himself koda kin soshi zaki wahala ne, plz stay away from him"
Tausayin sa taji batace komai ba, sakin murfin kofar yayi, taja motar jikin ta sanyaye, harga Allah bason Mujahid take ba aslima kure shi tasoyi yadda yake dauka kanshi wani abu da Insulting
mutane yadda yadda yaga dama.
Sai yanxu ma taji haushin abunda tayi, saidai bazata kuma shiga tsabgar saba.
[9/7, 12:37 AM] Xarah Bukar: Zuma Sai da Wuta✍

~na~

©ӽaraђ bųkaɾ
®NWA

24___26

Tun ranar Salma da Mujahid basu kara crossing path ba, haka yamai dadi matik'a saboda shigan mai rayuwa da take ba karamin treat bane agareshi. Ta b'anganan Salma ma kusan hakan ne tuni ta bawa banza ajiyar sa, harkokin gabanta da zuwa skull tasa agaba, tsakanin ta da Faiza kowa tasa ta fisheshi bamai shiga tsabgan wani, duk da faiza na rik'e da ita a zuciyan akan cin kashi datai mata saidai kama girmanta shi yafiye mata.

Yau sunday, bayan sunyi karin safe Salma ke jib'e a palo tana kallon ball, ko wanka batai ba jikinta sanye da nyt wear riga da wando, Mom ce ta fito palo cikin shigar alfarma tahau ta da fadan hanata zama da kayan bacci balle yau data kasance weekend lokacin ziyarar Baki, shagwabe fuska salma tayi kaman xatayi kuka ta mike ta shiga dakinta, Hoton sa dake kan console ta fara tozali dashi, muguwar harara ta tafka wa hoton had'e da jan doguwar tsaki ta shiga toilet freshen up. (Ni xarah nace baima san kina yi ba).

*****
Cikin kananun kaya yayi shirin sa tsaf daya matukar fiddo azahirin kyaun kyakyawan sifanshi, zuciyar sa fes ya tsuri mukullin motar sa ya sauko kasa, Junaina kadai ya iske zaune palo tana kallon Jennifer dairy, baibi takan taba ya zauna yana fadin "Ummi dauko min ruwa na sha". Kaman jira take ya mata magana ta mike tsulum tana mai duban mamaki..
"Yaya Yaushe kuma na zama Adda Ummi ?
Gabansa ne ya fadi, baima san Ummi ya ambata ba, kallon ta yayi gabadaya ta rikede mai kaman Salma saurin maido da hankalin sa waje daya yayi, yace...
"Ummi kuma, wace ce haka ?
Kaman zatayi kuka tace "yayata mana".
Tsaki ya yaja ya mike hade da rab'awa gefenta ya wuce kitchen, Junaina kam ba wuya kukan, share hawaye daya zubo tahauyi sannan ta arce da gudu dakin Hajiya.
Hajiya da Jafar ke zaune kan gado, wanda tuni ya dawo daga tafiyar da yayi, Hirarsu sukeyi cikin nishadi, shi dama jafar ma'abocin raha ne, indai yana Gida toh Hajiya bata da kewa..
Fashewa tayi da kuka ta karasa ciki hade da fadawa kan cinyar Hajiyar, hankali tashi tahau tambayan ta ba'isin, Jaafar kam dauke kai yayi ya koma duban wayansa sanin kukan ta baida nasaba da yayanshi..
Cikin muryan kuka tace "Hajiya sai yaushe zanga Ummi ? Yaushe zata dawo zama damu ?.
Cikin bazata tambayar tazoma Hajiya, murmushin dole ta kirkiro tace "junaina banason kukan banza, indai Ummi ce very soon zaki ganta, Abbanku dakanshi yace xai kawota...
Mik'ewa Jaafar yayi ya fice daga dakin, zuciyar sa namai zafin, baya kaunar ganin kukan junaina koda wasa.
Bata rai Junaina tayi jin an ambaci Abbanta tace "hajiya banason Abba ba ruwana shi dani, tunda nadawo hannuki baizo gurina ba, ni banma sanshi ba, yayata kawai nakeson gani dukda itama ban santa ba bata sani ba, amma zanji dadin kasancewa da ita"
Murmushi Hajiya tayi tahau shafa bayanta tana cewa "very soon zaki ganta, kinji autar hajiya"
Kad'a kai Junaina tayi batace komai ba banda sauke ajiyar zuciya da take.

Fitowan Jafar palon sukayi kicibis da Mujahid rike da bottle water yanai shirin fita waje "Hankalinka ya kwanta ka sata kuka ko ? Jaafar ya fada yanai kallon shi, fuska babu walwala.

Kallon am not your mate Mujahid yamai sannan yace "miye amfanin ka, kaje ka lallabata tunda sonta kake..
Yak'e Jaafar yayi.
"Ai ita kai takeso, bai kamata kuma kana hurting feelings dinta ba, ko baka sonta she deserve some respect"
Mugun kallo Mujahid yamai yace "fada kazo min kenan"
Ba fada bane am just saying the fact, ya ake ciki da neman Ummi.. ?"
Dariyan rainin wayo Mujahid yayi sanna ya tamke fuska
"Am done searching for bitches" bai jira abunda Jaafar xai ce ba ya ficewar sa waje.
Jaafar kam mamaki ne yakama shi, girgiza kai yayi ya zauna hade da tunanin yadda xai fara nemo Ummi kodan sanya Hajiyarsu farin ciki.

****

Cikin light purple arabian gown Salma tayi shirin ta, sauri kadai take ta fita Qrandsquare shopping data sabayi duk bayan sati biyu, agurgurce taje gurin Mom tai mata sallama ta fice waje, nan haraban gida ta iske Salim na waya, ganinta yasa shi katse wayan tamai kyau sosai.
"Salma sai ina, irin kyau haka ? Washe baki yayi.
Yatsine fuska tayi ayayinda take kokarin bude motar, tace "yau Sunday kaima kasan inda xani ?
Riko hannuta yayi "ki tsaya na kaiki
Kallon karfin hali barawo da sallama tamai tace "kabari next tym sai muje" janye hannu ta tayi yayi sauri kara rikota. "Salma nafara gajiya da wulakancin ki, kin dauki ni kamar wani puppy dinki, you keep using me when ever you want people to detest you amma damun keb'e saiki fara yank'wanani kuma am sure kina kaiwa wasu maza kanki cox d first tym dana gankii arayuwata nasan you aint a good person"
Dariyan rainin wayo tayi.
"Ya salim you're funny, ka fiya zalama shiyasa bazan iya baka kaina ba"
Ranshi ya baci matseta yayi gam jikinsa yanai mata mugun kallo itakam banda dariya ba abunda take, shigowar Motar Daddy ne yasa shi sauri sankin ta, amma tuni Daddy ya gansu, da gudu Salma ta karasa gurinsa tamai sannu da zuwa kasancewar yayi bulaguro, sosai yaji dadin ganinta sun dan gaisa tamai bye to koma mota taja tabar gurin.

Sai sannan Salim ya gaida Daddy, Mugun kallo yamai, cikin fada yafara cewa "ban hanaka zuwa inda Salma take,
Shuru salim yayi ran shi na zafi, Daddy ya cigaba "kaga yadda na taimaka na dauko ka harka zama wani abu, i wont hesitate throwing you out of this house if you dare hurt my Precious Daughter, kar kaga duk abunda take bana tankawa ina sane da komai, i trust her kuma nasan bazata bani kunya ba, so you'd better keep your distance".
Kai Salim ya sunkuyar, yagane inda zancen Daddy ya dosa, kar shaye shayan shin yayi effecting Salma, saidai ayadda yakejin son Salma bazai iya barin taba, Wucewar sa Daddy yayi bai jira abunda xai ceba.

***

Hankali kwance Mujahid yake tukin sa, gidan su Faiza zai je wanda ya zame mai jiki duk weekend, saidai baya zuwa hannu empty yakan dan siya mata kayan dadi, yanke shawaran tsayawa Grand square yayi dan siya mata kwamulashe.

Salma na isa Grandsquare parking tayi ta karasa ciki, tsayawa tayi a tsakiyar gurin tanai duban wana direction yaka mata ta fara bi, dan ko wana abu da maajiyar sa.

Gurin kayan kwalliya tayi tunanin bi kafin taje bangaran su Chocolate, hankali kwance tafara takunta mai daukan hankali, daidai kwanar dazai shiga siyan fruit ya hango ta tafe, saurin boyewa yayi gudun karta ganshi har ta iyo ta gabansa ta wuce, gurin kayan kwalliya ta tsaya ta loda iya son ranta sannan ta karasa gurin chocolate ta diba, duk akan idonsa, tafiya tacigaba dayi taji ta gware da mutum Handbag dinta ya subuce kasa kayan ciki kaman su pen da powder suka zubo, cikin sauri ya kwashe ya maida mata cikin jakar yayi gaba.

Bata gane waye ba saidai taji haushi yadda bai tsaya bata hakuri ba alhalin shi ya shigo gabanta, tsaki taja ta karasa counter tayi payment sannan taba security ledar kayan dan rike mata, fitowa taxoyi wani alarm dake kofar tayi kara, Security dake gurin yace Hajiya akwai wani abu ajakanne, harara takai mai

"do i look like a terrorist"

"Ba haka bane hajiya, ina kayan da kike siya"

Da hannu ta nuna security dake tsaye kofar da ake fita da kaya.

Alarm dai sai kara yake gashi kuma baa bari ta fita ba, gabanta ne yafadi ta tabbatar akwai wata kullalliya.

Wata mace ce ta karaso gurin, da alamun itace babban security agurin, warce jakan tayi tana fadin "Madam wetin dey inside d bag.."

Shuru salma tayi dan bata fahimci komai ba,

Zazzazge jakar Matar tayi saiga Gold Ring mai dauke da Tag din kudinsa 50k ya fado.

Ware ido Salma tayi adan tsorace tana tunanin yaushe ma tabi hanya juweries.

Mugun Kallo matar tayi mata sannan ta damko hannunta.

"Thieve, ole, dama sata ke kawo irin ku, toh i don catch you..

Iya tsurewa Salma takai, idan akwai abunda ta tsana bai wuce amata shairi ba, balle Sata da tunga uwarta ta haiheta bata taba iya, wata zuciyar tace kin manta kin sace hoto da agogo da Id, Saurin kawai da Thought din tayi tana fadi aranta "wannan ba sata bane, neman magana ne kuma aina maida komai, hoton ya rage shi kuma nawane" (who dash you)

"Ole muje office" taji muryar matan, kokarin janta take kaman akuya.

Marairace fuska Salma tayi tace "Madam dan Allah kiyi Hakuri, bazan sake ba"karasa maganar tayi kaman xatayi kuka.

Security dake gurinne suka bawa Madam din hakuri sannan ta kyaleta bayan ta gama mata wankin babban bargo, Salma kam tagama kulewa ko takan kayanta bata biba ta rugu waje ta fada cikin motar ta.

"Kawo nakai mata" Mujahid ya yace da Security dake baza ido yana neman hanyar da Salma tabi, ba masu ya bashi.

Dariya Mujahid yayi ya nufi inda ya hangi motar ta, aranshi yanai jin dadi yau dolene yaga hawayan da take ikirarin bawanda ya isa yasata zubda shi.

Kan Sitiyari Salma ta daura kanta, kuka takesonyi saida bazata yiba saboda wasu dalilai, sosai Idonta yayi jajir tahau tunanin yadda ring ya shigo jakarta, "kodai wanda ya fadarmin da jaka ne ya...." Knocking din window ne ya katse mata tunani, dagowa tayi sukayi four Eyes yana sakar mata wicked smile, kofar ya bude ya daura mata kayan acinyarta sanan yace "long time no seen"
Kallon shi tayi ta tuna da wanda ya bigita,, aranta tace wato shine yaja mata cin fuska.
Shuru tayi, bazata iya magana ba karya gano yadda ranta ke bace, dan kuwa kiris ya rage tayi kuka.
Hannu motar taja ta rufe ta kunna tayi gaba, sosai Mujahid yaji dadi, koba komai ya ajiyeta in her place, next tym she will learn to respect herself, saidai rashin kukan ta yabashi haushi.
Dariya yayi ya koma motar sa yaja gidan su Faiza, taji dadin ganinsa, sun jima suna hira kafin nan ya gangaro mata wata tambaya.
"Faiza ya student dinki, hop dai yanxu bata miki raini...
"Wa kenan" Faiza ta tambaya, dukda tasan wace yake nufi.
Yace "ko Ummi koya take da suna, yarinyar nan mai harka da area boys"
Tsaki tayi tace "Salma xakace, sam bana kaunar yarinyar nan... "Karashe maganar tayi tanai duban fuskan shi, saidai bata gano komai ba.
Shuru yayi tace "Mjay don't tell me you're fond of that girl ?
Dariya yayi ya share zance yace "ya bazawarai, nifa ke nake jira kiyi aure sai nayi, kinsan friends dont abandon friends.
Harara takai mai cikin salon wasa, azuciyar ta taji haushi abunda yace.
Tace "kamin adduaa Allah ya kawo na gari"
"Okay tam".
Wata hira suka kama sun jima tare daga bisani ya koma gida.

****

Washe gari..
8am Salma ke da Lecture, 7.30 ta fito fuska ba annuri, zuciyan ta na radadin abunda ya faru jiya, Daddy da Momy ta iske zaune a dining, Daddy nasha tea, ciki ciki ta gaida su, daga ganin fuskar ta bata cikin walwala.
Daddy yace "Salma make damun ki ?
Kaman zatayi kuka tace ba komai, juyawa tayi ta fice daga palon, mikewa Mom tayi da sauri zata nufeta, Dad yayi saurin dakatar da ita
Yace "karki damu, indai Salma ce she will over come any obstacle, mu bata time"
Zama Mom tayi jikin ta duk amace, tana son Salma duk wani damuwa ta Salma bataso.

***

Mujahid na shiri kunna Motarsa yaga Junai ta fito da saurin ta sanye da Uniform, tuna abunda ya faru jiya yayi, da sauri ya karasa inda take tahowa.
Murmushi ya sakar mata yace "autar mu ya kike..
Bata rai tayi zata wuce ya kuma jan motar gabanta, "Junai am sorry nasan namaki laifi jiya".

Sai sannan ta kalleshi, turo baki tayi tace naji"
"Zona kaiki skull".
"Banso" ta fada.
"Baki hakura ba kenan, toh bara na fito nayi kneel down n seek for your forgiveness" shirin bude motar yayi tayi saurin dakatar dashi, "yaya unless kai zakazo kayi picking dinta"
Murmushi yayi yace "i promise"
Itama murmushin tayi sannan ta shiga motar yaja.

***

Salma kam tunanin abunda zata wa Mujahid take dan huce haushi, tana isawo Traffic light ta tsaya jiran Green light, tagumi tayi tahau saka da warwara, kaman ance juya ta juya left hand side dinta, Mujahid tagani zaune da wata mai Uniform suna hira shi kuma yanai sakar mata murmushi.

Haushi ne yakamata yadda ta ganshi cikin nishadi meanwhile gata nan kaman ta mutu, saidai tasan abunda xatayi.

Grean light na nunawa Mujahid yaja yayi gaba, lane dinsa ta koma tafara binsa a baya har suka isa makaranta junaina, tana ganin Junaina tamai nuni da 12 xai dawo daukan ta sannan yamata bye yaja yabar gurin.

Dariyan Mugunta Salma tayi, tun bata aiwatar da kudirin taba taji farin ciki ya mamaye ta, reverse tayi ta koma baya inda taga wani Toy Store, shiga tayi ta siyi Bindigar wasa ta yara wanda idan ka ganta zaka dauka ta gaske ce, can gefe tayi parking zaman jiran 12 yayi.

12 nayi taga anfara fitowa, wasu anxo daukan su, daga can nesa ta hangi Junaina tsaye da kawayanta, sundan jima tare sannan suka mata bye suka wuce.
Kunna motar Salma tayi ta karasa daidai Inda Junaina take tayi wining glass, Kallon ta Junaina tayi tana Murmushi.

Murmushi Salma tayi ta fiddo takarda a Jarkata tace "you are...".
Katse ta Junaina tayi tace "am Naina, nyc meeting you" Hannu Junaina ta mika mata zuciya daya, harga Allah taji Salma ta kwanta mata arai.
"Shigo mu tafi, Officer mujahid ya aikoni kaiki office dinsa daga nan ku tafi gida..". Acewar Salma batare data mika mata hannu ba.
Junaina baki har kunne ta zagaya ta shiga gaba ta zauna Salma taja motar, adaidai lokaci shi kuma Mujahid yayo kwanar Makarantar.

Sun glasses dinta Salma tadau ta saka a fuska hade da kara daure fuska tamau, Junai kam banda murmushi ba abunda take.

Wayar Salma ce tayi ringing, daukar tayi tasa a kunne suka fara magana da wani, can kuma tace "Tk hop dai kazo da igiyoyin ".
Daga can yace eh.
Tace na kusa karasowa, katse wayan tayi.

Junaina taso tagano wani abu saidai bata fahimci komai ba saida taga sai tafiya suke ba

alamun tsayawa, gabanta ne ya fadi, nan take ta gano sumtin is not right.
"Sister kince office din Yaya zaki kaini" junai ta fadi.
Banxa da ita Salma tayi, kara tambaya Junai tayi, afusace Salma ta fiddo Bindigar, cikin tsawa tace "zakimin shuru ko saina harbeki...
Jiki na rawa Junai tayi shuru, Suna zuwa Dutsen Alhaji suka doshi wani daji, Salma ta sayar da motar hade da nuna mata bindigar.
Jiki na rawa Junai ta sauka, ganin maza biyu tayi gabanta rike da igiyoyi, "ku daure ta " Salma ta fada.
Ihu Junaina tayi cike da tsoro tace "baiwar Allah mina yi miki, wace ce ke?
Dariya Salma tayi tace "Mujahid bai taba baki labari na ba.
Cikin muryan kuka junaina tace "karya kikema yayana nasan baisan ki ba, kuma baya harka da Karuwai, kidnappers irin ku....
Wani wawan Mari Salma takai mata, nan Take kan Junaina ya juye, star, moon harma da rainbows ta fara gani saidai ta kasa tantance wanne ne wanne......

Tofah......
Muje zuwa.......

Labari don start ooooo
[9/7, 12:37 AM] Xarah Bukar: Zuma Sai Da Wuta

~na~
©χaraђ bцkar
®NWA

27 - 30

Zaman minti biyar Mujahid yayi ba alamun fitowar ta. Wani guard dake guri ya tambaya yacemai ta jima da tafiyA. Bai damu ba yaja motarsa yayi gaba, atunaninsa tabi motan friends dinta, office ya wuce abunshi.
Dakyar junaina ta dawo hayyacinta bayan wasu tsuntsaye data ga suna lilo bisa kanta tsabar rad'ad'in marin, nan take tsoron ta yadawo sabo sai sannan ta ankara da tuni sun daure ta da igiyar ajiki wata bishiyar kwakwa dake gurin.
"Welcom back" Salma ta fad'a daga inda take hakinci kan dutse dake gurin, maza biyun na tsaye bayanta rike da hangbag dinta, fuskar ta daure tamau babu annuri.
Kuka sosai Junaina ta fashe dashi, farar fuskar tuni ya sauya launi zuwa ja, ga wata uwar yunwa dake addabarta ko breakfast batai ba tafita skull..
Gyara zama Salam tayi tace "gwara ma kibar kuka, cox i wont spare you, ina da Unfinished business da yayan ki"
Cikin shesheka Junaina tace,
"koma miye kuyi settling tsakanin ku, dan Allah ki barni na tafi gida, ina da exam gobe"

"Okay, lemme c if yayanki zai dau call dina" jakar dake hannu guy ta amsa ta ciro wayarta sannan tahau dailing no din Mujahid.

Yana ganin Call din Salma tsaki yayi, bai dauka ba yacigaba da aikin gabansa, saida ta kira sau kusan hudu ba respond sannan ta kalli Junaina, dariya tayi tace "it seems today isn't your lucky day"
Adan tsoro junai ta ware ido, Salma ta cigaba "nan da 3 hours idan baiyi picking call dinaa ba i won't hesitate blowing your brains out" karashe maganar tayi tanai mata nuni da bindigar.
Junai kam ta gama firgita, kuka sosai take, tashi Salma tayi ta koma mota ta zauna zuciyarta na radadi, tana ji ajikinta sumtin is not right saidai bata san miye ba, ayanxu burin ta kawai ta rama abunda Mujahid yayi mata, kwantar da Sit tayi ta kwanta hade da sanya earpiece kunne tahau sauraran wakar freedom ta Akon.

****

Shuru har karfe hud'u Junaina bata dawo ba, shiga dakin ta Hajiya tayi taga wayam.
"Ikon Allah, har yanxu bata dawo ba" ta fada, nambar junai ta kira taji ta ajiye kan dressing mirror tanai ringing. Daya daga cikin mai aikknsu kande ta kwalawa kira, tana zuwa tace "kikace da mujahid junaina ta bar gida da safe"
"Eh" kande tace.
"shuru dai bata dawo ba, bari na kira mujahid"
Kira nambasa tayi, shikam alokacin ma ya fito masallaci sallah la'asar, office xai koma yaga call din hajiya, dauka yayi tace
"kuna tare da Junaina ?
Cikin rashin fahimta yace
"Yaushe?
Hajiya tace "bata dawo gida ba, tun bayan daka fita da ita"
Bata rai yayi. "nifah dropping dinta kawai nayi a skull...
"Toh kaje ka dauko ta" kaste call din tayi batare data jiran cewar saba.
Guntun tsaki yaja, aransha shi yana fadin yaran biyun nan fitinar su bata karewa, i dont have time for their nonsense" wucewa office yayi.

Ta bangaran Salma kuwa bata kuma trying no din Mujahid ba, haka tayi ta zamanta a mota daga bisani ne ta fito gurin Junai, ganin yadda ta galabaita yasa ta tura Tk cikin gari siyo mata abinci take away da drink, bayan ya dawo ba yadda batayi ta bawa Junaina abincin, fir taki karba taci banda tsine mata data dunga yi tana kuka.
Yammace ta doso, hakalin Salma yafara tashi, tunanin kar dare yayi masu gurin, uwa uban idan mujahid bai dau call dinta ba batasan ya zatayi da Junaina ba, tsoro ne yakamata kar yarinyar mutane ta mutu a hannu ta...wayarta ta kalla ta hau turama Mujahid Text msg.
Kaman bazai duba ba sai kuma yafasa ya bude sakon "pick d damm call before i murder your stupid crying sister".
Gabansa ne ya fadi, hankali tashe ya mike tsaye cikin rawar jiki yafara neman nambar ta, saida tayi ringing sau biyar sannan ta dauka..

Cikin fusata yace "dont tell me dagaske kike
Tsaki taja.
"do you take me as a joke" kusa da Junai ta karasa hade da riko gashin kanta, ihu junai tayi cike da azaban rikon da tai mata, wayar Salma ta dasa mata akunne, muryar Mujahid taji akid'ime yana cewa "Auta ki kwantar da hankalin yanxu zanzo...".
Maida wayar salma tayi kunnan ta sanna tace "kaji ai da kunnan ka".
Ran sa yagama baci, cikin daga murya yace "What did you want, say your price ?
Harara tayi kaman tana ganinshi, tace
"If you keep yelling at me i wont negotiate, so better calm yourself muyi magana like gentle people".
Kaman ya shaketa yakeji, kwantar da murya yayi.
"Duk abunda kikeso xan maki kuma zan baki ko miye, but plz leave my sister out of this"
Shuru tayi tana tunanin mai takeso gareshi, can ta tuna da abunda ya faru a Qrand Square, k'ala mata satan 50k da yayi saita tatikeshi hamsin sau goma.
Murmushi tayi tace "500k nakeso,
Iya k'uluwa yakai yace "aini ba ubanki bane dazan dauki 500k na baki, su kananan kwari da kike bi miye amfanin su"
Dariya rainin wayo tayi sannan ta bata rai tace "idan banga alert nan da 10 minti ba, forget you i have a sister" dif ta kashe call din.

Hauka ne kadai yarage Mujahid baiba, kaman wani zaki ya hau huci a office din, yasan Salma is a bitch saidai bai taba tsammanin she can stoop so low tayi kidnapping Junaina ba much less tayi demanding makudan kudi haka ba, tsoronsa daya karta gano Gidansu tunda har ta iya sato Junaina, Allah kadai yasan a ina ta gano shi as yayan Junai.
Karar shigowan text msg na account no dinta ne ya katsemai tunani, da sauri yadau ipad dinsa ya shiga yi mata transfer din kudi, amma a zuciyan shi yayi alwashi karbo kudin sa dan kuwa bazai bari taci bulus ba.

Salma naji alert tasa Su Tk suka kunce Junai, dakyar ta iya takawa suka karasa mota ta shiga abun tausayi, kallon su Tk Salma tayi sannan ta zaro 20k ta basu tace "aikkn nan bashi da amfani ku kama sanaa koda wanki da guga ne".
Sukam godiya sukai sosai cike da murna, dama rashin nasha da ci ke sanya su yin wani abun.

Shiga motar Salma tayi taja, Junai na zaune tana sauke numfashi wahala, hawaye take zubarwa, kanta dauke gefe tanai kallon waje.
Kiran Mujahid tayi, da azama ya dauka tace "ka fito tsakiyar cikin gari" katse call din tayi, yakuma kira bata dauka ba, saida ta iso National stadium sannan tayi parking, ta turamai text din inda take, kallon Junai tayi tace "kina iya sauka"
Kaman jira take ta bude motar, zata sauka taji Salma tace "am sorry idan kinji haushi na"..
Da karfi Junai ta rufe kofar batare data tsaya sauraran taba, saidai kalmar idan kinji haushi da Salma tace ya mugun kara bata mata rai, "wana kare xaa ma cin kashi haka yak'i jin haushi, itama dai tasan abunda tayi can never be forgotten or forgive" azuci junai tayi maganar, can gefe ta zauna akasa jiran Mujahid.

Cikin rashin damuwa Salma taja motarta tayi gaba.

Baafi minti 20 ba Mujahid ya iso gurin hankali tashe, da sauri ya sauka ya riko ta suka shiga motan yaja, ba abunda bai tambayi Junai ba fir taki magana har suka iso gida, Nan suka iske Hajiya da Jaafar shima alokacin ya dawo aiki yaga hankalin hajiya tashe, fitowa neman junai zasuyi sukaga motar Mujahid ya shigo..

Kafin ya tsayar da motar Junaina ta bude kofar ta fito, da gudu ta karasa gurun jafar hade da fadawa cikin sa tanai kuka mai tsuma zuciya.

Tambayan miyasa meta jaafar yahau yi, bata iya bashi amsa ba sai kuka, yajata suka shiga ciki.

Mugun kallom Hajiya tama Mujahid dake tsaye bayan ya fito motar, kaman marar gaskia haka ya koma.

Fuskar hajiya ba annuri tace "ina ka kaita, mai kayi mata..".

Shuru yayi baice komai ba, tsoron sa daya kar Junaina tama hajiya Description din Salma, yasan Hajiya dason bin diddigi.

Wayar hannuta Hajiya ta danna hade da kiran Aunty Bilkisu, fitowan ta kenan daga NNPC clinic inda take aiki. Hajiya tace da ita ta biyo ta gida Junai ba lapia.

Hararan Mujahid tayi sannan ta kama hanyar komawa ciki.

Zaunar da ita Jafar yayi kan gadonta yanai kara tambayan ta, jikinta gaba daya rawa yake, cikin muryan tace "wata yar Mafia ce ta saceni, kuma da alamun tana da wani Dirty relationship da yaya kuma fah her face looks familair i just dont know ina na santa"

Riko hannuta yayi yana lallashinta yace "ko Faizan Umma ce.

Kada kai tayi "Aunty faiza is too naive, ba ita bace wannan fah so pretty gata black beauty saidai zuciyan ta ba imani, i was so scared, kiris yarage bata harbe ni da bindiga ba" duk cikin Kuka take maganar, fuskar ta gabadaya ta kumbure.

Hankali jaafar ne yatashi, yau kam sai yayi confronting yayan shi, Hajiya ce ta shigo, ba tambayar da batai ma Junaina ba, taki gaya mata komai, sai cewa tayi b'ata tayi sunje gidan kawarta.

Aunty Bilki na karaso wa ta duba Junai hade da bata pain relief, sai sannan hankalin Hajiya ya kwanta atunanin ta ko wani abu mugun abu Mujahid, dakyar Junai ta iya tashi tayi wanka tayi alwala sannan ta fito tahau jera salloli.

Rai bace Jaafar ya haura sama, dakin Mujahid ya fada ba tare da Sallama ba, tsakiya dakin ya iske shi zaune akasa kan center carpet, hannusa rike da Sigari yana busa, daga ninsa cikin tsananin baccin rai yake.

Yana ganin Jaafar ya dauke kai,

Kansa jaafar ya karaso ya tsaye yace "wace yarinya ce keda guts din kidnapping junaina sannan kai kuma as a policeman you aint doing anything about it ?

Banza dashi Mujahid yayi, dan kuwa ayadda ranshi ke zafi sai iya haushi da duka.

Kafadar sa Jaafar ya riko yace " stand like a man and talk to me, ko nima tsoro na kakeji kaman yadda tsoron yar mafia ya hanaka arresting dinta..".

Azabure Mujahid ya mike yana huci, iya karfin sa yasa ya ture Jaafar wanda saida ya bugu da D mirror dake gurin, glass din ya face, da gudu Hajiya da Aunty b suka hauro sama.
Mugun naushi Mujahid ya kaimai a fuska, nan suka cakwade suka fara dambe, akideme su Hajiya suka fado dakin, Salati ta saki tahau kokarin rabasu, jaafar ta janye gefe wanda tuni bakinsa yafara zub da jini, fadi yake "matsoracin kawai, ai fitowa xakayi ka fadi abunda ya faru bawai kayi shuru"
Rufe mai baki Hajiya tayi tana jaafar yi shuru ya isa, mujahid kuwa huci kadai yake, ganin yadda attention din Hajiya da aunty b na gurin Jaafar yasa shi fara harhada kayan shi cikin akwati, atsorace Aunty B ta kalle shi Mujahid miye haka, ina zaka.
Baibi takan taba ya hade kayansa a kwati yaja ya raba gefen su ya wuce, Janyo Aunty B hajiya tayi tace "kyaleshi ya gama fushi, muje ki taimaka wa Jaafar" ba musu Aunty B ta riko jaafar suka sauka kasa, kallon dakin Hajiya tayi taga sigari dake baje agun, kai ta girgiza tace "Allah ya shirya min kai Mujahid"

Afusace Mujahid ya fada mota yaja, bai zarce ko ina ba sai Louis House nan inda gidajan mayan yan sanda Nigeria suke, babban Flat dinsa ya nufa, security dake gurin ya bude mai gate din gidan, hadaddan gida ne mai dauke da 3bd, 2palo ds kitch sai haraban gida da garden ta baya, ko dauka akkwati bai ba ya shiga gidan, ciki ma ya hadu ba karya..
Dirshan yayi kan kujera ya dafe kai kaman yayi kuka, shi kadai yasan abunda ke yawan mai azuciya.

Da nishadi Salma ta karasa gida, dakinta ta fada ta kwanta abunta kasancewar hutun sallah take, so take kadai taga Fuskan Mujahid, hotonsa ta dauka tana kalla hade da sakin lausassiyar murmushi.

"***

Washe gari kam Junai da zazzabi ta tashi, Neco sukiyi kuma aranar zasuyi Math, dole ta hakura ta zauna a gida ranta duk abace wani mugun tsanan Salma take ji aranta.

Mujahid baiyi niyyan fita ba tsananin yadda zuciyarcsa ke tafarfasa, haka ya daure ya fita dan zuwa wani programme da yan Gwagwalada University suka hada mai suna Nigeria law & constitution da zaayi a Sheraton Hotel, kwata kwata bashi da raayin zuwa, koda suka turo mai Gayyata bai amsa ba ya zabi wasu a office su wakilteshi, Faiza ce data kira shi awaya ta nace saiya je dan itama zataje, kasancewar lectures da dama zasu da kuma yan aji biyar masu karanta Law. Gidansu yaje ya dauke ta by 5pm sannan suka wuce gurin.

Suna Gama 2 to 4 lecture Salma ta dawo gida, hankalinta kwance bata da damuwa, tana son ganin yadda fuskar Mujahid zata kasance saida ta rasa ya zatayi, "kila ma jiya yayi kuka" ta fada aranta, dariya tayi. Ta fiddo wayarta kiran Salim dan jin ya yagansa da safe a office, tana bugawa salim ya dauka, hayaniya sosai taji tahau tambayan yana ina, yace yana Sheraton an gayyace su wani programme nayan skull dinsu,"
Tace "harda ogan ka kenan"

Shuru yayi yasan wa take nufi, tace ka fito waje nanda 30 minti gani nan"
Katse wayan tayi.

Da gudu ta shiga gida, agurguce tagaida mom ta fada toilet, wanka tai ta fito ta shirya cikin wata short Golden Gown mai adon crystal stone, hannu shi dogo ne, sai kuma red 6 inches shoes data sanyawa karfa ta, dama ba wata doguwa bace sosai, hill din yayi dagwas da ita, gashin kanta ta tamke waje daya sanan ta dauko weavon cap mai kananun kitso ta sanya kanta hade da tufkewa one side, kwalliya tayi ta kyace raini, sannan tadau wayoyinta da clutch purse red ta lallaba a guje ta fice, motarta ta shiga taja at 360 zuwa Sheraton.

Babbab hall ne mai shegen kyau, kowa zaune a round table mai dauke da sit din mutum biyu. Wani law student ke bayani anai mai tafi.

Mikewa Mujahid yayi, faiza tayi saurin zaunar dashi "Mjay kayi hakuri, ankusa gamawa, wai miya faru ne naga duk ranka abace"
Kwafa yayi ya koma ya zauna ba tare dayace uffan ba, Salim nagani ya mike yayi waje (ni xarah nace oga ta iso).

Gyaran Muryan Mc yayi yace "muna son volunteers na face of Gwagwalada na 2017, ina kyawawan suke" duk yan gurin dariya sukayi, saboda yadda ya fadi cikin salon shakiyan ji. Yacigaba "harkar nan fah no student no lecture, mutane da dama nema suke basu samu ba" Dariya yan gurin suka karayi, Mujahid kam ya kosa ya bar gurin, Faiza kam so take ta tashi as volunteer amma tana jin kunya, tasan dai tana da kyau gata fara, muddin ta zama face of gwagwalada ba karamin respect zata samu ba.
Kaman an tsikarate ta mike tsaye, kallon Ta MC yayi yace "Are you in".
Ba kunya tace yes" ihu da tafi aka fara, dan kam tana da kyau ba karya..Mujahid kam inda akwai bindiga kusa ba abunda xai hana ya harbe ta dan haushi.
Takawa Stage din Faiza tayi, cikin jin dadin yadda aketa hailing dinta, MC yafara fasa mata kai da zuzuta kyan ta, can yace "she is damm beautiful, akwai wanda ke opposing beauty dinta? "No" hall din ya dauka, Faiza kam she just dey feel her self.
Daga hanyar shigowa sukaji muryar Salma tace "i appose"
Mamaki kowa yayi, kallo ya koma kanta, wasu sun santa a skull wasu kuma yau suka fara ganinta, Takawa Salma tayi kan Stage din cikin yauki da kwarkwasa, Mujahid Kallon ta yayi yana rokon Allah kar zuciyarsa ta buga dan haushi dressing din da tayi, wani mugun tsanan tane ya sokesa a ziciya

MC yace "miyasa kikace haka yammata...
Harara takai mai tace "saboda na fita kyau, black is beauty...
Ihu yan Hall suka kwashe dashi, wata igbo gal dake zaune ta mike tahau stage wai bata yadda ba, itama tana da kyau ai, MC kam yaga ikon Allah, 3 people fighting for one thing, dabarace ta fado mai.
Yace "Ba karya duk kuna da kyau, but mutum daya akeso, saidai Ayi Bidding"
Faiza kam ji tayi kaman ta shake Salma, bata rai tayi tace ta siya 50k, Igbo gal dasan kudi ko

sisi bata saba ta sauka da gudu, Salma tace tasa 150k, kwafa Faiza tayi yaukam saita kure yar iskan yarinyar nan, tace 200k, Salma tace 500k, shuru faiza tayi kaman tayi kuka, dan kudin ta da take maneji da rike gidansu baima kai 500k

Ihu kowa yayi Salma ta burge su, Salim kam mamaki yayi yasan Daddy na tsakarwa Salma kudi, amm 500k yayi yawa tayi wasting abanza, Mc kam baki har kunne sun samu kudin banxa, atake ta masu transfer din kudin, crown ya dauko zaisa mata tace "no need, d title is okay for me" juyawa tayi tanai wani sexy cat walking ta fita agurin, wani ihu hauka aka farayi, jiki sanyaye Faiza ta sauka, gurin Mujahid ta nufa tace tashi mu tafi"
Baiko kalle taba ya raba gefenta ya wuce, da gudu ya karasa haraban waje inda Salma ke tafiya, gabanta ya tsaya yana murmushi sannan yace "congrat"
Daure fuska tayi
"I dont need your congrats saboda nasan your heart is burning right now, so gwara ma kar kayi pretending"
Rab'awa tayi gefe ta wuce, ya kuma shiga gabanta, hararar sa tayi tace "am done with you nonsense, am begging you ka fita rayuwata, kamin laifi na rama, kuma na hakura, stay away from me" wucewa tayi gefen sa.

Murmushi yayi ya tsaya kallonta harta shige motan ta, aranshi yace "kin shigo rayuwata kuma no way out..."
[9/7, 12:37 AM] Xarah Bukar: Zuma Sai Da Wuta

~na~
©χarafj bųkar
®NWA

31 - 33

Tsaye Faiza tayi tanai kallon shi, saida yaga motar Salma ta bar gurin sannan ya taka zuwa tasa mota, shiga yayi ya zauna yana cigaba da murmusawa, jiki sanyaye Faiza ta shiga yaja, sunyi nisa babu mai magana da wani, kowa da abunda yake sak'awa a zuciya.
Dakyar dai faiza ta samu courage din yimai magana, duban shi tayi fuskar sa fayau ba damuwa tace.
"Mjay badai ka fara folawa yarinyan nan ba?"
Kallon ta yayi yace
"I dont tink so, amma koda ace na fola mata ai it isn't a crime ko ?
Marairace murya tayi
"Kawai naga she isnt d right person for you, kuma ma you deserve more.."
Katse ta yayi da cewa, "tnx for your concern, i decide what i want and what i don't want"
Shuru tayi, ta shak'a ba kadan ba, sun danyi nisa yace "When are you ready to settle down
Aranta tace kai nake jira, afili tace "very soon, kasan komai lokaci ne kuma sai Allah yayi"

Daure fuska yayi Yace "kafin lokacin learn to respect youself bawai kina embarrassing kanki kamar yadda kikayi dazu ba, you ain't a kid any more"
Kallan takaici tamai, ita bataga wani bad abu datai ba dazai ce haka alhalin ita waccan data siyar da mutuncin ta lallab'a ta yaje yayi.
Bata iya cewa komai ba har suka iso gidansu, sauka zatayi taji yace "yaushe kike da class ?
Abunka da cool headed person, murmushi tayi tace "jibi"
"Allah ya kaimu" ya fada yaja motar yayi gaba.

Salma na isa gida ta hadu da Mom, fada sosai tasha da irin dressing din datayi, haushi biu ne ya hade mata, daki ta shiga tacire kayan sannan ta zauna kan gado tunanin abunda ya faru tahau yi, ta jima zaune daga bisani ta mike, hoton sa dake gurin tadau ta wurga ciki karamin trash can dake dakin sannan ta koma ta zauna zuciyarta na zafi.

***
Yau kam jikin Junaina ya warware, bataje skull ba saboda intervel na kwana biyu da take dashi, duk babu dadi takeji barin Mujahid gidan, ganin su Hajiya ko ajikinsu yasa ta nuna ita ma bata damu ba, tana son kiran shi awaya amma tana tsoro, ganin take idan ta kuma mai magana yar Mafia zata iya cafko ta.

Zaune Mujahid yake a office tare da abonkinsa Mubarak, sun dan tattauna issues daya shafin aikin su sannan Mubarak ya gangaro mai da cewa, "wai ya ake cikin da diyar Alhaji Abbas ?
Mujahid kam kaman jiran tambayan yake, ya jima yana son mai zancen Salma amma ya share, Dariya yayi Yace "yarinyar nan bomb ce, nan ya tsarawa Mubarak duk yadda ake ciki tun farkon haduwan su sannan ya kara da cewa "d worst part of the story itace same Ummi da Hajiya take nema ruwa ajallo"
Ware ido Mubarak yayi in shocked yace "abokina mai kake jira, ai albishir zaka ma Hajiya, komai yazo cikin sauki"
Mugun harara Mujahid ya sakar mai yace "yadda na tsanin yarinyar nan bana fatan gan inta gidanmu, what am curious about shine ya akai ta koma diyar Alhaji Abbas sannan kuma why is she alway acting bitchy, deep down nasan akwai something good about her"
Nisawa Mubarak yayi
"Toh ai ita zaka tambaya bani ba.
Muhajid yace "She isn't stupid da zan tunkareta da tambayoyi ta amsa min"
"Ai dama ba zuwa xakayi kafara jero tambaya ba, make friends with her, you can pretend loving her, kasan mata da rauni daganan saika tatso information da kake son sani"
Dariya sosai Mujahid yayi sannan yace "ajiye love aside, yadda na tsane ta i can't even pretend, abu daya zan iya shine mu zama friends, when am done with her sai nayi destroying dinta for good kaga na rama abunda tamin"
Kallon shi Mubarak yayi aranshi yace "this is serious, i cnt wait naga karshen Drama dinga" Afili yace "Allah ya bada saa, if you need my help kamin magana"
"Bani address din gidansu". Mujahid ya fada.
Ba musu Mubarak ya bashi dan kuwa Gidan Alhaji abbas sanan nene.

Salma ta warware, cikin walwala take, duk wani abun da zai b'ata mata rai kawar dashi tayi, basu da lec sai gobe, kitchen ta wuni tana taya mai aikin su abincin dare, bayan sun gama, ta jere komai a dining sannan ta shiga ta kara wanka ta sanyawa jikinta doguwar rigan kanti, bayan sallah ishai ta nufi Dakin Mom, sun jima suna hira, mai aikinsu Lami ta shigo tace maigadi na magana wai wani na kiran Salma awaje, tsaki Salam tayi tace kice mai bana fitan dare, ba masu Lami ta juwa,
Mom tace "kinma isa, ai tashi zaki kije kiga waye, dama tuni na fara jin kamshin yan jikokina"
Dariya Salma tayi bata da niyyah tashi, ganin mom ta bata rai yasa ta mike, daki ta shiga tasa Hijabi sannan ta fito zuwa waje.

Jingine yake cikin motarsa, agogon hannusa ya duba yaga 8.30 tsaki yayi, maigadi ya fito yace mai Salma bata fitan dare, bai damu ba yasa aranshi gobe zai isketa a school, shiga mota zaiyi yaga wata mota ta danno gurin gate din, tsayawa yayi, Daddy ne a motan tare da Driver, Wining glass yayi yace "yaro aida ka karaso ciki, halan wa kake nema...
Kafin Mujahid yayi magana salma ta fito, gaida Daddy tayi aladabce, tana ganin Mujahid ta juya zata koma ciki, Daddy yace "salma jeki mana, ba gurin ki yazo ba"
Yaken dole tayi ta amsa da toh ta karasa gurin Mujahid shi kuma Daddy ya shiga gidan.

Dan nesa dashi ta tsaye hade da kawar dakai gefe, kallon yayi aransa yana jinjina yadda ta bawa Daddy respect, dan matso wa yayi kusa da ita, murya ciki ciki yace "baza ki gaishe da bakon ki ba"
Yadda takeji tsanan shi bazata iya tanka shi ba, juyawa tayi a fusace xata wuce,
Yace "Ummi".
Wani irin shocked taji, gabanta ne ya fadi, she can't recall wen last data ji Ummi abakin wani.
Ganin yadda ta daskare agurin yasa Mujahid shan jinin jikinsa, sam baisan ya furta sunan Ummi ba, wayancewa yayi dacewa "Miemie, momy, ummita kinsan bansan sunan ki ba, dole yasa nahau guessing..."
Ajiyar zuciya ta sauke, saidai taji dadi yadda ya kirata da Ummi, juyowa tayi tace "Sunana Salma"
Yace "nice name" kalan ta yayi tamai kyau sosai.
Hararar sa tayi tace "kaga Malam miye ke tafe dakai, indai 500k dinka kazo amsa toh babu na zubar a titi"
Murmushi yayi.
"Karki damu nina yafe maki, nazo ne muyi sorting difference dinmu"
Shuru Salma tayi tanai mai kallon banxa.
Yacigaba "can we be friends ?
Mugun Dariya rainin wayo Salma ta face dashi, sannan ta daure fuska tace "you're not serious" juyawa tayi ta koma cikin gida, tana gudun dumamai zagi a zuciyanta.

Shima dariya yayi ya koma mota yaja yabar gurin.

Kicibis Salma tayi da Salim bakin gate, da alamun lekan su yake, hannuta ya riko

Fuskar daure yace "Salam ki gayamin gaskia, mike tsakanin ki dashi, jiya da yau sam bangane mai kuke nufi ba"
Fizge hannuta tayi, cikin daga murya tace "mind your business and stop acting like a fool" afusace tayi gaba ta barshi da sakin bakin Fool data kira shi dashi, kwafa yayi ya wuce part dinsa zuciyarsa na kuna...

****
Washe gari, 12 to 2 su Salma ke da lecture din Faiza, da wuri ta shiga skull, mutane sai mata congrats din face of gwagwalada suke, ko kallan su batai ba ta karasa Hall ta zauna, baa jima ba Faiza ta shigo Tafara masu lec, bayan ta gama ne ta sanar dasu test datai masu is cancelled, ihu sosai yan aji suka fara dan kuwa sunsa basu tabuka abun arxiki ba, Salma kam baki ta Tabe ko ajikinta.
Faiza na shirin fita hall din ta kalli Salma tace "ki sameni a office".

Bayan kaman 10 mins Salma ta taka zuwa Department, office din Faiza ta shiga ta iske ta zaune, da alamun zaman jiran Salman take.
Zama Salma tayi kan kujera dake gurin ba tare data jira permission dinta ba.
K'wafa Faiza tayi tace "zan baki A a course dina kuma zan biyaki idan kikayi min alkawarin fita harkan Mujahid"
Mugun Kallo Salma takai mata aranta tace "what an insult, aiko banyi karatu ba ina iya cin B, kudi kuma ai baki dasu"
Afili tace "I assume kin kirani muyi magana woman to woman not lecturer to Student ?
Kad'a kai Faiza tayi tace "duk yadda kike tunani hakane".
Mikewa tsaye Salma tayi tace "y not kibiyani na tursasashi ya soki, tunda naga har yanxu bakya gaban shi kuma shekarun ku na tafiya"
Hannu Faiza ta nuna mata alamun gargadi tace "karki kuskura ki zageni, cox am not your mate"
Dariya Salma tayi.
"Yes ma, amma abunda baki sani ba shine if you keep following him around like a fool, obeying is orders bazai tab'a sonki ba"
Afusace Faiza ta mike tsaye tace "enough, kawai ki fadi abunda kikeso"
"Ni banaso komai, ki rike kudin ki, grade dinki da Mujahid all for youself cox i dont give a fucking dammm about dem" juyawa Salma tayi, Faiza tace karya ne i know you love him".
Salma kam tagama kulewa, kallon ta tayi tace "love huh !!! Ki kalleni dakyau banda lokacin soyayyar shirme, infact the word love doesn't exist in my Dictionary"
Afusace Salma tabar office din hade da banging door.

Rai bace faiza ta zauna tana nazarin abunda Salma tace, kai ta gigirza tace "so take nadaina binsa na nadai obeying abunda yace kenan" tsaki tayi ta kuma cewa "karyan banxa sodai take nafita harka Mujahid danta samu shiga, toh yarinya kinyi kadan" kamar Tababbiya Faiza tahau surutu ita daya a office.

Ran Salma atafashe yake, tafe take tana zage zage ita daya, "wai harni zata siya saboda soyayar wani banxa da ban damu dashi ba, this woman is crazy how i wish ina son Mujahid da taga iskancin dazan mata" masifa tahau yi harta karasa gurin motar ta, key ta ciro zata bude taji murya kaman ta Mujahid abayanta,
"Hey" ya fada yana kallonta, tsaye yake a gefe inda ya parke motar sa.
Jin hadadan kamshin ya gauraye gun yasa ta tabbbatar shine, bata juyo ba saida ta bude motar, Bindigarta ta roba dake boye karkashin sit ta dauka, sannan ta juya gareshi afusace tanai nuna mar Bindigir, "am warning you, stay away from me"
Shikam kallonta yake, yau atamfa dogowar rigace ajikinta, tayi matukar amsar ta.
Dariya ya kwashe dashi ganin yadda ta nuna shi da bindigar ita a dole she's trying to scared a policeman.
"Whats funny huh ? Ta fada tanai kokarin pulling trigger kaman gaske.
Matsowa yayi kusa ya warce bindingar ba tare data ankara ba yace "Ummi wasan yara kuma kika koma yi.."
Kunya ne yakamata, sai yanxu ma tagano wawtarta.
Murmushi yayi Yace "ya labarin friendship dinmu?

Tabe baki tayi
"Am not interested"
Hannuta ya riko da saida yaji wani irin, itakam ko ajikinta yace " nasan you hate me but atleast find a place in your heart to accept my friendship"
Hannusa ta kalla dake rike da nata tace "sakeni" sakinta yayi, tace "i dont make friends with the enemy"
Rab'awa gefe tayi ta wuce ta fada motan taja tabar gurin.
"OmG" Mujahid ya fada hade da kaiwa hannu shi daya naushi, baiyi tunanin zatayi wuyan samu ba, ayadda yake ganin kuma she will never accept him. Rai bace ya koma motar sa baiko bi takan faiza ba yaja ya koma office.

Ajiyar Zuciya Salma ta saukr tana tunanin whats going on a zuciyan Mujahid, she isn't stupid da zatayi accepting friendship dinshi all of a sudden bayan ta gama swindling kudinsa through kidnapping sister dinshi, Girgiza kai tayi afili tace "it doesn't make sense, am sure he is up to something".

Mujahid na komawa Office ya nufi office din Mubarak, nan ya tsara mai abunda ke faruwa.
Tsaki Mubarak yayi yace "sai kace ba namiji ba, ka kasa karkato da hankalin ta.
Mujahid yace "am not used to shiga harkan mata, mostly suke manne min, ya kakeso nayi, nifa duk ta gama wahalar ni"
Mubarak yace "abu mai sauki tunda taki yadda da rokonta da kake, ai rik'ota zakayi, na tabbata ba dutse bace da bazatayi feeling wani abu ba, kaga daga nan kila adace"
Dariyan haushi Mujahid yayi yace "itakam Tafi Dutse, duk moves dinta ina observing, no matter yadda xan janyo ta jikina she wont feel anything"
Then try kissing her" Mubarak ya fadi.
Ware ido Mujahid yayi yace "what, gaskia i can't, tayama zan fara kissing dinta sai tayi tunanin

ko sonta nake".
Mubarak yace "exactly abunda muke so tayi tunanin kenan, koda bata sonka she will forever remember dat kiss, daga nan kuma zata dan fara kulaka koda tayi fushi mayb na kwana biyu ne"
Murmushi Mujahid yayi, ya gamsu sosai da shawaran abokinshi, sun dade suna planing yadda komai zai kasan ce daga bisani ya koma office..

Nima xarah nace bara nayi wanka kafin naje dauko rahotan yadda Kiss xai kasance 💋
[9/7, 12:37 AM] Xarah Bukar: Zuma Sai Da Wuta

~na~
©ӽarafŋ bųkar
®NWA

33 - 36

Sosai Ja'afar ya duk'ufa da neman Ummi, duk wata social media a duniya sai da ya garzaya neman masu sunan Ummi amma bai samu actual Ummii da yake nem ba, harta Yaran yan Chibok da aka sace saida ya binciko fuska kowa babu ta Ummi. Duk da ya jima da ganin Ummi amma bazai manta da face dinta ba, kusan shekaru 11 da suka wuce ya tab'a kai Hajiyar su Gombe ganin Ummi, ranar kam tasha kuka ba yadda batayi ta biyo suba Matar Babansu ta hana dagabaya ma Baban cewa yayi su tafi karsu kara zuwan mai gida.
***
Salma kwance kan cinyar Mom a palo, latsar wayar ta take hankalinta kwance, Daddy zaune gefen dayar kujerar suna kallon tashar CNN tare da Mom.
Maigadi ne yayi sallama daga waje ana kiran Salma, take gabanta ya fadi, Daddy yace "kaishi Guess palo gatanan zuwa".
Banza Salma tayi kaman bata san mi aka ba saida Daddy yace "maza tashi kije ki sameshi, na tabbata yaron dana gani kwanaki ne, na kuma yaba da hankalinsa"
Turo baki Salma tayi tahau gunguni tana fadin "bashi da kirki wlh"
Mom tace "banson shirme, ki biya kitchen ki kaimai na shashe baki"
Takaici ne ya cika Salma, daki ta shiga ta tsayan gaban mirror tana surutai, can kuma ta janyo kayan kwalliya tahau shafe shafe da manne manne, duk dan ta b'ata mai lokaci ta tsiro da hakan, nyt wear riga da wando ne ajikinta, dan tuni dama tara na dare ta gota, ciresu tayi, tama rasa wana kaya zatasa, can dai ta dauko wata pink doguwar riga tasa hade da yafe karamin veil din, kitchen ta nufa tadau bottle water da exotic juice tanufi guess palo.

Shikam tsaye yayi palon yana mumurmushi dani kaina basan maanar sa ba, iya haduwa yayi, sanye yake da tsadadun kananu kaya sai zubai bala'in haddadan kamshi yake. Tana turo kofar palon ya maida duban sa gareta, shigowa tayi sukayi 4 eyes, gabanta ne ya fadi, wani mugun

kyau da kwarjini yayi mata, ta bangaran sama kusan hakanne, sunfi 2 mins staring at each other sannan ta tabe baki, ta karasa shiga ciki, bata bi takan saba ta wuce bayansa ta tsaya rike da ruwan da lemon, wayarta dake hannunta tahau latsawa.

Dariya ta bashi ba kadan ba, juyowa yayi ya matsa kusa da ita yanai mata wani duba, cikin cool voice nashi yace "Ummi ba gaisuwa ?"

Tsaki tayi, tadan jan baya, gabadaya ya gama tafiyar da tunanin ta, dakyar tace

"Kaga officer ba zama nazoyi da kai bai, ruwan nan kuma bazan bayar ba tunda ba gayyatarka nayi ba" cilli tayi da ruwan da lemon kan kujera.

Wani killer smile ya sakar mata yace "kinyi kyau"

Cikin k'aguwa da tsayuwar ta zauna bisa kujera dake gurin, d'aure fuska tayi tace "kaga dare nayi, wai mi kakeso dani ne, na riga na fadama am not interested da kudurin ka"

"Kinsan miya kawo ni." Ya fada yana kokarin zaman kan 3 sitter da take zaune, kaman an tsikareta ta mike tsaye "nizan tafi sai anjima" hanyar fita tayi yayi sauri rikota ta fado bisa kirjinsa, wani mugun feeling sukaji atare, ahasale ta dubeshi tace "what the helll..." Kallon daya zuba mata yasa kalamanta mak'alewa a mak'oshinta, gabad'aya ya tsareta da manyan idanuwan sa, Lumshe ido tayi yau kam takasa resisting charms dinsa dole ta tsaya tapping current, tuni ta manta duniya da take, bata ankara ba taji bakin sa kan nata, cikin wani salo taji yanai kokarin masu tsotsan Allah tsine uwar shegu, shi kanshi ya dauke wuta kokarin saisaita kanshi yake ya kasaa, Salma kam anji zuma ganin ba Sarki sai Allah yasa ta fara maidawa kura aniyarta, tuni suka fara fita hayacinsu, ringing din waryata ne ya katse masu hanzari, akidemi ta dawo daidai, janye jikinta tayi gefe tanai kokarin daukan wayar da tuni ta sullebe daga hannuta, "na shiga uku" ta fada ganin call din Mom.

Jiki mace yake kallon ta, baiyi tunanin zaiji wani pleasant feelings game da ita ba, ido ya zuba mata yana son ganin reaction dinta saidai taki dagowa ta kalle shi, durkushe take tana kallon screen din wayarta, aranta takaicin abunda ya faru take, wannan abun kunya damai yayi kama.

Murya sarke yace "Ummi

Afusace ta mike, bata iya dubanshi ba, tasa hannunta biyu ta rike kanta, kaman zatayi kuka tace "what were you tinking, are you crazy ?

Magana xaiyi ta katse shi da cewa "i cant believe this.." juyawa tayi da gudu tabar palon binta yayi yana kiranta, saidi tuni ta shige part dinsu da gudu.

Shafar suman kashi yayi yana cewa "oh my God, what have i done...." Wani mugun haushi kanshi yakeji, duk sai yaji dama hakan bata faru ba, ji yayi kaman ya bita bata hakuri, yasan bai kyauta mata ba, koma miye Mubarak ya jaza masa, rai bace ya fice yabar gidan.

Da Gudu Salma ta fada cikin gidan, babu kowa palo sai motsin Mom da taji tana kusurniya a kitchen, dakinta ta nufa tayi cilli da wayanta ta fada cikin bathroom, ruwan shawa mai sanyi gaske ta sakarwa kanta, ba karamin tafasa zuciyan ta yake ba, wani mugun tsanan Mujahid takeji aranta, haushi ta daya da yayi kissin dinta a banxa, yaci bulus alhalin babu So ko kauna tsakanin su. Kukan da ta dade batai ba arayuwanta ta fashe dashi, sosai take kuka ba kakkauta, saida tayi awa biyu sannan ta fito daure da towel bayan ta cire kayan jikinta, dakyar ta iya fadawa gado ta zube kaman mataciya, hawaye take tadau wayarta dake gun ta tura mai text msg kamar haka .

"i hate you with passion," sannan ta kashe wayar.

(Ni xarah nace Salma you too dey exaggerate, d'an kiss kawai duk kin ishe mu da kuka as if you know enjoy am).

[27/07 1:22 PM] Mujahid na komawa gida kasa zaune yayi, nan tsakiyar palo ya tsaya yana kai komo kaman wani zautacce, ganin text msg dinta yasa shi gigicewa, "nashige su, meke faruwa ? Ya fada, flashes din abunda ya faru ke yawon mai akai, nan yahau tryping no dinta yajita akashe, cilli yayi da wayan ya shiga daki, dakyar yasamu yayo wanka ya kwanta kan lausassiyar bed dinsa amma tuni bacci ya k'warace ma idanunsa, juyi yayi tayi akan gado da tunanin barkatai, abubuwa da dama zuciyarsa ke sakarmai saidai ya kasa gasgata komai, mikewa wa zaune yayi yana fadin "no, it cant be...", ganin zuciyar sa na neman tarwatsewa ya mike ya dauro alwala yahau nafilo da neman gafaran Ubangiji.

****

Washegari Salma ta tashi da zafanfan zazzabi da saida aka kwantar da ita asibiti, hankalin Mom sosai ya tashi dan tunda take bata taba ganin Salma cikin yanayi haka ba, kwanan su uku Salma ta fara dawowa daidai, data tuno encounter dinta da Mujahid wani mugun bak'in ciki take ji, haka dai suka dawo gida ta koma sabgogin gabanta bayan tama kanta alkawari fita harkan Mujahid koda ace zai kasheta bata kuma tanka shi.

Acikin kwanakin nan Mujahid shi kadai yasan irin tashin hankalin daya shiga, kullim da salmw yake kwana yake tashi, ba yadda bai ba dan yakaceta aransa amma ya kasa shi kuma yasan ba sonta yake ba, kiranta awaya da tura mata aplogy text ba wanda baiba saidai shuru kota kansan bata bi, gidansu yaje yafi adurga bai samun ganin ta.

Yau da wuri ya shirya cikin kananu kaya ya fita office, office din Mubarak ya nufa yahau shi da masifan yaja masa matsala, Dariya sosai Mubarak yayi yace "bafa sonta kake ba, miye kuma xai dameka dan taki kulaka har yanxu"
Haushi ya kama Mujahid yace "ai bance ina sonta ba, hakuri nakeson bata dan nayi realizing ban kyauta mata ba"
Tsayar da Dariyan Mubarak yayi yace "inada wani plan"
Harara Mujahid yakai mai yace "banso wani absurd plans dinka, tashi zakayi muje gidansu ka gyara abunda ka bata..
Ware ido yayi "ni kuma asuwa mi zance mata..Salma kiyi hakuri nina turo abokina yayi kissing dinki..." Cikin salon rainin wayo da Dariya Mubarak ya karashe maganan.
Takaici ne ya rufe Mujahid, afusace yabar office din, mikewa Mubarak yayi yabi bayansa yana fadin "muje kafin kayi kuka" bai kuma bar dariyan ba.

***

Fitowa Salma tayi haraban gidan, jikinta sanye da cikin red & creamy less, da madaidaicin crem veil yafe bisa kafadarta, Yau bata da lecture, sunyi da su Shehu zasu hadu Central Library yin wani Assignment da aka basu.
Motarta ta shiga ta kunna hade dayin reverse.

Mubarak ne ke tuka Motan, fuskar Mujahid Murtuke cike da haushi dariyar da abokinsa yake, suna shigowa anguwan ya hangi Motar Salma ta fito daga gidan, can hanyar titin gabansu yaga tayi, tab'o Mubarak yayi yace "kai tsayar da motar gatacan ta fito"
Tsayar da motan Mubarak yayi, Mujahid yahau kokarin bude motar dan fita.
Mubarak yace "yaukam indai taki kulaka, ka shareta kawai for good" In serious tone yayi maganar.
Shuru Mujahid yayi ya fita daga motan, Keke napep yayi saurin tarewa ya fada ciki hade damai nuni da yabimai bayan motar dake can gabansu.

Tuki take tanai bin wakar "Love will Remember" na Selena Gomez, fuskar ta fayau bata da damuwa, bata ankara ba taga keke napep a gefen ta yanai kokarin over taking dinta, tsaki taja ta kuma baiwa motar ta wuta, ta mugun tsanan ayi overtaking dinta, shikam Muhahid sai yiwa mai napep masifa yake akan yayi sauri ya shiga gabanta, wuta Sosai Salma ke bawa mota ayayinda Keke ke binta da Kero, Ranta ya mugun bacci, kwanar Babban high way tabi taga Mai keke baibar binta ba, afusace ta gangara gefen titin hade kashe motar ta fito afusace cin durun uwar sa, tsayar da Napep din yayi gaban motarta sann ya fita da sauri bayan ya biyasa.
Mutuwar tsaye Salma tayi ganin Mujahid, bata iya taku gaba ba, tayi sauri juyawa bakin motar ta bude murfin, nufota yayi da sauri hade da rike murfi.
Amarairece yace
"Salm plz ki saurarani, we need to talk"
Ko kallan shi batai ba ta dauke kai gefe, fuskarta ta daure tamau.
Hannusa ya daura bisa hannunta dake kan murfin motan, da sauri ta zame nata hade matsawa gefe,
Am sorry" ya kuma fada kaman mai shirin kuka.

Wata civic ce tazo wucewa, har tayi gaba tayo baya, maza uku ne suka fito suka tsaya gaban Salma, dayan su yace "Yammata lafiya kuwa ?
Kaman zatayi kuka tace ba "ba lapia ba, wannan mutumin ke takurani
Mugun kallo suka kaima Mujahid, yace "ba wani matsala kanwatace"
Ware ido Salma tayi tace "nikam bansan shiba, mayb ma dan yankan kai ne"
Tsorata Mazan sukayi, aikuwa suka janye Mujahid suka haushi da Duka.
Da sauri Salm ta fada motan hade da sauke ajiyan zuciya, shegen nacin tsiya ta fada aranta, kunna motar tayi ta maida dubanta baya danyin reverse, abunda tagani yayi mugun girgizata, duka sosai Mazan kema Mujahid kaman an aikosu, shikuwa baya da niyyyan guduwa balle tanka su, jibga kawai suke kaman an aiko su.
"Oh my God" ta fada cike da kidema, bude motan tayi da sauri ta karasa gurin su.
"Dan Allah kuyi hakuri ku bari, yayana ne" kaman zatayi kuka tayi magana.
Tsayar da dukan Mujahid sukayi hade da kai mata mugun kallo, dayan su yace "dama yayanki ne kika b'ata mata lokacin tsayawa dukan shi, toh kinyi kadan wallahi, sai kin biyamu dan ubanki"
Iya kidima Salma takai, dagudu ta koma mota tadau jakarta, 2k kadai ke ciki da sauri ta ciro ta mika masu, basu karba ma suka raina, hakuri ta basu fir sukaki yadda, wayar ta iphone 7 ta

mike masu tace "kuyi hakuri da wannan, it worth alot of Money"
Tsaki sukayi, suka juyawa suka fada motan su suka ja.
Hankali tashe Salma ta nufi Mujahid dake kwance yana tarin wahala ga jini ta baki da hanci. Akidime ta d'ago kansa bisa ciyarta, duk ta gama gigita tama rasa abunyi, rokon shi tahau yi akan ya tashi su bar gurin kafin maza su kuma dawowa, tari sosai yahau yi kaman wanda zai shid'e, mikewa tayi ta taimaka ya tashi sannan suka karasa motar ta, baya ta bude ta shigar dashin sannan ta fada gaba taja motar.

Tuki take amma gabad'aya hankalinta na kanshi. Murya sanyaye tace "miyasa baka gudu ba, inda sun kashe ka ya kenan ?
Yunkurowa Mujahid yayi hade da sakin dan kara, hannu yasa ya shafi gefen bakinsa dake jini, dakyar yace "i dont care koda sun kashe ni tunda ke kanki ba kaunata kike ba, gwara na mutu ki daina gani na"
Nisawa tayi tace "ko bana kaunar ka altleast kana da parent, siblings da friends da suke kaunar ka"
Tari ya kuma yi bai iya cewa komai ba.
Ta cigaba "am begging you, don't ever risk your life because of me"
Ciki ciki yace miyasa kikace haka ?
Share tambayan tayi kaman bata jiba, chemist ta tsaya, ta taimaka suka shiga ciki akamai treating ko ina hade da hadomai da magunguna, sun fito ta tambayashi gidansu dan dropping dinsa, can gidansa dake Louis house ya mata kwatance, bata damu ba taja suka kama hanyar gidan, sosai take tausayamai.

Sun iso gidan, ta rikoshi suka karasa ciki, tsoro ne yakamata ganin cewa shi daya ke gidan, dakewa kawai tayi ta zaunar dashi kan one Sitter dake gurin sannan ta ajiyemai ledar maganin gefen.

"Mai kake bukata ? Ta tambaye shi
Ruwa yace yakeso dan shan maganin, hanyar kitchen ya nuna mata ta shiga ta dauko bottle wara tare da glass cup, zubawa tayi sannan ta mika mai, hannun sune ya hade tayi sauri sakar mai da cup din, Murmushi yayi yace "ki zauna mana ?
Kai ta girgiza alaman a'a, bai damu ba yahau shan maganin hade da kurban ruwa, Salma kam kuramai ido tayi tana kallon kyakyawan fuskar shi, dukda some part sun kumbura bai hana kyansa fitowa ba, murmushi ta saki adaidai tym din daya kalleta suka hada ido, daburcewa tayi tahau fadin "xan shiga kitchen wanke hannu" da sauri ta juya ta fada kitchen hade da sauke ajiyar zuciya, saida tayi mintuna Uku sannan ta dawo palom, nanta iske shi yana kokarin mikewa tsaye, ganinta yasashi komawa ya zauna yace "na dauka ko bacci kike ai ?
Kaman marar gaskia tace "a'a ni tafiya ma xanyi" kanta na kallon hanyar fita tayi magana..
Yace "inda na mutu ya zakiyi ?
Sai sannan ta kalle shi, tace "ya zanyi kuwa ? Life goes on"
Kallonta yake saidai this tym around bai fahimci komai game da ita ba, yace,
"Amma miyasa kika taimake ni ?"
Tabe baki tayi tace "friends don't abandon friends".
Lumshe ido yayi yace
"Thank you"
You're welcome" ta fada, juyawa tayi takama hanya fita, bakin kofar ta tsaya sannan ta juyo tace

"Get well soon" bata jira abunda zaice ba ta fice.

Mikewa Mujahid yayi da axama ya tsaya bakin window kallonta, saida yaga ta shiga mota taja sannan ya ciro wayarsa dake aljihu ya kira wata namba, bugu daya aka dauka.
Cikin masifar yace " wato kasheni kukai niyyan yi ko ?.
Daga can mutumin daya dauka yace "Oga kayi hakuri, amma ai kai ce muyi making komai ya zama real, thanks goodness yarinyar tayi intervening da wuri.
Dogon tsaki Mujahid yayi ya katse call din.

Typing din yau sai ahankali wlh, kuyi sorry banyi editing ba....

*#ZSAW*✍
[9/7, 12:37 AM] Xarah Bukar: Zuma Sai Da Wuta

~na~
©ҳaraђ bųkar

*This page is Dedicated to my Cousin Sisto, Maryam abubakar Lamin (Maryeama Dasoorh), Love you so much, May Allah guide n shower you his blessings*

37 - 40

Bayan Kwana biyu da aukuwan lamarin sannan Mujahid ya fara fita office. Bai kuma bi takan Salma ba. Da azahar bayan ya fito sallah Masallacin su na office ya hadu da Salim tsaye yana waya, cike da farin ciki yake wayan, da alamun kuma da mace yake, Mugun Kallo Mujahid ya watsa mai sannan ya wuce zuwa office dinsa, zama yayi yana tunanin kardai da Salma yake waya, haushi ne sosai ya turnuke shi, Wayarsa ya fiddo ya lalubo lambar salma, son kiranta yake amma baisan abunda zaice ba asalima tun ranar yake saurara kiranta kodan tamai ya jiki, amma shiru. Dabaran Turo mata text msg yayi.
Salma zaune a kan kujerun dake ajiye gefen faculty dinsu tare dasu shehu da wasu yan ajin su suna tattaunawa game da wani course da zasu shiga test, wayarta ke kunnata tana waya da Salim, murya kasa kasa hade da dariya, katse wayan tayi, shehu yace "wannan dariya fah ?.
Tabe baki tayi, tace "yayana ne, lallab'ashi nake yakai min motata gyara ban iya jure shiga taxi"
Yace "kai yaune fah kawai kikazo da taxi, Yayan nan naki kodai dashi zaai ?
Wani mugun kallo takaiwa Shehu, ba shiri yayi azaman kama kanshi, lumshe Ido Salma tayi hade da kallon wayarta wanda tun ranar take tunanin zai kirata amma shuru, tanason sanin ya yanayin jikinsa yake, taso zuwa office din Faiza tambayar ta, saidai ta fasa gudun kar girma ya fadi kasa wanwas.. Karar shigowan sakone ne ya katse mata hanzari, tayi azaman budewa ganin Mujahid.

"Hi, kwana biyu, dafatan kin isa gida Lapia ?
Murmushi ta saki, aranta tace "sai yau ya tuna dani"
Reply ta rubuta mai, "ya jikin ka, kashe maganin?
Dadine sosai ya kamashi, baiyi expecting tamai reply da wuri haka ba.
"Am okay, when are you less busy nazo na maki special godiya for saving my life..
Gabanta ne yafadi, itakam bataso su kuma haduwa da daddare dan kuwa tsoron shi take, saidai kuma tana son ganin kyakyawan fuskan sa, tunani ta hauyi can dai tasamo mafita ta turo mai "ina skull yanxu, zamuyi cA test, kana iya zuwa kasame ni by 4pm"
Yana gani murmushi yayi, Mikewa sukayi suka tafi Hall kasancewar lokacin test din yayi.

***

Hudu nayi Mujahid ya karaso yayi parking can gaba da inda Hall din yake, lumshe idanu yayi yahau zama jiranta.
Cikin nutsuwa Fa'iza ta kankamce office dinta, sannan tadau jakarta ta fito, yau bata zo da motar taba kuma batayi tunanin Mujahid ya fito aiki ba saboda condition dinshi, can gaba da faculty tasamu taxi ta tare shi ta shiga yaja, sun shigo round kenan ta hangi Motarsa, saurin tsayar da taxi din tayi tahau duban motan, saida ta hango fuskan shi ta tabbatar shine.
Murmushi tayi aranta tace "ashe ma yazo daukata" wayarta ta duba bataga call dinsa ba tayi tunanin ko rashin netwrk. Sauka tayi daga taxi din ta nufo motarsa sa cikin sauri.
Shikam Mujahid kallon saitin gaban shi yake dan ganin tahowar Salma bai ankaraba yaji anbude kofar gefe an shigo, kallon ta yayi cike da mamaki.
Gyara zama tayi tace, "Mjay aida security ka tura office ya kirani, instead of kayi ta jirana"
Bata rai yayi yace.
"Aiba wajan ki nazo ba, kuma am not your driver..
Dariya tayi, cikin rashin kula da yanayin sa tace "wasa kake, gurina kazo kawai haushi zaman jiran da kayi kake.."
Mujahid kam bai iya cewa komai ba, hankalinsa tuni ya koma kan Salma dake tahowa tana duban cikin jarkata tana lalube, komi take nema, oho, yafada aransa, takaici ne ya kama Faiza ganin inda idanuwan sa ke kalla.

ID card dinta take tunanin kota manta a Hall yasata alube, tana gani  ta zuge jakar ta maida hankalinta kan tafiyar ta, murmushi tahau yi ganin motar sa, kadan ya rage ta isa gurin ta lura da Faiza dake hakince kan sit tanai kai mata mugun kallo, gaban Salma ne yafadi, saurin shanye murmushi tayi hade da bata rai, kaman ta fasa karasawa gurin sai kuma ta dake ta karasa saitin gurin da Mujahid ke zaune, kawar dakai tayi gefe tace "sannu"
Kallon ta yayi tamai kyau, kwana biyu nan ya lura ta daina shigar banxa data saba, jallabiya ce baka jikinta tayi rolling da veil din, kallon Faiza yayi da gefen Ido kaman yahau ta da duka, yace "ya test din ?
Haushi ne yakama Salma, "wato bazai ce shigo motar ba nice sanda mai jure tsayuwa, wlh kunyi kadan" aranta tayi magana, Afili tace "Nina tafi sai anjima" kaman zatayi kuka tayi maganar, tafiyar ta tayi bata jira cewar saba.
Tsaki Yaja ya kalli Faiza dake cika tana batsewa yace
"Miyasa kike son janyowa kanki raini, gurinta fah nazo bake ba, anjima kuma idan ta hukuntaki

kihau kuka".
Kallon takaici tamai
"Ai tare ta ganmu, kuma ma aina fita matsayi agurinka"
Kasa tankata yayi dan haushi, kunna motar yayi  yaga Salma na kokarin Tsayar da Taxi, dasauri yaja inda take yace "Kizo nayi dropping dinki
Sai sannan ta dubeshi, Murmushi tayi hade da ciro 1k dake jakarta sannan ta nuna mai tace ina da kudin motar haya basai an lab'a niba" karawa gaba tayi abunta.
Kulewa Faiza tayi tace "kaga ja'ira ni take gayawa maganar banza baka ce komai ba"
Dogon tsaki Mujahid yaja hade da watsa mata Harara, yace "ki tafi da motar gida zanzo na dauka" bai jira cewarta ba ya bude murfin ya fita, Sakin baki Faiza tayi cike da Mamaki rashin M irin nasa, k'wafa tayi cikin tsananin haushin Salma sannan ta fito ta zagaya gurinsa ta zauna hade da data motar.

Salma na shiga taxi data tsayar, taji an bude kofar baya inda take zaune an shigo, adan tsorace ta kalleshi, magana zatayi taji yacewa mai taxi su tafi, mamaki ne yakamata, "ina ta sa motar" ta fada aranta, batasan ya fito fili ba..
Lafewa yayi kan sit din hade da fuskan tarta sanan yace "nabarwa Auntyn ki ta tafi gida dashi tunda kinki shigowa.."
Kunyace ta kamata, aranta taji dadin abunda yayi tasan kam Faiza taji haushi, matsawa kadan tayi tahau bude wani handout tada ciro ajakar, Murya kasa kasa tace "ya jikin ?
Shuru yayi baice komai ba, dagowa tayi suka hada ido ta wayance da cewa "ba lafi, bruises dinma sun warke," dauke kai tayi tahau bude pages din handout din.
Dogon ajiyar zuciya ya sauke hade da lumshe ido yace, "Miyasa baki kirani awaya ba ?
"Hmm, nayi bizy ne, soon zamu fara exams"
Magana zaiyi Wayarsa tahau ringing, dubawa yayi yaga hajiya, gabansa ne ya fadi, yaushe rabo dayaji motsin su Hajiya tun randa yabar gida, gyara zama yayi sannan ya dauka, gaidata yayi ta amsa ciki ciki, sannan tace "kazo gida kasameni ina da magana da kai ."
Dafe kai yayi kaman yayi ihu, sanin maganarta batada nasaba da wacce take kusa dashi, murya kasa kasa yace "Hajiya yamma tayi, gobe insha Allahu zan shigo"
"Allah ya kaimu" ta fada hade da katse wayan.
Satar Kallon shi Salma tayi tace "wace ce ?
Yak'e yayi yace "mama nace"
Cike da fara'a ta dubeshi tace "i would like to meet her, wana unguwa take ?
Tashin hankali ne ya diran mai, dakyar yace "ba anan take ba, can Sokoto suke zama"
Harara takai mai cikin salon wasa tace "kodai bakaso nasanta ne, naga ai sister dinka anan take skull.."
Dariya yayi wanda da gangan ya tsiro shi gudun karta dago shi, yace "Amina wai, ai sunyi hutu tama koma gida can sokoto.."
Murmushi Salma tayi tace "ayyo" aranta kuma tana tunanin Amina dayace dan kuwa ba Amina sister dinshi tace sunanta ba, bata damu ba ta kawar da tunanin kasancewar taje gidan shi kuma bata ga alamu yana da yan'uwa ba.

Shuru ne ya ratsa tsakanin su har taxi ya iso gidan su.

Kallon shi tayi, gabadaya baya cikin hankalinsa, tabosa tayi, adan firgice ya kalleta, murmushi tayi tace "kana da abun dariya, kodai dukan yafara tab'a kane.."
Murmushin k'asaita yayi, irin wanda yake fizgar zuciyar wanda aka yiwa.
Yace
"Kije ki huta, i'll call you later"
Okay, bye ta fada ta fice a mota.

Gobe Birthday na 👯👯👯👯👯👯💃
[9/7, 12:37 AM] Xarah Bukar: : Zuma Sai Da Wuta

~na~
©χaraђ bųkar

41- 43

Gidan su fa'iza ya wuce amsan motarsa. Isketa ta yayi tsaye haraban gidan jingine bisa motar. Da ganin sa tahau cika da batsewa, cikin koya kula da yanayin ta yace tabashin mukullin.
Kaman zatayi kuka tace "Mjay miyasa zaka min haka gaban yarinyar nan, shikenan ta gama raina ni yanzu gani zatayi daidai nake da ita tunda kana kulata"
Kallon takaici yayi mata.
"Keda ita ba d'aya bane, you're my friend ita kuma she is nothing.."
Cikin rashin gamsuwa da kalamansa ta tab'e.
"ban yadda ba saboda dazu kallon da kake mata baiyi kama da babu komai ba, kuma na tabbata ka fara sonta"
Murmushi gefen baki ya saki wanda shi kadau yasan manufarsa, yace "tabbas na kamu da sonta saidai son da nake mata baikai na kasance tare da ita ba, kin dauka zan barta taci bulus ne bayan tamin rashin mutunci "
Nisawa Faiza tayi, aranta batai na"am da koma mai yake niyyan yiba, tunda har ya furta yana sonta ba lailai ne ya rama abunda zaiyi ba
"What are you planning ?
Girziga kai yayi yace "i dont know yet, ina dai tunani gagarinmin abunda zanyi na koya mata hankali, so nake tayi kuka da idanta"
"Daganan kuma saika rabu da ita kenan ? Faiza ta fadi.
Tsaki yaja
"Kinga enough of your questions, you're just a friend banaso ki wuce limit dinki" ya fada, amshe mukulli hannuta yayi ya fada motar yaja ya barta nan tsaye baki sake cike da takaici.

Salma na shiga Gida daki ta wuce ta kwanta, zuciyar ta fal da farin ciki,  tunanin Mujahid take tana tuna farkon haduwa su izuwa yau, kwata kwata takasa gane kanta, shin sonshi take komi, kullum dashi take kwana ta tashi, girgiza kai tayi, sam babu lissafi soyayya aranta, bata tab'a yi

ba saidai na baya data gani sun wahalu daga karshe ma tsana ce ta biyo baya shiyasa take bala'in tsoron fadawa soyayyar wani. Tana son Mujahid amma bazata nuna mai komai ba ayanxu har saida tabbatar he won't break her heart.

****

Tun daga ranar lamari ya canza tsakanin su, soyayya da kulawa sosai Mujahid yake nunawa Salma saida bai fito yace yana sonta ba, har ilah yau bai kuma canza kudurin sa na koya mata hankali ba, ta bangaran Salma kuwa zuciya daya take zaune dashi takan yi mamaki sai kace ba kwanakin baya suke casa juna ba, aranta takanyi tunanin anya kuwa Mujahid baida wani mugun nufin akanta, saurin kawar da tunanin take saboda tsananin yadda yake damuwa da lamarinta.

Daddyn Salma ne tare da Ja'afar a office dinsa. ja'afar yana daya daga cikin lauyoyi da Alhaji Abbas ya aminta saboda tsananin rike gaskia da Tsoron Allah da yake azuciyarsa, sau tari yawan idan zaiyi harkar canji da dollars ko euro yafi yadda da damk'awa jaafar takardun shaidan komai dan yasan bazai cucu saba.
Zaune suka suna magana akan wani fili daya siya a Kaduna, copy na takardu shaida da komai ya mikewa Jaafar, karba yayi yana dubansu
Daddy yace "ka adana su da sauran"
Hade takardun jaafar yayi cikin briefcase nasa sannan ya mike da niyan yimai sallama, dakatar dashi Daddy yayi hade da cewa "ya maganar mu ta kwanaki, naji shuru baka kara waiwayar zancen ba.."
Zama jaafar yayi had'e da kirkiro murmushi dole, shikam yama manta da zancen, shuru yayi yana tunanin zancen da neman amsar bawa Daddy, bazai yaudari zuciyan saba dan kuwa yana son Junaina, saidai kuma ba damuwa tayi dashi ba ga kuma Daddy da yakeson ya hada shi da Diyar shi dako sanin ta bai yiba balle ma yasota, shi kuma auran bayama cikin lissafinsa yanzu kokarin Nemo Ummi kawai yake dan farin cikin hajiyarsu kuma baima isa ya tunkareta da sunan yana son aure ba, ana takai wa yake ta kaya.
Ajiyar zuciya ya sauke yace "Alhaji wani hazari ba gudu ba, maizai hana mu hadu da diyar taka, idan ta amicin dani saina yadda karya zamana ko tana da wanda takeso"
Farin ciki sosai ya lulube Daddy, kasancewar ta bangaran Salma ba matsala koda batason Jaafar yasan zata mai biyayyah, kuma ma baiyi tunanin Salma nada wani da takeso ba.
yace "ba matsala, gobe kazo gidana mu kara tattaunawa saika ganta
Yake jaafar yayi aranshi yace "Allah yasa karta aminci, afili yace "saidai yau nazo, saboda gobe da safe ina da aiki a Kaduna"
"ba damuwa, Allah ya kaimu zuwa dare" acewar Daddy.
Godiya yama Daddy sannan sukai sallama ya fice azama.

Tun ranar da Hajiya ta kira Mujahid tace yazo gida bai samu daman zuwa ba sai rana ta yau acewarsa aiki yamai yawa bacin kuma da gangan yaki zuwa.
Fuska ba yabo ba fallasa Hajiya ta tarbeshi, nan tahau mai fadan barin sa gida akan abunda baikai ya kawo ba, Mujahid kam shuru yayi yana sauraran ta dan ya kagara ta gama ya wuce

aikinsa, tace "Bani hotunan Ummi dana baka kwanakin baya"
Sosa keya yayi alamun marar gaskia yace "mi zaai dasu, an ganta ne ?
Hajiya tace " baa ganta ba, kawai hoton zaka bani tunda ba nemo ta zakayi ba, tuni Jaafar ya dukufa da nemo ta kuma am sure zai samota aduk inda take"
Ware ido Mujahid yayi adan kidime yace "jaafar zaki bawa hoton ?
Mugun kallo takai mai, tace "ko babu hoto Jaafar yasan fuskan ta, kaida ba saninta kayiba yasa na baka hoton"
Gabansa ne ya fadi, fatan shi Allah yasa kar Jaafar ya hadu da Salma, nisawa yayi yace "Hajiya basai jaafar ya nemo taba, nida kaina zan kawota gidan nan very soon."
"Ka ganta ne" Acewar ta.
Kai ya girgiza alamun a'a, aranshi yace "ki bani time very soon zaki ganta amma saina koya mata hankali yadda idan ta shigo gidannan bazata yadda ki had'ata aure da niba".
Tashi yayi ya mata sallman zai wuce office ya fice waje, nan suka hadu da Junaina ta dawo daga gidan wata kawarta dan tuni sun gama Neco.
"Yaya kyan tafiya dawowa" ta fada tana dariya.
Tabe baki yayi yace, "ce maki akayi nadawo"
"Oh Allah, he will never change, ni ina can ina missing dinshi amma koya kula dani" aranta tayi maganar, Afili tace "yaya akwai abunda nakeso kasani, sumtin is going on in this house"
Kallon gefe yayi babu mai dubansu sannan ya jata gefe danjin wana abu ke faruwa, sau tari dama ita ke kaima rohoton abubuwan dake faruwa agidan dan ba zama yake ba.
Murya kasa kasa tace "bansan full story dinba, naji dai Hajiya na Waya da Aunty Bilkisu akan wani abu, i dunno ko kudi ne ko gida ko kuma ince sumtin is missing i dont really know, naji Hajiya tace tunda kai kaki nemo wa idan ya jaafar ya nemo shi zata
bawa ta fasa baka"
Hankalin sane ya tashi danya gane inda Zancen ya dosa, saidai bazai bari Jaafar yaga Salma ba much less ya yadda da auran suba.
Dakewa yayi yace "little sis kinsan mi zakimin"
Kur tayi tana kallon shi, yace "inaso ki sawa Jaafar ido, idan kinji yana waya akan wata mace ko bincike ki bani feedback kinji"
Kai ta girgiza alamun toh, murmushi ya sakar mata. "yauwa my beautiful sister, you know i like you alot"
Dariya tayi tace "nidai yaya kadawo gida plz, wlh i missed you alot".
"Karki damu nakusa dawowa"
Dadi sosai taji, sun jima yana biyeta sai shagwaba take zuba mai daga bisani ya lallab'a ta ta tafi ya koma motarsa yaja yabar gidan.
Tuki yake yana neman mafitan yadda Jaafar bazai hadu da Salma ba, idan yayi sake kuwa yanaji yana gani zaiga Salma a gidansu, dabara ce ta fadowa mai yadau waya hade da dailing no din Salma.

Alokacin kuwa had'e book dinta Salma tayi cikin jakarta sannan tabar dakinta, gurin Mom ta shiga ta mata sallama ta fito cikin sauri, library na skull takesan zuwa karatu saboda jibi ne zasu fara exams.
Kokarin bude motar tayi taga kiransa, murmushi tayi ta dauka.

Daga can Bangaran cikin sweet voice dinshi yace "Angel of my life, son kowa kin wanda ya rasa"
Dariya tayi kasa kasa, tace "ka fara koh, how am i even sure am your angel"
Yace "believe me, ba karya nake ba, idan ma baki yadda ba God knows it.
"Kaga ni library zani, inada exam jibi, kana ina?
Yaji dadi abunda tace, aranshi yace "perfect, nasan abunda zanyi"
Afili yace "ina driving, ki jirani nazo nayi picking dinki saimuje inda babu wanda zai dameki dan kisamu kiyi karatu, nasan ki da tsokana kar kije kiyi dambe da mutane a library" karashe maganar yayi cikin zolaya.
Shagwabe fuska tayi kaman yana ganinta, tace "nifah bani da tsokana, ko dambe ban taba yibaaa.."
"Hmm, kedin, ki jirani am coming" katse call din yayi, ta fita can bakin gate jiran shi, baafi 20 mins ya karaso ta shiga motan ya kama hanyar office dinsa, tagane hanyar, tace "lailai ma office dinka ne bazaa dameni ba?
Wani shumin kallo yayi mata da saida taji shi a kwakwalwar kanta, murya kasa kasa yace "duk wanda ya dameki cikin cell zan wurga shi..
Ware ido tayi adan tsorace, "cikin cell sai kaca a film"
Dariya yayi bai kuma cewa komai ba ganin yadan tadan tsorata, suna isa parking yayi, suka fito suka shiga elevator har zuwa cikin office dinsa, ita batama san akwai elevator ba kasancewar ta stair security yabi da ita kwana kin baya.
Office din babba ne mai shegen kyau can gefe inda Couch da center table yake takarasa ta zauna shi kuma yA karasa gurin table dinsa ya zauna kan kujerar sa hade da fara aikin danna laptop din gabansa, sosai yaci serious da abunda yake batare daya dubi Salma ba.
Itakam abunda take so kenan, bude handout dinta tayi ta dukafa da karatun General studies da suke dashi.
Bayan kaman awanni uku Mubarak ya shigo office din, ganin Salma yasashi dariya, zama yayi gurin mujahid yana zolayar shi murya kasakasa, b'ata rai Mujahid yayi, yafara magana cikin fad'a, duk ahankali suke magana, Salma bataji komai ba kuma bata damu dason jiba, sund'an jima sannan Mubarak ya fice office din.

Gyaran murya yayi, Salma ta dubeshi
Yace "bani labarin samarin ki ?
Dariya tayi
"Banda saurayi, infact ni bana soyayya"
"Miyasa ?
Ajiye pen din hannuta tayi hade da yin tagumi, amaraice tace "Sanadin So Ummata tasha wahalan rayuwa, daga karshe ma Abbana ya rabu da ita da tsowon ciki, bansan lokacin ba, bansan anyi ba amma ayadda naji labari yadda komai ya faru yasa kwata kwata na cire so araina"
Kallon tausayi yayi mata, tunda yake gida bai tabaji labarin Ummanta abakin Hajiya ba, saidai zaiso sani..
Kaman wanda baisan da rasuwan Umman ba yace "ina umman take ?
Kaman zatayi kuka tace "ta rasu, lokacin daban santa ba, i was 3years old tym din".

Maida dubansa Mujahid yayi bisa laptop din yace "bai kamata ki cire so aranki ba, tunda iyayan ki daban ke daban"
"Hmm, am sacred banso ayi breaking heart dina"
Shuru Mujahid yayi baice komai ba, bayason cikata da surutu, bari yayi sai kuma gobe ya kara jeho mata wata tambayar.
Cigaba da karatun Salma tayi, lokaci Sallah azahar nayi ya nuna mata toilet dake office din sannan yafice zuwa masallaci, bayan ya dawo ya tura aka kawo wa salma abincin take away, godiya tayi.

Karfe bakwai Daddy ya dawo Gida, nan ya tsarawa Mom batun zuwan Jaafar, sosai taji dadi da batun daddy dan kuwa ta kagara Salma tayi aure ko zata nutsu, nan daddy ya shaida mata bayan Sallah Isha'i Jaafar zaizo ganin Salma, dadi sosai taji, wayarta tadauka dan kiran Salma.

Bayan Salma ta idar da sallar Magrib, Qur'an dake ajiye a office din tadau ta karanta sannan ta ijeye ta cigaba da karatunta, lokacin Mujahid yafita masallaci bai dawo ba, kirar Mom tagani tayi azaman dauka.
Aladab ce ta gaidata, Mom ta amsa sannan tace "Salma kibar duk abunda kike kidawo gidan yanzu nan, Daddy zai baki wani Surprise"
Farin ciki ne ya kamata, tace "momy miye ne, dan Allah gayamin i cnt wait saina zo"
Dariya momy tayi tace "idan kinason sani kizo maza yanzun nan, kuma kiyi sauri" katse call din Mom tayi, cike da Murna Salma tahau tattare books dinta ajaka, Mujahid ne ya shigo, ganin tana hade komai yace "keda kika ce sai 10 zamu tafi, kin fasa ne ?
"Eh nafasa, kaini Gida" cigaba tayi da hade komai zuciyar ta fal murna.

8.20 Jaafar ya iso gate din Gidan Daddy, bai tab'a zuwa gidan ba yasa yakira Daddy awaya dan tabbar da gidan ne, nan take Daddy ya kira mai gadi aka budewa mai gate ya shigo gidan, cikin palo gidan Daddy yamai iso, ya shiga yagaida Mom aladabce, sosai mom ta yaba da hankalin sa, sun gaisa sosai, mai aiki ta kawo mai na shasha baki, shikam Jaafar gaban sane keta faduwa, har yayi dana sanin kowa kanshi gidan.

Mom kam murmushi kawai take tana saurara isowan Salma....
[9/7, 12:37 AM] Xarah Bukar: Zuma Sai Da Wuta

~na~
©ӽaraђ bųkar
®NWA

43 - 50

Murmusawa Mujahid yayi ganin yadda take cikin walwala. Table dinsa ya k'arasa yadau wayarsa tare da mukulin mota. Ficewa sukayi daga office suka nufi ma'ajiya motar, Salma na tafe tana waya da Mom, cikin sauri tayi gaba ta tsaya bakin motar. Wayar sace tayi ruri, ya duba

yaga Junaina da kuma miss call datai mai wanda bai lura ba sai yanzu, tsaye yayi nan inda yake batare daya karasa inda Salman take ba ya dauka.
"Little sis ya ake ciki ?
Kaman munafuka Junaina tahau duben ko ina a palo gudun kar wani yajita, murya kasa kasa tace "yayA naga ya jafs ya fita, kuma naji yana waya da wani zaije ganin wata yarinya, i dont know wace yarinya ce"
"Yaushe ya fita ?..
"Yadan jima kuma bai cewa Hajiya Komai ba"
"Okay Sis, ki cigaba da samai ido, i'll call you later" katse call din yayi ya karasa motan suka shiga, sai sannan ya tambayi salma dalilin tafiyar ta, bata boye maiba ta fadi mai Mom ke kiranta kuma it urgent.
Shuru Mujahid yayi yana tunani anya ba gidansu Salma yaje ba, wata zuciyar tace it cnt be possible, miye zai kaishi gidan, saidai surprise da Mom zata bawa salma ne ya tsaya mai arai, zuciyar sam bata aminta da hakan ba, kuma baiji yana son tafiyar Salma ayanzuba. Kallonta yayi da gefe ido yaga tana latsar wayarta fuska ta dauke da murmushi..
Murmushi yayi sannan yaja wani wawan burki da saida ta tsorota, afirgice ta kalle shi, gani tayi ya daura kansa bisa steering hannusa dafe kan gefen cikinsa, murkutsutsu yahau yi tamkar wanda zai mutu.
Tsabar gigita bata san sanda takai hanunta bisa bayan saba tanai tambayarsa maike damunsa, kasa magana yayi banda cije labb'a da yake, fita tayi motan ta zagayo gurin sa. Tambayarsa ta kuma tayi, murya ciki ciki yace "am sick, can you drive ?
Kai ta gigiza alamun eh, taimaka mai tayi ya koma dayan sit din sannan ta shiga taja motar. Kaman mai shirin kuka ta kalle shi, "wana asibiti zamu ?
"Kaini gida kawai" ya fada yana lumshe ido, shingidewa yayi akan sit kaman wani marar lapian gaskia.
Hankali tashe tahau driving ba tare data tuna kiran da Mom ke mata ba, suna isowa gidanshi ta taimaka mai suka shiga ciki ayayinda sai faman cemai sannu take, shikam dariya ke cinsa yana gimtsewa. Zaunar dashi tayi kan two sitter sannan ta dube shi, murya cike da tausayi tace "sannu yaya.."
Yi yayi tamkar baiji taba saima rufe ido dayayi, itakam tanason tafiya ga dare yafara lulawa, gyara zama tayi ta fuskan ceshi tanai karemai kallon aranta tanai kara jin sonshi. Sunkai 20mins ahaka kafin nan ya bude ido, suna kallan juna, lumshe ido yayi yace hado min tea nasha magani"
Ba musu ta mike ta shiga kitchen ta hado ta kawo mai, k'insha yayi ya ajiye akan yayimai zafi da yawa, zama tayi tanai jiran tea yayi sanyi tanason tafiya saidai bata iya barin sa cikin larura.

Har kafar Tara su Daddy da jaafar na zauna suna jiran salma, shuru babu labarinta, sau kusan hudu Daddy na kiran wayarta babu respond, ransa ne ya bacci, nan yahau tambayan Mom, cemai tayi skull ta shiga karatu saboda exams da zasu fara, jin shaanin karatu yasanya Daddy yayi calming down, dan yasan lokacin exam Salma bata wasa. shikam Jaafar dadi yaji, amma aransa mamaki yake ace yarinya har yanzu bata dawo ba, jinjina kai yayi "anya ta arziki ce kuwa" azuci yayi maganar.

Hira kadan suka tab"a Daddy yace mai yayi hakuri idan ya dawo daga tafiyar sai yadawo kafin nan diyarshi ta gama exams sai ayi magana, Jaafar kam bai damuba, gaba ta kaishi gobarar titi a Jos, san samu ma kar Daddy ya kuma mai zancen. Sallama yayi masu yabar gida.

Mujahid kuwa shiriritar da Salma yahau yi, bayan tea yayi sanyi k'insha yayi wai zaiyi amai, saida ta kuma had'amai Black tea sannan yadan sha kadan da maganin bayan tasha walaha da lallaba shi sannan ya iya shan pill na magani guda daya, acewarsa daci yayi yawa. Bayan nan kuma ta tashi da niyya tafiya ya langwabe da ciwon kai, saida ta tayi zaman kusan 30 minti tanai mai sannu.. Karshe dai saida yaga 11 tayi sannan ya koma normal, tace mai zata tafi dare yayi, ba kunya yace suje ya kaita gida, itakam mamaki ne ya kamata mutum sai kace mai aljanu, tunani tayi anya ba raina mata wayo yake ba. Haka dai tabishi suka shiga mota, sai janta yake da hira, kasa magana tayi tsananin yadda taganshi garau, wayarta ta duba taga miss calls na Daddy, tsaki tayi aranta tace "Allah yasa banyi ranshi surprise dinnan ba"
Nan baki gate ya sauke ta tamai sallama ta shiga gida, Mom ta tarar zaune palo, dan tuni Daddy ya shiga ya kwanta, ganin Salma yasa hankalinta ya kwanta, fada tayi mata sosai akan dawowan dare amatsayin mace bai kamaceta ba, hakuri Salma ta bata, itadai surprise din takeson sani, tambayar Mom tayi taki fada mata komai sai  ce mata tayi bayan exams zataji komai daga bakin Daddy.

***

Washegari langwabewa Mujahid yayi bayan yayi shirin sa tsaf na fita office, Salma ya kira yace ta taimaka ta kaishi office dan baya jin dadi, bata kowa mai aranta ba dukda dai zuciyar ta na kisyasta mata wani abu, kuma jiya taji dadin karatu a office dinsa. Gidan taje ta dauke sa suka tafi.

Tun ranar abu kaman wasa, kullum Salma na tare da Mujahid iyakacin taje skull tayi exam tadawo ta koma office dinsa ta zauna karatu, ko shopping zataje saidai ta zauna shi yaje yayi mata, sam bayaso ta fita ba tare dashi ba gudun kar yan'uwansa su ganta, balle jaafar da har yanxu neman ta yake.
Har azuciya Mujahid yasan ya kamu da son Salma saidai yayi alwashin rama abunda  tamai dan kuwa bazai barta taci bulus ba, ganin yadda ta dukufa da karatu yasa ya bata lokaci dan gama exams dinta, ita kuwa Salma zuciya daya take zaune dashi, abu daya ke daure mata kai yadda bai furta yana sonta ba alhalin soyayya kuru kuru yake nuna mata, tanason sani mike zuciyarsa game da ita.

Ta b'angaran Junaina bata daina cusa kai gurin mujahid ba, ko tusa akai a gida saita buga ta fadimai, wataran rohoton sumai amfani wataran kuma data fara fadin abunda bai dameshi ba katse wayan yake. Kullum a rokonshin take ya dawo gida.

Yauce ranar da Salma ta gama Exams, tana fitowa Hall tayi kicibis da Faiza zata shiga next hall

supervision, Hararan juna sukayi kowa ya wuce, kowane da abunda yake zak'awa game da junan su aranshi, K'wafa Faiza tayi aranta tace "yar banzan yarinya very soon zai jefar dake". Tuni Salma tabaiwa banza ajiya, kobi takan Faiza bata kuma ba tq fada mota taja zuwa gida, karfe sha biyu ne lokacin, so take tayi wanka ta huta kafin taje gurin Mujahid tamai albishir din gama exams danba sani yayi ba.

Tana isa gida parking tayi ta fito, kokarin kulle motar tayi taji muryan Salim abayanta.
"Yau kuma baki je wajan sa karuwan ci ba ? Fuska babu annuri yayi magana.
Mamakine ya kamata, ta juyo tace "yaya karuwan ci, a ina, yaushe, ?
Mugun kallo yakai mata wanda daga gani asama yake, cikin zafin nama ya riko hannuta da karfin gaske wanda saida tadan tsaki kara, "ni zaki rainawa wayo Salma, gayamin uban mi kikeyi a office dinsa"
Kokarin kwance hannuta tahau yi takasa, bata rai tayi tace "zan kira Daddy idan baka sake niba.."
Mugun dariya yayi yace "tunda shine ke dauramiki gindin kina iskancin da kikaga dama ko, waya sani ma kokin bashi kanki"
Wani mugun girgiza Salma tayi da kalaman sa, cike da tsantsan bacin rai takai mai azababan mari da dayan hannuta, ba shiri ya saki hannuta yanai mata kallon mamaki lokaci guda kuma zuciyar sa ke tafasa, afuce ta nuna shi da yatsa "idan kana iskancin ka yakare akaina karka kuskura kasako min iyaye, banza, dan akuya kawai, kuma kasani i hate you Mujahid nakeso bakai ba wanda baisan ciwon kansa ba"
Dafe Kunci Salim yayi yana huci, tunanin abunda zai mata kawai yake, Harara ta ballamai, wucewa zatayi yasa mata kafa tayi wani mugun faduwa kasa wanwas, adan tsorace ta daga kai ta budeshi, sosai ta tsorata da yanayin, "anya Salim baya da hankali" ta fada aranta.
Nunata yayi da yatsa yace "ni kika mara saboda da wani banza, aikuwa sai kinyi danasani zan nuna maki ni ba wawan da kike tunani bane" juyawa yayi ya tafi, zuciyarsa na tafasa, shi kadai yasan makircin da zai shuka mata gurin Mujahid din da take takaman tanaso da kauna.

Salma kam tsoro ne sosai ya kamata, mikewa tayi kokarin yi ta kasa zabar azabar dataji kafar ta guda nayi, dakyar da azaba ta mike tsaye, kaman tayi ihu dan azaba, awahale ta iya jan dayar kafar ta karasa cikin gida, bata iya shiga gurin mom ba ta wuce dakinta.

Duk akan Idon Salim, yaji dadin yadda yaga ta kasa takawa, koba komai dole ta hakura da zuwa gurin Mujahid, murmurshin Mugunta ya saki afili yace "zaki gane kuran ki .............

Ni xarah nace Toh Fah, Salma duk ke daya, enemies ta ko ina.
Allah ya karemu daga sharin masu shairi.
[9/7, 12:37 AM] Xarah Bukar: Zuma Sai Da Wuta

~na~
©ҳaraɦ bųkar
(Aunty cute)

51

Tsabar rad'adin da k'afar take mata dak'yar ta cillara ta fad'a band'aki tayi wanka ta fito ta kwanta gado, sosai k'afar tayi tsami haka dai ta daure har bacci b'arawo yayi awon gaba da ita.

Mujahid ne zaune office yana danna na'ura mai kwakwalwa dake gabansa, jifa jifa yakan k'yallarawa agogon tsintsiyar hannusa kallo, guntun tsaki yaja ganin k'arfe daya ta gota bata iso ba gashi kuma ya k'agara ya ganta.
Mubarak ne ya shigo office din tare da sallama, amsawa yayi ciki ciki ba tare daya dubesa ba, Dariya Mubarak yayi hade da zama yanai kallon office din tamkar wani sabon bak'on sa, duban Mujahid yayi, cikin zolaya yace "yau matar ka bata zo ba?
Sai sannan Mujahid ya dubeshi, murmushi yayi.
"Zata zo, na tabbata ma tana hanya"
"taku salon soyayyar daban take, wai ma yaushe zaka rama abunda tama ? Mubarak ya fada ba tare daya bar kyalkyalewa da dariya ba.
Nisawa Mujahid yayi, yace" abokina ina cikin yanayin, na rasa mai zan mata kuma ma bazan iya cutar da ita ba, koba komai yar'uwa tace ta jini, na hakura, yanzu so nake na sadata da Hajiya".
Dakatar da dariyan Mubarak yayi, yace "naji dadi ka gano gaskian zuciyanka, Hajiya kuwa sai tafi kowa farin ciki da kai, yaushe zamuje mu kai amaryar mu gidan sirika.." Cike da zolaya Ya karashe maganar, mugun kallo Mujahid yamai yamike ya fice tare kokarin gitmse dariyar data zomai.
Murmushi Mujahid yayi yadau wayarsa dan kiran Hajiya yi mata albishir, dailing nambar zaiyi, Salim ya fadomai cikin office kamar wani mayunwacin zaki.
Ajiye wayar yayi yabishi da kallon waya baka izinin shigo min office, cikin rashin damuwa da kallon dayake mai Salim yaja kujerar dake fuskantar sa ya zauna had'e da dora kafa daya kan daya, sannan cikin karaji yace "Sir ba batun aiki ya kawo ni nan ba."
Ran Mujahid yakai mak'walan baci, shuru yayi yana jiran abunda zaice.
Salim ya cigaba
"Salma tawace, tare ka fara ganin mu, tun kafin ta sanka muke mu'amala, dan Allah karka shiga tsakanin mu, muna matukar son Juna, adalilin ka yau ta zubar da cikana da take dauke dashi"
Mik'ewa Mujahid yayi, fuska daure, afusace yace "tashi ka fita kafin nasa a cilla ka waje"
"Kayi hakuri sir banxo da fad'a ba" mikewa Salim yayi had'e da risinawa sannan ya fice a office din.
Tsaki yaja ya koma ya zauna ranshi na k'una, ko kadan bai yadda da abunda Salim yace ba, yasan kafin su saba da Salma kallon marar kamun kai yake mata yanzu kuwa d'an zaman da yayi da ita ya tabbatar ba abunda yake tunani bane, kuma ma yasan ba yadda zaai Salma ta

kaiwan shashashan yaron nan kanta, tsaki ya kuma ja yace "Salma tafi karfin ka, baka isa ka rainamin hankali ba, wawan banza kawai". Wayarsa ya dauka yahau kiran Salma, sau biyar ya kira tana ruri baaa dauka ba, ajiye wayar yayi zuciyar sa na aiyyana mai abubuwa, saurin kawarwa yayi ya cigaba da aikin gabansa.

Bayan la'asar Salma ta farka bacci da matsananci ciwon kai, dakyar ta yunkuro zaune taji kafar tai mata nauyi, wani irin juwa take ji, sauka tayi kan gadon ta rarrafa zuwa bandaki ta dauro alwala ta fito tayi sallah zaune sannan ta koma gado ta kwanta, daukar wayarta tayi taga kiran shi, da sauri tayi dailing no dinsa.
Kaman jira yake, yayi azaman dauka yace "kina Ina ?
Murya ciki ciki, kaman mai shirin kuka tace "ina gida, tuna dazu nadawo saidai bana jin dadi"
Bata rai yayi.
"Mike damun ki ?
Shuru tayi, tanason cemai kafar ta ke ciwo tana tsoron ya tambayeta sanadi, ga kuma kanta na ciwo, wahalalliyar ajiyar zuciya ta sauke sannan tace "kaina ke ciwo".
So yage ya gasgata zancen Salim, yace "deme kuma ?
Zuciya daya bakinta ya furta "cikina"
Baice komai ba kuma bai jira abunda zata kuma cewa ba ya katse wayar, bata kawo komai aranta ba ta ajiye wayar hade da gyara kwanciyar ta.
Kasa gasgata zance Mujahid yayi, yanaso ya yadda da abunda Salim yace ya kasa, kalllon wayarsa yayi dake rike hannusa jiran ko zata kira shi yaji shuru.. Jiki sanyaye ya ajiye wayar aranshi yana fadin "Tabbas Biri yayi kama da mutum....

Masu korafin basu san ma'anar zuma sai da wuta, bara na maku bayani dalla dalla.

Shi sak'ar zuma baa iya daukan shi saboda Zuma🐝🐝 dake makale jikin sakar, komin yadda zaki ki kori Zuma bazata koru ba tsananin yadda take da taurin kai da kafiya maganin ta daya ce wato Wuta...kinasa mata wuta zata saduda ta gudu tabar sak'arta ba tare da bata lokaci ba.

Shiyasa hausawa sukace Zuma Sai da wuta.

Shin acikin
Mujahid
Salma
Salim
Jaafar
Da
Junaina waye Zuman waye wutan ??

Ina jiran Amsar ku....

[9/7, 12:37 AM] Xarah Bukar: Zuma Sai Da Wuta

~na~
©χaraɧ bųkar
(Aunty Cute)
®NWA

Vote me on Wattpad @Cutexarah

xarahbukar.wordpress.com

52

Da Magrib Mom ta lek'a d'akinta kansacewar taji shigowarta tun rana, ganin bata da niyyah fitowa ya sanya ta bibiyar ta, kwance ta ganta can k'arshe gado akudundune, k'arasa wa gurin tayi tahau tashin ta, bude ido salma tayi, jikinta gabad'aya k'yamar yake tsabar yadda zazzab'i mai zafin gaske ya cafketa, hankali mom ne ya tashi ganin yanayi ta, ba tare da b'ata lokaci ba ta taimaka mata tasa kaya suka fita waje, kiran Salim tayi yaxo yaja su zuwa asibiti, a mota sai faman yi mata sannu yake tamkar ba shine sanadi ba, bata iya amsa shiba har suka isa asibiti aka bata gado.
Koda Mujahid ya koma gida kasa zaune yayi, kalaman Salim ke yawo a kwakwalwan kansa. Kamar wani tab'abb'e yahau girgiza kansa yana fadin it cant be possible, yana son Salma kuma yayi trusting dinta, ba zai tab'a yadda da zance salim ba" wayarsa dake ajiye kan 3 sitter yadau hade da mik'ewa tsaya yayi dailing no din Salma, har kusan sau biyar bata dauka ba, nan take wani mugun haushin ta ya dirar mai, cilla wayar yayi kam kujerar sannan ya zauna kasa hade da dafe kansa. Atakaice dai ranar dakyar ya iya runtsawa, da safe bayan yayi shirin sa na office fita yayi, bai zarce ko ina ba sai gidan su Salma, ya jima yana horn daga bisani mai Gadi ya iske shi ya sanar mai babu kowa agidan sai Salim, hajiya da diyarta kuma suna asibiti, Alhaji dama baya gari.
Komawa Mota Mujahid yayi ran sa bak'in k'irin, zuciyar sa kuwa ta gama gasgatar mai da gaskian lamarin, wani irin haushi kanshi yake ji da tun farko yayi sake har Salma ta shigo mai rayuwa, yana son salma, she's the only gal da yasan he can die for, saidai bazai taba yadda ta raina mai hankali ba much less tayi deceiving dinsa with her cute innocent face, nambarta dake wayar sa yayi deleting hade da kunna motan, kallan gate din gidan yayi yace you're dead to me" afusace yaja motar sa yayi gaba.

"Wai yaushe hakan ta faru bansani ba" acewar Mom, zaune take gefe gadon da Salma ke kwance, kafar mai targade daure da farin gyalle, Yunkurowa Salma tayi ta jingine jikinta a karfan gado, Magana zatayi Salim ya shigo rike da flask da Mom ta aikeshi gida ya dauko, Harara Salma takai mai, yace "sannu sister, ya jikin ?
Atakaice tace "lapia" duban Mom tayi tace "ina tafiya nayi missing steps na fadi"
Mom tace "tsautsayi kenan baya wuce ranar sa, Allah ya tsare gaba, ya ciwon Kan ?

Da sauki" Salma ta amsa,   tashi Mom tayi ta fita gurin Doctor, kusa da ita Salim ya karaso hade da marairece fiska yace "sis am sorry, duk nina jaza maki"
Tabe baki tayi
"Ba komai ya wuce, ni yanzu kawai gida nakeson komawa, nabar wayata kan gado" kaman zatayi kuka ta karashe zance, Mujahid ne aranta,   tana son fadimai tana asibiti karya jita shuru.
Mom ce tadawo dakin tana waya da Daddy ya mike ya fice, mikewa Salma wayan tayi ta amsa yiwa Daddy magana.

K'ashe gari likita ya sallame su, suna isowa gidan wayarta tadau ka taga miss call dinsa, farin ciki ne ya ziyar ceta ganin yadda ya damu da ita, kiran sa tahauyi fuskar ta dauke da murmushi.

Alokacin Mujahid zaune yake office yana danna laptop dake gabansa, fuskar sa babu annuri, shi kadai yasan yadda yake jin zafi azuciyar sa, yana ganin kiran nambarta yaki dauka, har kusan sau goma takira bai dauka ba, karshen ma wulla nambarta yayi a reject list ya cigaba da aikin gabansa yana huci.

Mamaki ne yakama Salma alamun da  wayarta  ya nuna mata nambarta is rejected, zama tayi tana tunanin lapia kuwa, bata saduda ba daddare tahau kokarin kirasan still abu daya yake nuna mata, hankalinta ne ya tashi, duk atunaninta ko wani mugun abune ya faru dashi. Kasa runtsawa tayi har garin Allah ya waye, da safe shiryawa tayi ta shiga motarta taja zuwa office dinsa, tana isa daga main entrance gate din wasu polisawa suka hanata shiga, mamaki ne yakamata dan kuwa sun santa duk zuwanta barinta suke, rokon su tahau yi da magiya, fir suka hanata shiga karshe ma ce mata sukai Ogan su yace karsu barta ta shigo.
   Jiki sabule ta koma gida, kwata kwata batama san miya faru hakan ke faruwa ba, batai kasa a gwiwwaba saida tayi kwana uku tana zuwa basa barinta ta shiga, hankalinta sosai ya tashi, a kwana na hud'un ne ta kuma komawa, tana cikin rokonsu Mujahid ya iso gurin cikin motarsa zai shiga, ajiyar zuciya ta sauke ta nufesa da sauri, saidai mi, ko kallanta bai yiba yakara baiwa motan wuta ya shige ciki yabarta nan tsaye cikin tsananin tashin hankali marar mitsaltuwa, nan take zuciyar ta ya fadi mata somthing is not right, kai komo tahau yi agurin tana tunanin. Horn taji bayanta da azama ta juwa, tagane shi, Mubarak ne da take gani office din mujahid, karasa gurinsa tayi hade da gaidashi, yace "mai kikeyi anan, ki shiga mana".
Kai ta girgiza, tace "Mujahid ya basu order karsu bari na shiga, dan Allah ka taimaka ni, i need to talk to him".
Tausayi sosai tabashi, saidai yasan Mujahid da kafiya koda ya shigar da Salma bazai yadda ta shigar mai office ba tunda har yasa doka a entrance kar abari tashigo, ko miya hadusu kuma, duk axuci yake zancen.
Yace "why not ki hakura da ganinshi ki tafi gida, i dont tink zai kulaki"
Kaman zatayi kuka ta marairace fuska tace "dan Allah ka tamakeni, yaki kulani for d past 4 dayx, i need to talk to him, inason sanin miyasa yake ignoring dina all of a sudden"
Shuru Mubarak yayi yana naiman mafitan yadda hakan zai yuyu, ajiyar zuciya ya sauke yace "kinga abu daya zan iya maki, ki fadi inda kikeso ku hadu, ni kuma na maki alkwarin kawo maki Mujahid"

Nisawa Salma ayi, taji dadin abunda yace, hakan kadai zaisa ta hadu da Mujahid harya saurareta.
Risinawa tayi tace "nagode sosai"
Dariya yayi
"Baki fadi inda zan kawo miki shi ba"
Murmushi tayi tana tunanin peaceful gurin da yakamata su hadu, can ta tuna da plantation garden na Daddy, gurin nada matikar girma, kyau da shaawa uwa uba akwai flawowi da mayan bishiyoyi gwanin shawaa.
Tace "kasan A & M gardens na hanyar Dikkoh ?
Yace "uhhm nasan gurin, can kike so ku hadu".
Cike da farin ciki tace eh, dariya yayi yace ba matsala gobe by 4.30 zaki ganmu"
Godiya sosai tamai sannan ya wuce, motarta taja ta wuce Garden din.
Tana isa Baba nayaro ta iske, mai kula da shuke shuke gurin, gaidashi tayi aladabce ya amsa cike da fara'a, suna shiri sosai da Salma kasancewar yawanci idan damuwa tayi mata yawa gurin take zuwa shan iska.
Gurin da pink da yellow flowers suka fi yawa nan Salma tacemai ya gyara gurin yayi kyau dan tana da bako, so take idan yazo duk wata bakin cikin sa ya yaye, shikam Baba nayaro dariya sosai tabashi yahau zolayan ta yayi sirki.... Sun dan jima suna magana daga bisani Salma tamai sallama ta koma gida..
Salim ta tadda ya fito daga motar sa, da alamun shigowar sa gidan kenan, "Salma daga ina kike da yamma haka ? Ya fada cikin salon kulawa kaman gaske, deep down kuma so yake yasan ina taje dan kwana biyu baya ganin ta a office din Mujahid.
Ganin yadda yake mata kirki kwana biu yasa ta saki fuska tace "ya salim Ogan ka naban Tough tym, kwata kwata nakasa gane kanshi, yanxu baya kulani"
Murmushi yayi wanda shi kadai yasan maanar sa yace "kin manta The boss is always d boss, fadin Sakon ki saina kaimai".
Tabe baki tayi "no need gobe zamu hadu a Garden din Daddy by 4pm suprised visit zamu ma juna.."
Ware ido yayi in shocked, "yasan Garden dinne ?
Dariya tayi, tayi gaba tana fadin "a'a, gobe zai sani" tafiyar ta tayi..
Tsaye Salim yayi zuciyar shi na kuna, aranshi yace "muje zuwa, mahaukaci yahau kura", naushin iska yayi ya wuce part dinsa.

*****
Washe Gari.

*Kaduna*..

Jaafar ne tsaye bakin motar sa bayan su kammala shari'a da sukai tayi kusan kwanakin da suka shud'e a Supreme court. Bude motar yayi ya ajiye tilan takardu dake hannunsa sannan ya shiga motar, yaja komawa Birnin tarayya (Abuja).

*Abuja*

Tun Safe Salma ta birkice kayanta gabayada tanai neman wanda ya dace tasa, karshe dai white jean da pink top ta ajiye gefe sannan tadau Hoton Mujahid wanda tuni ta wulla a trash can kwanakin baya saidai daga baya tacire ta adana shi, daukon hoton tayi tana kalla hade da lumshe ido, daga bisani ta bude pink cluth bag dinta ta ajiye frame din ciki, wanka tayi ta fito ta sannan ta zauna jiran karfe hudu ta cika.

K'asa Zaune Salim yayi a office, duk mintina kallon agogo yake, yana fitowa sallah azahar, joint dinsu na yan shaye shaye yaje, saida yayi tatul sannan yahau kuka yana tunanin yadda zai raba Salma da Mujahid, rasa mafita yayi daga karshe ya yanke shawaran zuwa Garden din Kidnapping dinta kafin su hadu da Mujahid.
Karfe uku da rabi nayi Motar sa ya shiga yaja yanai wani reckless driving har ya isa Garden din, black Face mask daya siya na musamman yadau ya sanyawa fuskar sa sannan ya shiga Garden din cikin sadaf ya boye cikin wata bishiya.
Katon Scissors ne Hannu Baba Nayaro, sai gyaran wasu flowers yake cikin sauri yana duba lokaci kar Salma ta iso ta iske bai gamaba, aiki yake sosai yaji alamun saukar Numfashi daga ina yake, dakatar da aikin yayi yafara takowa gurin yana fadin "waye anan...?
Tsoro ne ya kama Salim, da sauri ya fito yakama wuyan Baba nayaro, yace "sshh kamin shuru karka kuskara kayi ihu"
Kokarin kwace kansa Baba nayaro yahau yi, yakasa, iya karfinsa ya take kafar Salim, da sauri Salim ya sakarmai wuya, Guduwa Baba nayaro zaiyi Salim yayi saurin rikosa hade da kwashe tsoho da mari, nan take fada ya kicibe tsakanin su, sukahau dambe, duka sosai Salim yama baba nayaro, ganin yana kokarin guduwa yasa ya dauki scissors din zuciya daya ya caka mai atsakiya cikinsa, ihu Baba yayi ya fadi kasa bakinsa na ambato kalmar shahada, tsoro da firgice ne yakama Salim ganin yadda jinin Baba ke bulbula, hankali tashe ya cire mask din fuskarsa yahau yiwa Baba sannu, nunasa Baba yayi da yatsa yace dama kaina....,
Tsorata Salim ya kuma yi da sauri ya ruga da gudu yabar gurin cike da tsananin fargaba.

Fuska dauke da seriousness Mubarak ya iske Mujahid, yace "Mjay tashi muje na nunama wani abu"
Dubasan Mujahid yayi kaman bazai kulasaba ganin yadda yaci serious first tym in his life yasa shi cewa "miya faru ?
Mubarak yace "it urgent, plz tashi muje banaso ka cikani da tambaya"
Kaman bazai tashi ba, daga baya kuma ya mike bayan Mubarak ya fice a office, "this is not good" Mujahid yafada aransa, atunanin sa ko batun wani crime ne Mubarak yakeso suje sugani, drawer na table din ya janyo yadau bindigar sa da Handcuffs yasa a ajihunun sannan ya fita, gurin mota ya iske Mubarak, shiga sukayi Mubarak yaja motar.

Hudu na cika Salma ta kammale shirin ta, jakarta da hoton ke ciki ta dauka sannan ta fita palo, dakin Mom ta nufa da sauri tai mata sallama akan zataje shopping sannan ta fito, bata dau motar taba acewarta kar Mujahid yagani bakin garden din yafasa karaso wa ciki, Fita waje tayi ta Tari Taxi ya kaita Garden din.

Tana shiga Garden din wani irin fresh air taji da farin ciki, fatan ta Allah yasa Mujahid yace yana sonta da sai tafi ko wace farin ciki.
Taku daya biyu zuwa uku tayi tafara ganin d'ison jini, bin jini tayi har inda Baba nayaro ke kwance, cike da tashin hankali ta tsugunna gaban sa takiran sunansa, jini sosai ke zuba saman cikinsa, hannu ta tasa ta tari jinin tana ambatan innalillahi wa inna'ilaihi rajun, jijji gashi tahau yi ko motsi baya yi, tuni hannuta da farin wandonta suka kwashi jini, ihu take tana kiran sunan baba.

Parking Mubarak yayi, kallan sa Mujahid yayi yace "wai miye zan gani anan ne, nifa ban ciki da wasan ka na banza.."
"Fito muje" Mubarak ya fadi, fito wa sukayi suka shiga Garden din, suna tafiya Mujahid yaji ihu, kallon Mubarak yayi yace "whats going on ?
Kafin Mubarak yayi magana sukaji wani ihu, atake maza suka rafta da gudu inda ihu ke tasowa.

"Na shiga Uku" Salma ta fada, tanai kokarin cire Scissors din dake makale jikin cikin Baba, kasawa tayi ta mike hade dasa duka hannunta biyu akan scissors din da niyyan cirewa.
"Mi kikeyi anan ?
Muryan Mujahid taji agabanta, sam bata lura da tahowar su da gudu ba, adan tsorace tayi Baya ganin mugun kallon dayake mata, "ba komaii" ta fada cikin inda inda.
Tsayawa gefe Mubarak yayi, Mujahid ya karasa hade da Taba wuyan Baba, babu alamun rai tattare dashi, kallon Salma yayi, cikin karaji da zare ido yace "Uban mi kika yimai ?
Kaman zatayi kuka tahau fadin "nima haka naganshi.."
Mujahid ya gama kulewa, ko daya bai yadda da abunda tace ba, yace "ni zaki rainawa wayo, munafuka, yar daba, karuwa yar iskaaa..."
Katse shi Mubarak yayi da cewa "mjay stop it mana, baka da hankaline kake tunanin karamar yarinya da kashe tsohon mutum haka..".
Kallon banza yama Mubarak sannan ya dube Salma hade da ciro bindigar da handcuffs, nunata yayi da bundigar, fuskar ba annuri yace "you're under arrest ..."
Katse shi tayi da cewa "yaya dan Allah kayi hakuri, wlh bani bace, believe me.."
Tsawa ya bugu mata dasaida yan hanjin ta suka kada yace "shut up, you have the right to remain silent, anything u say can and will be used against you in a court of law..."
Iya kuluwa Mubarak yakai, ganin Mujahid da gaske yake arresting salma zaiyi yasahi, riko hannusa "Mjay, calm down mana, kar kayi using personal issues dinka da aikin ki, we both know ba ita ta kashe shiba".
"Karya kake, am sure itace tayi kisan kuma abunda yasa ka kawo ni nan kenan danna gani da idona"
Kallon Salam Mubarak yayi yamata sign din ta gudu, tagane da sauri ta juya zata gudu, mujahid yace "don't you dare walk out on mee"
Tsayawa tayi chak, kuka takeson yi dan taji dadi takasa, kwata kwata ba mujahid din data sani ne wanan ba saidai she isn't stupid dazata tsaya yayi arresting dinta abanza.
Tana jin yafara taku daya biyu a bayanta tayi sauri afkawa da gudu, Tsayawa Mujahid yayi yana kwalla kiran sunanta, ganin bata da niyyan tsaya wa yasanya shi pulling trigger, daidai kafardar hannuta Bullet din yabi ya karce ta, ihu tayi sosai, wani mugun jiri yafara daukar ta, bazata iya

tsayawa ba ta cigaba da gudu hade da rike gurin wanda tuni jini yafara zuba.

Ko ajikin Mujahid saima kokarin kara kai mata harbe da yake, wani Mugun Mari Mubarak ya tsakar mai, suka haure da Dambe...

Hankali tashe Salma ta fice a garden din, kan titi tayo da gudu tana neman madafa, kasancewar titi high way ce yasanya motoci daidaiku ke wucewa aguje batare da sun lura da ita ba, titin ta kalla da idanuwan da sukayi dishishi, kallon bayanta tayi taji tsoron kar Mujahid ya kamata, da sauri ta ruga tsakiyar titin, kafin takai ga gangarawa kasa wata BmW ta kunno kai, kiris ya rage bai kwashe taba yayi saurin taka burgi, itakam stars tafara gani nan take jira ya kwasheta kasa...
"Subhanallahi" Jaafar ya fada ganin yadda ta zube kasa, ga jini ta ko ina ajikinta, fitowa yayi da sauri ya karasa gurinta, kallonta yayi gabansa ya fadi, "Ummi.."
Ya kira sunanta a akideme, daukarta yayi yana jijjiga, yana kiran sunanta, ahankali ta bude ido ta kalle shi, "Help me..' Ta iya fada, kanta ya fado bisa Kirjinsa alamun babu rai tattare da ita...

Innalilahi wa inna'ilaihi rajun yahau furtawa, Ummi bazaki mutu ba dayardar Ubangiji... Ya kuma fadi, da sauri ya karasa da ita mota yasata abaya sannan ya shiga gaba motan ya zaune hade da cire suit jacket dinsa daya shafi jini ya ajiye gefe sannan yaja motar.....
[9/7, 12:37 AM] Xarah Bukar: Zuma Sai Da Wuta

~na~
©χaraђ bųkar
(Aunty Cute)

Wattpad @Cutexarah
Blog xarahbukar.wordpress.com

53

Saida Mubarak ya tabbatar Salma ta b'ace agurin sannan ya dakatar da fad'an hade da matsa wa gefen yana cewa "May calm down plz, ka saurare abunda zan fad'a ma"
Iya k'ulewa Mujahid yakai, nunasa yayi da bindigar cike da fusace yace "enough of your nonsense, hand over the d damm keys"
"Easy mehh.." Mubarak ya fad'a had'e dayin surrender, key din ya ciro ya wulla mai ya ceb'e.
Fuska ba annuri Mujahid yahau shi da mugun kallo yana cewa "dont you dare interfere, am warning you, stay out of this"
Kai Mubarak ya daga mai, tausayin Salma sosai yakama shi da takaici duk dalilin sa komai tsakanin su yakara tabarb'arewa, yana gani Mujahid ya juya da sauri yabar gurin.

Titi ya nufa bai ganta ba sai jinin daya gani kwace gurin, hannu yasa yaji jinin fresh ya tabbatar ba tayi nisa ba aduk inda take, Wayarsa ya fiddo ya kira duk polisawa dake check point din hanyoyin fita da shiga ya shaida masu lailai susa ido dakyau akan masu wucewa akwai wata

wanted dangerous crimal data gudu kuma suyi making sure sun cafketa, komai na yanayin Salma da kayan jikinta saida ya kwatanta masu yadda zasu ganeta.

Sun Shiga gari, wani mugun Holdup ya tsayar dasu, hankali Jafar ne ya tashi kansancewar garin yad'an soma duhu, sauri kawai yake danya kai Salma asibiti. Wining glass yayi ya leka can gaba ya hango polisawa da sojoji tsaye suna lek'a motocin dake gaba da nashi, gabansa ne ya Fadi, da sauri yadau Jacket dinsa dake gefe ya rufawa Salam dake kwance seat din baya.  Dukda baisan make faruwa ba Addua neman tsira yahau yi.
   Yana isa gurin su Wani Sojo yace yayi kasa da glass din motar kasancewar sa tinted baa ganin make ciki.
"Ba matsala let him go, dan'uwan Oga ne" Wani babban dan Sanda dake gurin ya fada yana duban Jaafar, yasan shi sosai, gaisawa sukayi, police dun ya fadimai abunda ke faruwa, Tsuru Jaafar yayi danya gano bakin zaran. Hannu police din ya daga ma jaafar yaja motar ya wuce. Ajiyar zuciya ya sauke na relief, fasa kaman hanyar asibiti yayi ya wuce gidansu da ita. Da azama yayi parking ya fito yadauki Salma sukayi ciki, babu kowa palo, hajiya na dakinta, Junaina kuma tun safe taje gidan Aunty Bilki zama da yaranta... Sama ya haura da ita zuwa dakinsa ya kwantar da ita bisa godan sannan yahau kai koman yadda zai taimake ta shiba likita ba. Dabarar Kiran Aunty Bilki yayi, wayarsa yadauka ya danna lambarta...

Bayan Mujahid ya koma office, rundundar yan sanda kusan motoci hudu ya hada suka nufi gidan su Salma, tamkar wani wild vampire yake acting shi adole saiya cafko Salma aduk inda ta boye. Mom na zaune Palo tana trying no din Salma jin shuru bata dawo Shopping ba har dare yayi, kiran nambar take tana ringing baa dauka. Mai gadi ne ya kwankwaso ta mike ta bude, ya shaida mata yan sanda ke neman Salma. Hankalinta ne ya tashi ta zaburi mayafi a daki ta fito nan taga abu kaman yakin dunia..
Mujahid na zauna motarsa a gefe yana  bada order, yana ganin Mom yama wani police signal ya karasa gurin ta hade da nuna mata takardar mai dauke da arrest warrant din Salma, salati Mom tayi bata gama rufe baki ba, yan sanda suka rab'a gefenta suka shiga gidan neman Salma, basu ganta ba suka fito waje, Salim ne ya iso gurin adan birkice daga inda ya biya bayan ya gama aika aika, kayan jikinsa na dazu basune jikin saba.
nan yahau tambayarsu meke faruwa, bayani suka mai, yahau ware idanu cike da kid'ima, ko Kallansa Mujahid bai ba balle ma yayi smelling rat, orders ya bawa yan Sanda suka bar gurin bayan ya dakatar da yan sanda shida suyi guarding gidan.

Mom kam kuka tafara yi ta kira Daddy a waya ta shaida mai abunda ke faruwa, Salima ma kuka yafara daya shiga dakinsa, baiyi tunanin haka abubuwa zasu kansance ba.

Aunty Bilki na asibiti tana duba patients, taga ga call din Jaafar, dauka tayi, yahau roka da magiyan taxo ta taimake shi yana cikin matsala, batagane inda zancen ya dosa ba tace bazata samu daman zuwa ba saboda dare yayi gida takeson komawa tabar Yaran, kuka jafar ya fashe dashi yanai cigaba da rokonta, ba yadda ta iya ta fito ta shiga motarta taja zuwa gidan, tana shiga sukayi Kicibis da Hajiya ta fito Palo, gaisawa sukayi tafadi ma hajiya kiran da Jaafar yayi mata, hankalin tashe duk su biyu suka haura sama.

Yana zauna kusa da Salma yana kuka suka shigo,
Tsayawa sukayi bakin kofar.
"miya faru haka.." Aunty Bilki tafada a tsorace ganin jini ta ko ina kan bedsheet..
Kasa bayani Jaafar yayi yace "plz help her, she is dieing..."
Hajiya tace "wace ce ka kawo har daki jina jina haka.."
Murya sarke yace "Ummii umman ce..".
What" Aunty Bilki ta fada, da gudu ita da Hajiya suka karasa bakin gadon.
Salati Hajiya tahau tana tab'a fuska Salma, "miya sameta, ina ka ganta.." Akid'ime hajiya ta jero tambayar.
Aunty Bilki tace bamuga ta zama ba, dauke ta muje asibiti. Nan jaafar yahau masu bayanin yadda komai ya faru kuma zuwa asibiti bazai yuyu ba.
Kowa hankalinsa atashe, Aunty Biilki kuka, jaafar kuka, da sauri tafiddo papper da pen ta rubuta mai abubuwa da zata bukata sannan ta aike shi pharmacy suyo wa, da sauri ya fice, baa fi 30 minti ba yadawo da komai, Aunty bilki tahau gyara ta da treating dinta yadda ya kamata, saukin abun Bullet din bai shiga hannu ba, allurai tai mata sannan ta hada mata da drip.

Hajiya kam tarasa shin kuka zatayi ko farin ciki, dukda tasan Ummin ce saida ta duba kirjinta dan tabbatar da Birthmark dinta wanda kowa adangin su yana dauke dashi, saidai kowa da inda aka mai shaidar, farin ciki sosai tayi bayanta gani, daukar Salma tayi ta maidata dakinta hade da kwantar da ita bayan tai mata sauyin kaya.
Palo suka dawo sukayi cirko cirko cike da jimamin abubuwa, Sallamar Junaina ce ta katse masu shuru, ganin yanayin su tahau tambayan make faruwa, babu wanda ya iya amsata, Aunty Bilki tadau jakar ta tayi waje, Jaafar kuwa mikewa yayi ya haura Sama, Hajiya tace "dare yayi, nikam na shiga" mikewa tayi ta shige daki jikin sanyaya.
Tabe baki Junaina tayi ta wuce dakin ta, aranta tana tunanin miya samesu, Wayarta ta dauka dan kaiwa Mujahid Rahoto, sau kusan shida tana kiran sa baya picking haka dai ta hakura.

Lokacin Mujahid na zaune tsakiyar Palonsa, kansa dafe da hannayansa, yana ganin call din Junaina yaki dauka, kuka sosai yake yana tunanin ina Salma ta shiga, babu inda basu bincika ba, babu ita balle labarin ta, fatan sa Allah yasa ba mutuwa tayi ba, idan har ta mutu rayuwar sa naciki hadari.

****
Har gari Allah ya waye zuwa rana Salma bata motsa ba, da yamma  Auntu Bilki tazo takara mata allura sannan ta tafi. Duk shige da ficen da ake akan idon Junaina, tanason Sanin maike faruwa adakin Hajiya, takawa tayi sadaf ta leka ta hangi Hajiya zaune tana jan carbi, Jaafar zauna gefe gado iya abunda ta hanga takoma palo ta zauna.
Kallon Salam jaafar yake cike da tausayinta, fuskarta fayau kaman ka kirata ta amsa, Hannuta ya riko hade da daurawa bisa fukarsa yanai shakar dumi da kamshin hannuta, idonsa sa cike da kwalla, hannusa yakai kan kyakyawan fuskarta yanai shafawa, aransa yace "i'll protect you, til my last breath" baisan maganar ta fito fili ba, Hajiya na jinsa ta mike ta fice daga dakin..
Junai tagani palo bata iya ce mata  komai ta wuce kitchen.
Kaman wasa jaafar yaji ta rike mai Hannu da hannuta dayake rike dashi, kura mata ido yayi

yaga babu alamun motsi fuskan ta, da sauri ya mike, wayarsa yahau neman dan kira Aunty Bilki, bai ganta ba, ya tuna ya barta a daki, da sauri ya fito dakin Hajiya ya haura sama. Mikewa Junaina tayi, da gudu ta shiga dakin kafin ya dawo, wata tagani kwance kan gano, karasawa tayi hade da kare mata kallo, tsaf tagane Salma ce data sace ta, "kutumar Uba, yar iskan nan ce a gidan nan" ta fada da karfin gaske, saurin kama bakin ta tayi hade da ficewa daga dakin, dakinta ta koma tahau lalubar Nambar Mujahid awayanta, sai cewa take "tab, wlh bazai yuyuba"
Dailing no din tayi.

Mujahid na zaune office da wusu yan sanda suna bashi feedback akan nemo Salma basu ganta ba, zaginsu yahau akan basu iya aikin su ba, ganin call din Junai yasashi Jan dogon tsaki, "yarinyar nan saina ji ubanta zata kyalleni" ya fada, dauka call din yayi da niyya zazzaga masifa,
"Yaya kasan wana gani adakin Hajiya, yar daban nan data sace ni kwanaki..."..
Azabure ya mike tsaya, "Uwar mi takeyi adakin Hajiyar, how comes taje Gidan...?
"Yaya nima ban sani ba, kaman dai bata da lapia, naga su hajiya sunyi jugum sai kace wata yar uwarsu.."
Katse call din yayi bai tsaya sauraran surutun taba, kallan yan sanda yayi yace ku hada motoci goma da ambulance daya kuje inda zan baku address ku daukon min ita"
Address din gidan yabasu, ya kuma cewa suje yanxu batare da bata lokaci ba yana biye dasu abaya.

Tsaki Junaina taja, tayi kwanciyar ta aranta sai tsinewa Salma take, Jaafar na daukan Wayarsa Dakin Hajiya ya koma, nan ya iske Salma na jijiga tana aman wani bakin jinin, idanuwan ta rufe, tsorata yayi ya kira Aunty Biliki ya shaida mata..
Akidmi tace "jaafar ka kawo ta asibiti, she need blood, idan ba hakaba zata iya mutuwa saboda tayi loosing alot of blood".
"Aunty yan sanda zasu iya kamamu, bakiga duk asibiti ansa securities neman taba"..
Aunty B tace "kazo da ita, zan san dabarar da zamuyi mu shigar da ita."
Hankali tashe Jaafar ya kashe Wayan, Hajiya ce ta shigo dakin, fadamata  yadda sukayi yayi. Tace "dauketa muje mota bamuga ta zama ba" da sauri ya dauki salma suka fice, haraban gidan suka fita suka ga an wangale gate, motar yan sanda mai siren suka gani suna shigowa tare da ambulance.

Cirko cirko Su hajiya sukayi suna kallon Yan sandan da already sun fito, daya daga cikin su ya nuna yace fito da gadon, ba masu aka bude ambulance aka fito da gado, inda Jafar ke rike da Salma suka nufa da niyyan karban ta, hade rai yayi hade da ja dabaya, Hajiya kuwa tsoro ne yaka mata, tahau rokonsu Allah da Annabi, ko ajikinsu, ganin Jaafar sai bata basu lokaci yasa suka nunasa da bindinga, ko gezau bashi da niyyan sakin Salma.
Gefe Oga gurin yayi ya kira Mujahid ya fadamai abunda ake ciki. Daga  can karshe layin Gidan Mujahid ke zaune a motarsa yana jiran fitowar su.
Cikin fada yace "you guys are dumb, i dont care koma uban miye zakuyi agidan nidai kawai i want her out of that house dead or alive"..

"Yes sir" dan sandan yace hade da katse wayan...
Kallon sauran yayi yace, ku kwato ta da karfi da yaji...
"A"a hajiya ta fada akidime, mi yayi zafi haka kukeson karasar da ita da ranta, kaga Mujahid basu ita tunda ga ambulance samun lafiyar ta shi yafi komai yanxu. Dakyar da rokon Hajiya jaafar yabar Salma suka daurata gadon suka ja suka bar gidan.
Hajiya kaman zatayi kuka tace "jaafar ya akai suka san tana gidan nan, ina Mujahid kirashi awaya..."
Ran Jaafar ya baci ba kadan ba, sai yanxu ma ya tuna da Mujahid Police ne, magana zaiyi yaga Junaina ta fito tana kyalkyalewa da dariya.
Afusace ya karasa hade da damko wuyar ta, yace "mai kika cewa Mujahid..
Ware ido tayi atsorace, tace babu"
Yace "kin dauka bansan kina min bincike kina kaimai rahoto ba, ki gayamin abunda kika fadamai kafin nagama dake.."
Hajiya ce tayi saurin shiga tsakanin su, "miye haka jaafar, zaka kashe tane.."
"Hajiya ki tambaye ta kiji, bakin su daya da Mujahid, how comes suka san Ummi na gidan nan..".
Kallon ta Hajiya tayi tana cira amsa daga gareta.
Gunguni Junaina tahau yi tace "nifa bansan meke faruwa ba, kawai na kira ya Mujahid na fadimai yarinyar data sace ce ita"
Hannu Jaafar ya daura akai yace "ya salam, amma kin zalince ta, baki ga condition da take cika.."
"Inna ruwana" junaina tafada, wani mugun Mari Hajiya takai mata had'e da nunata da yatsa tace "son zuciya kikayi ko adalci, idan har wani abu ya samu Ummi ki tabbata gidan ubanki zaki koma.." Fuuu hajiya tayi gaba ta koma ciki.
Ihu Junaina tayi tace "na shiga uku, badai Abbana dabaya kaunata ba, wace ce Ummi ? Ta tambayi Jaafar dake tsaye, banza da ita yayi ya shiga motar sa yaja yabar Gidan.

Direct central Hospital suka wuce da Salma aka bata gado, da sauri Mujahid ya karaso gurin ganin Doctor ya fito daga dakin.
Doctor yace "tana bukatar jini, saidai bamu da type dinta, nan da 30min xaa kawo ledar type dinta"
Ahasale Mujahid yace "Kaga Doc bana son wasting tym, muje adibi nawa asamata"
Doc yace "ba matsala, inda jinin ku yazo daya muje a diba"
Da sauri suka shiga lab akayi yan aune aune jini yaxo daya aka diba sannan aka karawa Salma, bayan Doctor ya fito daga dakin yace da Mujahid suna sa ran farfadowar ta nan da awanni takwas.
Farin ciki sosai Mujahid yayi ya k"usa kai cikin dakin, kusa da ita ya tsaya yana kalon yadda ta rame farat daya, sonta sosai ke ratsa mai zuciyar saurin kawar da sonta yayi a zuciyar sa sannan ya cire handcuffs a aljihun sa ya sak'ala hannuta daya da karfan gadon, fuska ba annuri yakai hannun sa kan fuskar ta yana shafawa yace "bazaki mutu ba, bazaki gudu ba sai kin gane kuran ki......
[9/7, 12:37 AM] Xarah Bukar: Zuma Sai Da Wuta

~na~
©χaraђ bųkar
(Aunty Cute)

54

Yafi minti goma tsaye kanta yana taunting dinta da mugayan kalamansa marasa dad'i sannan ya zura mukullin cuffs din a aljihu ya fito daga dakin, fuska daure ya dubi yan sanda uku dake gurin sannan ya gargad'esu da karsu bar kowa shiga dakin idan ba Doctor ba.

Parking Jafar yayi a haraban asibitin bacin ya gano dakyar nan gurin ambulance din ya kawo Salma, duba girman asibitin yahau yi yana tunanin ta inda zai fara bi, juyawa yayi ya hangi Mujahid tafe daga can nesa dashi, da azama ya nufesa, Mujahid na ganinsa yakara shan kara shan mur.
Ajiyar zuciya Jafar ya sauke ya tsaya gabansa cike da tashin hankali yace "thanks Goodness you're here, kasan cewa Ummi ce yarinyar daka aika mutanan ka har gida dauko ta ?"
Cikin rashin nuna damuwa Mujahid yamai kallon banxmza yace "is dat y you're freaking out ?
Kallon rashin fahimta Jafar yamai yace "kana sane kenan ?
Tsaki Mujahid yaja, baice komai ba yayi gaba abunshi, mamaki ne ya kama jafar, ba tantama Mujahid yasan Ummi ce saidai bai san dalilin dayasa yake kokarin hunting dinta down ba, koma miye zaiso sani daga bakin Ummi, duk azuci yake magana  Hanyar daya hangi yan sadan tsaye ya tabbatar nan Ummi take.
Karasawa gurin yayi suka ki bari ya shiga, haka ya hakura komawa gida saboda dare yayi.

General clinic inda aka mik'a gawar Baba nayaro nan Mujahid yanufa, police dayabar incharge din dauko gawar ya iske tare da wasu mutane zaune suna Kuka.
Yace "suwaye wannan ?
Police din yace "family din deceased dinne nayi contacting, kai suke jira tun dazu"
Kafin yayi magana daya daga masu kuka yace "dan Allah ka taimaka ka bamu Babanmu, mu mikashi gidan gaskia, bamu damu dasai an dauki mataki ga wanda ya kashe shi ba, wlh mun yafe" kuka sosai saurayin yake, daga gani ba masu hannu da shuni bane.
Tausayin su Mujahid yayi, yace yana zuwa, so yake ya amshi evidence mai karfi dazaiyi preventing Salma zuwa prison. Idan har ya karba ya boye sai randa yaga dama zai fito dashi ya ceceta.
Gurin Doctor ya shiga suka gaisa sannan yace.
"Ka gama autopsy (dissection da akeyi dan gano possible cause of sum1s death)
Doctor yace " komai anyi, zuwa gobe result will be ready.
Kwantar da Murya Mujahid yayi yace "make sure karka nunawa kowa, zan zo dakaina na karba"
Doctor bai kawo komai aranshi ba ya amsa bai da toh, fitowa mujahid yayi ya fadima mutanan cewa zasu iya tafiya da gawan, sukam kuka kawai suke.

Hankali tashe Daddy ya dawo Gidan, nan Mom ta labarta mai abunda ke faru, kuka sosai take

babu labarin Salma, ran Daddy sosai yabaci ya kira Salim awaya, kaman wani majinyaci ya fado palon, duk ya fita hayyanci tsabar gulity conscious dake damu shi.
Cikin tsawa Daddy yace
" dan uwarka ina ka kaimin Salma?
Tsuru Salim yayi ji yake kaman asirin shi zai tono, yace "wlh Daddy nima neman ta nake.
"Karya kake, duk wani rashin jin Salma tare kuke yi ka dauka ban sani ba, dan haka gayamin gaskia awana dalilin ake tuhumarta da kisan mutum ?
Shuru Salim yayi baice koma ba, Daddy ya cigaba "asararrar banza tashi ka bani waje, kuma ka binciko min duk inda Salma take".
Jiki ba kwari ya mike ya fice.
Mom tace "wayarta na ringing baa dauka"
Bara na gwada atawa, Daddy ya fada hade da dailling no dinta.

Jafar na Isa gidan yayi parking, fitowa zaiyi yaji ringing din waya, dubawa yayi ya hango Pink Jakar Salma, dauka yayi ya bude yaci karo da frame mai dauke da Hoton Mujahid, kallon hoton yayi cike da mamaki, nanya tabbatar sunsa Juna, "toh make faruwa ? Ya tambayi kansa, wayarsa ya duba yaga miss call Mom hamsin saina Dad guda biyar, ajiye jakar yayi cikin motar sannan ya karasa gidan rike da wayan, dakin Hajiya ya shiga ya iske ta zaune tayi tagumi, fada mata yayi yadda sukayi da Mujahid hade da nuna mata wayan ummi da iyayanta kerlta kira, ranta sosai ya kara baci da kuma tsoro daya kamata da ganin Dad naciga da kiran Salma. Kallon namban jafar yayi kaman yaso yagane nambar, wayarsa ya danna yayi compare din nambar Dad dake kira, gabansa ne ya fadi, ya kalli Hajiya yace nasan Gidan da Ummi take, tace ai zuwa zamuyi bamuga ta zama ba, tashi tayi da sauri ta zuri hijab sukai waje.

Hankali tashe Daddy ya kira no din abokinsa head of police gabadaya, sun jima suna magana daga karshe ya yanke gobe zaiso office suyi magana.
Baa fi mintin uku ba maigadi ya kwankwaso wai sunyi baki, izini yamai dasu shigo, Su Hajiya na shiga Daddy yaga Jafar, Hajiya kam kallon Mom take wanda tasha kuka harta gaji.
Zama sukayi aka gaisa, Daddy yace "jaafar yanxu nake shirin kiran ka awaya"
Ajiya zuciya ya sauke ya mikawa Daddy wayan Salma, karba yayi, ya labarta masu haduwa su da Salma da kuma yanxu asibitin da take. Salati Mom tahau yi hade da fashewa da sabon kuka, Hajiya kam binta kawai tayi da ido, Daddy yace "amma officer in charge of this case sai yaci uwarsa, saiya fadamin yaushe yaga yata ta kashe wani dahar zaiyi babak'eran aresting one n only daughter na"
Katse shi Mom tayi da cewa, "Alhaji tashi zakayi muje mu dibo yarta."..
Jaafar yace "baa bari, saidai gobe.."
Sai sannan Mom ta dubi Hajiya dakyau sun danyi yanayi da Salma, sharewa tayi tace "mungode sosai da temakon yarmu da kukayi, Allah ya saka da alheri"
Ajiyar zuciya Hajiya ta sauke tace "nice da gode maku, Allah kadai yasan dami xai saka maku"
Kallon rashin fahimta Mom tayi mata, hajiya taci gaba "basan ya akayi Salma ta dawo hannunku ba, saidai kun cancanci riketa yadda naga duk kun damu" k'walla hajiya ta share tacigaba "ni yayar mahaifiya salma ce, na jima ina neman ta banganta ba"
Ware ido Mom tayi, shikam Dad baiyi mamaki ba, koda ya hadu da Salma daman neman

yan'uwanta taxoyi a garin Abuja, ganinta karama lokacin yasanya ya kawo ta gida yarike ta tamkar yar cikinsa, saidai yaji dadi ganin Jaafar amatsayin d'an Hajiya, hada aura salam da Jafar yazo asauki kenan.
Kuka Mom take sosai tana rokan Hajiya karta rabata da Salma, Hajiyan ma kuka take tace "karki damu Salma takuce halak malak bazan rabaku da ita ba"
Dddy yace "ikon Allah kenan, jaafar Allah yayi bazaku hadu da Salma ba tun shekarun baya dana ma zancen auran diyata, ashe kai dan'uwan ta nema, faduwa yazo daidai da zama".
Sosa keya jaafar yayi hade dayin murnushi..
Hajiya kam jikinta ne yayi sanyi jin Daddy zai ruguza mata plans, saidai ba yadda ta iya tunda shiya rike Salma, bata isa tace Mujahid ta kamawa Salma ba, balle yadda taga Daddy yadau zafi da officer dake kokarin aika salma gidan yari....
Sun dan jima suna magana, daga bisani su Hajiya suka bar gidan bayan sunyi zasu hadu gobe a asibiti.

****

Washe gari bayan Mujahid yayi Sallar asubah asibitin ya nufa gurin Salma danso yake ta farka agaban idonsa.
Salma kam Baccinta take, wata nurse ta shigo dakin tacire roban jini sannan ta sa mata na ruwa, fita nurse din tayi, baiyi awa daya ba Salma ta fara motsi, ahankali ta bude, ganinta cikin farin daki yasata mikewa azabure, wani kara tasaki jin ta karce hannuta, duban gurin tayi taga haunta da karfen gadon makale da handcuff, kokarin cixgewa tayi ta kasa, "na shigu uku" ta fada bayan ta tuna abunda ya faru"
kuka ta soma yi, jin motsin xaa shigo yasata tsayar da kukan hade da kafawa kofar ido. Mujahid ne ya shigo, jikinsa sanye da dagon jallabiya, tana ganinshi ta hade hade rai, tuna neman kasheta da yasoyi tayi.
Murmushi yayi mai dauke da ma'ana iri iri sanna ya karasa daf da ita ya tsaya, murya ciki ciki yace "ya jikin ki ?
Banxa tayi dashi
Yace "hope you're ready to spend 30 years a gidan yari"
Dogon Tsaki taja, tace"am ready, then after 30 years kuma i'll come back to destroy you for good".
Dariyan rainin hankali yayi yace "kina da guts dayawa" gashin kanta ya damko, saida tayi kara, daure fuska yayi yace "dan uwarki ni kike yiwa tsaki.."
Dukda ciwon da jikinta yake mai hanata kokarin cizge hannusa daka kanta ba, kaman mai shirin yi kuka tace "idan banyi tsaki ba mai kakeso nayi, apologise or beg your pardon kake so nayi, toh kasani, that will never happen, badai so kake ka kaini prison ba, bismillah, kuma point of correction uwarka badai uwata ba..."
Iya k'ulewa Mujahid ya kai, wuyanta ya damko da karfin gaske, yace " uwata kike zagi.."
Tace "uwa batafi uwa ba, idan kana nonsense dinka dont ever include my Mom."
Sakinta yayi yana Huci, juyawa yayi zai fita tace "am hungry, get me sumtin to eat".
Bai iya tanka taba ya fice zuciyarsa na zafi, baiso reaction din Salma haka ba, yaso ace kuka zatayi ta rokoshi amma dan karfin hali irin nata ba ita tayi kisan ba but she is willing to serve 30 year a prison... Tsaki yaja yana tunanin yadda zaisa a azabtar da ita a prison. Motar sa ya shiga

ya koma gida dan shiryawa zuwa office.

Sai da gari yayi haske Mom da Daddy suka shirya fita asibiti gurin Salma, har sun shiga mota yan'uwan Baba nayaro suka kira Daddy suka fadimai rasuwar, hankalinsa sosai ya tashi fasa zuwa asibitin yayi ya nufi Gidan taaziya, Mom kam asibiti ta wuto nan ta iske Hajiya da Jafar na jiranta a haraban gurin, shiga sukayi wards din, sukayi saan police daya ke gurin wanda ya iso da safe baisan da order din Mujahid ba yabar Jaafar ya shiga, Mom da Hajiya sun tsaya suna magana awaje.

Bacci Salma take ya karasa ya zauna kusa da ita, kallonta yake cike da so da kauna, shafan pretty face dinta yayi har zuwa kan lips dinta yana admiring dinta, dan motsawa tayi yayi sauri cire hannusa, bude ido tayi ahankalin ta dubesa, atunaninta Mujahid ne, tace "ina abinci ? Can kasan makoshinta tayi maganar.
Murmushi yayi yace "yanxu xaa kawo, how are you feeling ?
Sai sannan tagane ba Mujahid bane, yunkurowa zaune tayi kokarin yi, yayi sauri temaka mata.
Kallan shi tayi ayayinda shima kallon ta yake, murya kasa kasa tace "thank you"
"For what" ya fada hade da rike hannuta mai sakale da handcuff, haushi ne sosai yakama shi yasan aikin Mujahid ne.
Murmushi tayi, jikin sanyi voice tace "kaman nasanka wani wuri kafin ranar da kayi saving dina?
Dariya yayi wanda ya kara fiddo kyau shi,
aranta tace "so cute dashi, ba kaman banzan nan ba kullum fuska daure"
Magana zaiyi Mom ta shigo dakin, Hajiya abayanta, da sauri Mom ta karasa gurin Jafar ya mike tsaye ya matsa gefe, kuka Salma ta fashe dashi ganin Mom, nan take ta susuce tahau rarrashi, dakyar Salma tayi shuru tace "Mom yunwa nakeji, kuma acire min wannan abun" turo baki tayi tanai mata nuni da cuffs din hannuta.
"Mun shige su" Mom ta fada cike da mamaki, kallon Hajiya tayi tace "amma babu azzalimi kaman Officer nan, ji mugunta dan Allah.."
Sai sannan Salma ta lura da Hajiya dake kallon su jiki sanyaye, shuru Hajiya tayi sanin cewa d'anta ne azzalimun da Mom ta ambata.
Maida dubanta Salma tayi ga Mom, murya kasa kasa tace "Mom matar nan kaman Hajiyar Ummata"
"Itace, tare da d'anta daya taimake ki" nuna jaafar Mom tayi,
Farin ciki ne ya mamaye Salma, duk sai taji Jafar ya kara kwanta mata, ashe dai jinin tane shiyasa ya ceceta.
"Hajiya.." Salma ta fada tana kallon Hajiya, murmushi hajiya tayi ta mike ta karasa gareta tana fadin "aina dauka bazaki gane niba" rugume juna sukayi, Salma na kukan farin ciki.

Daddy na zuwa gidan Baba nayaro taaziya yayi masu, bai samu janaizar saba, abun tausayi dayaji sanadin Mutuwarsa, tashin hankali biyu ne suka hade mai, jiki babu kwari ya wuce NPF (HQ) gurin head of police, sir Ahmad.
Kara tattauna abunda ke faruwa sukayi, Sir Ahmad yace tabbas yasan da case din saidai baisan diyar shice major suspect ba, atake ya tura department dinsu Mujahid kiran sa, baa same shiba ya aika a kira mai Mubarak sanin cewa su biyu ne witness aranar da abun yafaru.

Mubarak na zuwa, Sir Ahmad yahau shi da tambayo yi, bai boye komai ba ya zayyane masu labarin salma da mujahid tun farkon haduwar su har zuwa ranar da abunda ya faru, ya kuma jajjada wa sir Ahmad lailai Mujahid baya cikin hankalin sa, So da kiyyaya sun rufe mai ido.
Zufa Daddy yahau yi, gano cewa duk case dun revovle around Baba nayaro, "amma yaron nan ya cika dan iska, yan'uwan marigayi basu pressing charges ba saikai dan kawai wata manufarka daban zaka tsangwama d'iyata" azuci Daddy yayi maganan.
Sir Ahmad yace "zaancen banza kenan, wato personal feeling dinsa yake hadawa da aikinsa dan cimma burinsa, dan bashi da kunya kuma harda aika gawa asibiti ayi autopsy alhalin yasa ko kyankyaso yarinya bata iya kashewa"
"Kaga Mubarak, nemi wani ya amso mana autopsy din mugani"
Ba musu Mubarak ya mike ya fice, police din daya kai gawar asibiti ya tura ya amso, Doctor kam zuciya daya yabada atunaninsa Mujahid ne ya aiko.

Mujahid na Tuki ya dunga ganin call daga office, asibiti zaije amsan autopsy ya fasa ya wuce Office, yana isa aka sanar mai Sir Ahmad na kiran shi, hankali kwance ya shiga office din, wani mugun Harara Daddy yakai mai, shan jinin jikinsa yayi ya dake ya karasa gurin Sir Ahmad.
Sir Ahmad yace "yanxu M. Abdulsalam ka kyauta da abunda kayi, kaida kake daya daga cikin wanda suka san aikinsu, miyasa kakeso yin injustice ?
Kallon bangane ba Mujahid yamai, police ne ya shigo da autopsy result ya mikawa Sir Ahmad, Mujahid kaman yayi ihu.
Budewa Sir Ahmad yayi ya karanta sanna ya dubesa yace "the deceased was beating with severe blows before stab to death, yanxu gayamin ita buduwarta ka da kakejin haushi itace tamai dukan kafin ta kashe shi ko kuwa she is stupid dazata kashe shi kuma ta tsaya yimai kuka ba tare data gudu ba"
Shuru Mujahid yayi yana kallom Mubarak da wutsiyan ido, sarai yasan shiya tona komai..
Sir Ahmad yace "ka godewa Allah Mahaifin yarinya baiyi pressing charges akan attempting kashe diyar sa dakayi ba, daga yanxu nayi closing case dinnan, kai kuna you're suspended till further notice".
Mugun Kallon Mujahid yakaiwa Sir Ahmad, afusace ya ciro bage, Id da bingidar ya zubarsu kan table dinsa, hade da ficewa afusace yanai huci, mikewa Mubarak yayi yabi bayansa..
Daddy yace "hukuncin yayi tsauri da yawa.
Sir Ahmad yace "Barni dashi, so nake yagano bambancin sentimental feelings dinsa da aikinsa".

Mubarak na kwalla mai kira ko kallan sa baiyi ba,
Ya shige motarsa yaja afusace, gurin abinci ya nufa ya siya take away sannan yaja zuwa asibiti gurin Salma..
Tundaga nesa ya hangi babu police gurin, haushi ne yakamasa, yana shiga dakin mutanan daya gani yasa shi daskarewa gurin, Hajiya da Mom zaune gefe suna hira, Jafar zaune kusa da Salma yana bata tea abakin tana zuba mai shagwaban ta koshi, sai wani lallabata yake.
"Kai kuma fah, daga ina ? Mom tafada fuska ba annuri ganinsa sanyen da kayan yan sanda. Afusace Hajiya ta mike ta kwashe shi da marin da saidai Salma ta saki ihu tsabar razana.

Bai damu da marin ba banda jafar dayake watsawa mugun kallo.
"Dan ubanka bani mukullin Handcuffs din.." Hajiya ta fada cikin karaji.
Karamin mukullin ya mikata ta amsa ta jefawa jafar ya cabe yayi sauri bude handcuffs din, mikewa yayi yabawa hajiya, "ungo tsiyar ka, kuma ka fice anan" hajiya ta fadi hade dajan haunnsa ta dunkule mai Handcuffs din ciki, Mujahid baice komai ba yayi kokarin ajiye abincin, tsawa Hajiya tamai tace ya wuce da abinci baa bukata, zuciyarsa na tafasa ya juya ya fice.

Mom tace "dan banxan yaro, waishi police, kinyi maganin shege"
Mugun Kallo Salma takai mata ba tare data lura ba, aranta adduaa take Allah yasa Mujahid ba d'an Hajiya bane, idan kuwa hakan ya tabbata she won't forgive him da boyemata shi dan uwan tane da yayi.

Mujahid na Fitowa ya Hadu da Daddy zai wuce ciki, kawar dakai yayi gefe ya wuce ranshi na kuna.
Dariya Daddy yayi yace "kaji da rashin aikin ka, Salma kuwa tama nisa".

Wayyo su oooo anyi 2 zero 😂
[9/7, 12:37 AM] Xarah Bukar: Zuma Sai Da Wuta

~na~
©χaraђ bųkaɾ
(Aunty Cute)

55

Daddy na shiga d'akin yayi farin cikin ganin Salma ta warware, nan ya basu albishiri din yadda komai ta kasance. Mom kam tafi farin cikin rashin aikin mujahid sai d'ura mai zagin Allah tsine take. Hajiya kuwa murmushin dole kawai take, tana mamakin karfin hali irin na Mom, kodayake Salma diyar tace duk abunda tace daidai ne. Salma kam tagama gano komai da Reaction din Hajiya sai fama yiwa Mom ido take akan tayi shuru bata sanma tana yiba. Aunty Bilki ma tazo dubata, sun dade asibiti kafin daga bisa suka koma gida.

Kwana su Salma biyu a asibiti Likita ya sallame su. Gidan Mom suka wuce wanda ba hakan Hajiya taso ba. Bayan kwana biyu kuwa Daddy dakan sa yacema Salma ta shirya Jafar ya kaita gurin Hajiya tayi mata kwana biu, dadi sosai taji dama ta jima dason tambayarsa zataje sai Allah yasa ya furta mata hakan.
Ranar da zasu Jafar na waje parking lot yana jiranta, ita kuma tana tare da Mom a palo suna Sallama, mik'e mata wayarta Mom tayi tace

"Saura idan kinje ki manta dani"
"Haba Mom taya zamanta dake, kece fah uwa ta" ashagwabe tayi magana.
Kunnan ta Mom tajA, cikin zolaya tace "banda rashin ji, kinga Allah ya kawo maki mijin mai kirki karna kuskura naji kinma Jafar rashin Mutuncin, nasan halin ki"
Dan k'ara Salma tayi hade da cizge ruk'on da Mom tayi mata, dariya tayi sannan tace "kai Mom ina laifin wanda ya taimake ka cikin tsaka mai wuya"
Dariya sukayi atare sannan sukayi sallama, har bakin Motar Mom tarakata tanai kara mata fada, motar zata shiga ta hangi Salim bakin window dakinsa yana kallonta, dauke kai tayi tana mamaki yadda yake acting crazy kwana biyun nan. Saida Mom taga sunja sannan ta koma ciki.

Shuru sukayi kowa da abunda yake sak'awa aransa, satan kallon ta Jaafar yayi yaga tana juya wayar dake hannunta, da alamun kuma tunanin take ganin bata cikin hayyacin ta. Cikin cool voice yace "tunanin mi kenan, ko har yanzu jikin ne ?
Sai sannan ta dawo daga duniyar tunanin inda jakar ta da hoton Mujahid suke, tasan dai tare suke da wayarta cikin jakar amma Wayar kadai Mom ta bata ba jakar.
Murmushin ta saki hade da dubansa, tace "everytime i close my eye kai nake gani, kana da kirki sosai"
"Uhmm are you sure, ba wani can daban kike gani ba.." Cikin zolaya ya karashe zancen.
Dariya tayi bata ce komai ba, banda murmusawa da take.

Gabadaya duniyar tama Mujahid zafi, ba aikin fari balle na baki duk zaman kadai ce ya ishe ba, tun ranar dama bai kuma bi takan Salma ba, mugun haushi da tsanarta yake ji duk asanadin ta ya rasa komai, one thing dayafi damunsa shine yadda ya kasa yakaceta aransa, wani mugun Tsaki yaja hade da kaiwa hannusa daya haushi, gidan dayake zaune ma bakin kirin yake ganin sa tsbar takaici, mikewa tsaye yayi daga kan kujerar palon da yake zaune, kai komo yahau yi yanai nemawa kansa mafita, karshe dai ya yankewa kansa komawa Gida tunda dama ba koransa akayi ba shiya kori kasan, duban agogo yayi yaga biyar na yamma ta gota fasa tafiya yayi ya bari zuwa gobe.

Suna isowa Gidan, Salma ta jinjina kyan da girman gidan, fitowa tayi daga motan tanai karewa ko ina kallon, kallon Jafar tayi, tsaye yake bakin boot yana ciro trolleys dinta.
Tace "wow yaya this house is beautiful.."
Magana zaiyi sukaga an bude gate motar kirar avensis ta shigo, dauke kai Jafar yayi, salma kam kallon motar take har tayi parking idan suke tsaye, Junaina ce ta fito amotan hade dakaiwa Salma wani mugun kallo aranta tana fadin "i cnt believe this devil is my sister" wani mugun tsanan Salam takaraji tun ranar da Hajiya ta fadi mata ita kanwar tace, dan haushi ma ko asibiti kasa zuwa dubo ta tayi.
"Ya jafs ina wuni" tafada batare data kalle saba, tayi wucewarta

Bai amsa ba, sai kallon Salma dayayi yaga duk jikinta yayi sanyi, murya maraice tace "i dont think she will forgive me..

Yace "she is very angry but trust me she will hose down"
"I pray so" Salma ta fada hade da sauke ajiyar heart, ciki suka karasa, Hajiya na zaune palo tana kallon aljazeera, ladabce Salma ta gaidata, farin ciki mara misaltuwa ne lullube Hajiya, kasa zaune tayi ta mike tahau nannan da Salma, babban dakin mai kyau anan kasa Hajiya ta nuna mata amatsayin nata, Salma kam kin zama tayi ta nace lailai ita a dakin Hajiya zata sauka, hajiya kam taji dadi hakan, ranar kam Salma taga gata gurin Hajiya da Jaafar, sai wani narke masu take suna biyeta, Junaina kam sai binta da harara da tsaki take, zama tayi dakin tahau trying namban Mujahid dan kai masa rahota, taji wayarsa kashe.

****

Washe gari Mujahid yayi shirin sa tsaf cikin kananun kaya dayayi matukar fiddo azahirin kansa, kulle gidan yayi ya fada motarsa yaja yabar Gidan.

Bayan sun kare breakfast, wajen gidan Salma da Jaafar suka fito yanai nuna mata ko ina da garden dun gidan. Kaman masoyan juna gwanin shaawa suke tafe suna darawa abunsu ba tare da matsala tattare dasu ba, zayawo sukayi suka tsaya bakin motar sa, da alamun fita zaiyi. Marairace murya tayi tace "yaya yaushe zaka dawo ?
Folding hands dinsa yayi a kirji hade dakai mata wani killer smile, yace "tun baje gate ba harkin fara missing dina"
Dariya tayi, sai kuma ta tsayar da dariyan tace
"Yaya you're very special,
Shuru sukayi suna duban juna for some seconds sannan tace "plz karka dade.."
Agogon hanusa ya kalla yace "i promise..
Okay bye" ta fada..
Kashe mata ido yayi, sukai smiling atare sannan ya shiga motar yaja.

Palo ta komo hade da sauke dogon ajiyar zuciya, sai sannan ta tsaya karewa ko ina na palon kallo kasancewar babu kowa..
Palon ya hadu, idanuwan ta suka sauka kan Katunan frames mai step guda biyar manne jikin bangon palan, wata farar kyakyawan Tsoyuwar mai glass ce a babban frame din, "ko wace ce wannan" ta fada.
Mai bi masa ta kalla Hajiya da late Abban su Jaafar wanda sanye yake da kayan Sojoji, sai saura kuma hoton jaafar, junaina da Mujahid, sun mata kyau sosai, kallon na Mujahid tayi ta buga uban tsaki aranta tace "to hell with you".
Afusace ta juya zata bar gurin tagan shi Tsaye bakin kofar shigowa, kusan minti daya yayi tsaye ganin ta tsaye gaban Hotonsa, baisan wace ce ba, yadai tsaya jiran ta juyo.
Harga Allah ta tsorata da ganinsa, ihu yarage batayi ba ta maze ta tsayaa mayar mai da mugun kallon dayake wurgo mata.
Magana zai yi Hajiya ta fito daga daki tanai kiran Ummi, "naam Hajiya" Salma ta amsa aladabce, ganin Mujahid yasata daure fuska tace "kai kuma daga ina ?
Sosa keya yayi ya gaidata, tabe baki tayi

Da sauri Salma ta risina tace "yaya ina wuni, sannu da zuwa" fuskar ta daure da fara'a..
Kallon mamaki yabita dashi..
Hajiya tace "bada kai take ba, mugun banxa, Allah yasa dai zuciyarta a tsarkake take shiyasa bata nufeka da shairi ba upon all abun  dakai mata, idan baka sani ba toh yar'uwarka ce"
Ware ido yayi in shock.
Hajiya tacigaba "iskancin banxa au dama baka sani ba ?
"Bansanta ba, yama sunanta ? In serious tone yayi maganar
Kallon Banxa Hajiya tamai sannan ta kalli Salma tace "kiyi hakuri da abunda ya maki, Mujahid sunan sa, daga shi sai jaafar a haife.."
Shuru Salma tayi, ta mugun kuluwa da denying dinta da yayi, sai yanxu ta kara tabbata wa dagangan yaki nuna cewa yasanta tun farkon haduwan su..
Dakyar tace "ba komai hajiya ya wuce" wuce wa tayi daki, hajiya tabita abaya..
Tsaye Mujahid yayi gun hade da daura hannu akai, "yaushe tazo gidan nan ? Ya tambayi kansa..
Tifowa Salma tayi rike da Plate a hannu, ko kallan shi batayi ba ta wuce ta gabansa, fizgo hannuta yayi da karfi, ihu tasoyi yayi sauri rufe mata baki da hannusa yaja ta suka shiga kitchen, can karshe bango ya turata hade da matse ta da jikinsa har suna juwo numfashin Juna, tsuro tayi da ido, fuska ba annuri yace "What are you doing here, evil tramp from hell..
Alamun tamai da bakinta is close, cire hannu yayi daga bakinta, harara takai mai tace "the evil tramp is you, you kept me away from knowing my family and the worst part of the story you try putting me behind bars, why, do you hate me that much ?"
Cikin rashin damuwa da abunda tace yace "datx your story not mine, i need to know uban miya kawo ki gidan nan ? Cikin zare ido yayi maganar.
Dariyar takaici tayi tace "the only reason y am here, its because of your brother, he is such an Angel, so sweet, i cnt wait to be in his arms..".
Murde hannuta yayi, yanai mata mugun kallo da idanuwa sa da suka sauya launi zuwa ja, ko ajikinta saima kokarin gyara gashin kanta daya bazu gefe, hannu ya nunata dashi, "badai karuwan ci ya kawoki cikin gidan nanba, we shall cee about that.."
Tsaki taja ta kalli hannuta dayake rike dashi tace "M.u ka saki hannu karuwa mana, ko ka fara shiga tarko ne.." Cikin salon rainin wayo tayi maganar.
Haushi biyu ne ya kamashi, "wai M.u, amma yarinyar nan ta raina ni, kodan Yaya bamu" aransa yayi magana.
Rai bace yayi wurgi da Hannuta sannan ya juwa zai fita sukayi kicibis da Junaina zata shigo, "yaya yaushe ka dawo" ta fada da murnan ta, ko kallanta baiyi ba yayi gaba abunsa.
Tabe baki tayi, ganin Salma Mak'ale gurin kaman mai shirin kuka, karasawa gurinta tayi tanai kai mata kallon banxa sann tace "bawai kinzo gidan nan ba, better stay away from my boyfriend, Mujahid nawane nikadai, kodayake y am i wasting tym talking to you, very soon zaiyi kicking dinki out of this house cox he hate you so much Big sister" tsaki taja ta juya ta bude fridge tadau drink sannan ta fita tabar Salma daskare tanai kallon ta.
"Oh ma God, little sis you're too good ki falling wa M. U, na shiga uku" ta fada hade da zamewa kasa ta zauna.
Kanta ta daura kan kafafunta tahau yin kuka dani bansan dalili ba.
[9/7, 12:37 AM] Xarah Bukar: Zuma Sai Da Wuta

~na~
©χarafj bųkar
(Aunty Cute)

56

Ido jajir ta mike ta k'arasa bakin sink ta wanke fuskarta sannan ta fita zuwa palo, Junaina ta iske zaune tana kallon cartoon, kallon banza suka aikama juna sannan ta wuce dakin Hajiya. Kallon daya Hajiya tayi mata tagano kuka tayi batace mata komai ta mike ta fita a dakin. Jiki ba kwari ta fada gado ta kwanta, lumshe ido tayi hade da girgiza kanta tana fadin kanwata da Mujahid, no no it wont happen gaskia, mutumin nan mugune, i wont allow him hurt my little sis" maganganu tahau yi tamkar tababbiya daga bisani kuma shuru tayi tanai neman mafita.

Karfe takwas na dare Jafar ya dawo gidan, baiyi mamakin ganin Mujahid ba, ko takansa biya ba ya karasa kitchen inda yajiyo muryar Hajiya tanai bawa masu aikin ordern su tsaftace ko ina.
"Sweetheart da kanki, yau kece a kitchen" ya fada yanai karasa shiga kitchen din.
Dariya tayi ta rufe kofar fridge datake rike dashi tana duban yadda yake kyalli, "Son kansan dole saida sa ido, maid dinnan sumtymz basu sanin aikin su"
Sosa keya yayi yace "naga Mujahid ya dawo, why ?
Tabe baki tayi,
"Wayasan mai, ni tunda yaxo baice min komai ba"
Nisawa Jafar yayi.
"Ummi fah, tana ina ?
Kwatar da Murya Hajiya tayi, tace "tana daki, i dunno watx wrong with her amma dagani she is depressed"
"bari naje naganta" ya fada da azama hade da juyawa.

Zaune take bisa praying mat tayi tagumi bayan ta idar da sallar ishaai. Shigowa yayi hade da Sallama, amsawa tayi tare da saurin gyara zama tanai sakar mai murmushi, kusa da ita ya zauna yanai kare mata kallo, yace "meke damunki ?
"Maika gani, ba abunda ke damuna..
Hannuta ya riko, tadan razana, ya lura da hakan ya share yace "you're lieing, nasan akwai abunda ke damunki i can feel it"
Kallon shi tayi ido cike da tear, ahankali ta zame hannuta daka nasa, cikin sanyi murya tace "you're a good man, i dont tink you will be happy with me"
"Miyasa kikace haka, Don't you love me ?
Kuka ta fashe dashi hade da kawar da fuska tana shesheka, hannu yakai bisa fuskar ya juyo da ita sunai fuskan ta juna, murumshi ya sakar mata yace "bana son kuka tashi muje muyi Dinner"
Atare suka mike, ya goge mata hawaye yace ta shiga toilet ta wanke fuska, ba musu taje ta wanko ta fito, cikin zolaya yace "to miye kuma na b'ata rai, sai kinmin murmushi zamu fita".
Dariya tayi bata ce komai ba suka fita tare zuwa palo.

Dining area suka nufa, Mujahid na zaune shida Junaina tanai mai magana kasa kasa, shikuma yayi kicin kicin da Fuska, ganin Salma da Jafar yaka daure fuska. Hajiya kuwa tana palo zaune, bata fiya cin abincin dare ba.

Zama Salma tayi ba tare data kalle saba, gefenta Jafar ya zauna.
Hararar iska Junaina tayi sannan tace ya jafs kaifah muke jira tun dazu"
Dariya yayi
"Ai gani nazo you can served us.."
Cikin zumudi dajin dadi yay mata dariya unlike kwanaki dayake daure mata fuska, hannu takai kan serving spoon zata dauka Salma ta rigata dauka, tsaki taja ta janye hannuta. Murmushi Salma tayi ta bude warmers din, ganish macroni ne da pepper chiken, plate din gaban Jafar ta zuba abinci sannan ta ijiye serving spoon din.
Kallon ta Jaafar yayi yace "bazaki zubawa kanki ba"
Spoon tadauka tace "habibty tare zan ci dakai" ashagwabe tayi maganar.
Mugun kallo Mujahid yakai mata, so yake su hada ido amma taki kallon shi, saima faran cin abincin sukayi tana zuba mai yauki da yanga.
Junaina kuwa tafi shi k'ulewa yadda Salma ta nuna halin kota kula da serving dinsu, kallon Mujahid tayi, tanaso tasama masu abinci tare tana tsoron ya dizga ta, mazewa tayi ta zuba mai da niyyan suci tare taga ya mike yadau plate din abinci ya koma kujerar dake fuskantar Salma ya zauna..
Kuka ne kadai ya rage Junaina batayi ba, akule ta dibi nata abinci tanai kaiwa su Salma Harara.

Ajiye Spoon din Salma tayi, murya kasa kasa tace
"Yaya feed me Hannu na ciwo"
Murmushi Jafar yayi, ya fara feeding dinta, fork ya dauka ya yanki kazar xai bata abaki, da sauri ta girgiza kai tare da turo mouth "no yaya hakorina ke ciwo, bazan iya ci ba ka faraci abakin ka idan yayi laushi saika ban"
Dariya sosai tabashi, ya  dake yasa naman abakinsa yafara ci, sai kallon shi take tana lumshe ido.

Dogon Tsaki Junaina  taja jin abunda Salma tace, aranta tace "so disgusting"mikewa tayi hade da daukan abincinta ta koma palo.

Duk yadda Mujahid yaso su hada ido da Salma ki tayi, iya kuluwa yakai da rainin hankali da suke agabansa, saidai bazai bari ta amshin Kazar bakin k'anin saba. kafarsa yakai daidai kan nata hade da murjesu da karfin gaske.
Dan karamin kara ta tsaki takai dubanta kan Mujahid,
"habibty miya faru ? Jafar ya fada, duk ta kidime zabar yadda Mujahid ke cigaba da take mata kafa.
Cikin inda inda tace "yaya hakorina xai cire.."
"This is serious" jafar ya fada hade da mikewa yace bari nakawo maki warm water" da sauri yabi hanyar kitchen.

Matso da Fuskan sa Mujahid yayi kusa da fuskanta, sannan ya kalli palo dan tabbar da babu wanda ke ganin su, Duban ta yayi fuskar daure, yace "what do you think you're doing ?" Ahankali yayi maganar.
Harara takai mai, ta matso da fuskan ta tsatin kunnansa tace "Datx non of your bizness, kuma kabar taka min kafa"
"You're trying to seduce hime right ?
Bitting lower lips dinta tayi tare da kashe mai daradara eyes dinta yace "kwarai kuwa, are you jealous ?
Dariya yayi yakai mata cixo a kumatu sannan yace
"Dont even tink about it"
kallon banxa tamai, ta shafa inda ya cixa tace "dan iska kawai" mikewa tayi afusace zata koma palo yasa mata kafa tafadi tim akasa.
"Subhanallahi" Hajiya da Jafar suka fada tare, fitowan shi daga kitchen yaga duk abunda ya faru, sharewa yayi ya karasa gurinta, "sorry Habibty" ya fada yanai kokarin taimaka mata, Mikewa tayi batare data bari ya tab'a taba, yaken dole tayi tace "yaya ba komai fah, faduwa kawai nayi"
Sannu yahau cemata suka zauna a kujera 3 sitter, Hajiya ma sannu tai mata, junai kuwa sai dariya take kyalkyalewa.. Oga Mujahid baima san suna yiba, banda abincisa da yakeci ko ajikinsa.

Warm water din Jafar yabata, kin sha tayi tace hakorin yadaina ciwo, shuru tayi bata kuma cewa uffan fa tsananin yadda Mujahid ya bata mata rai, tunanin yadda zata rama kawai take. Duk yadda Jafar yaso suyi hira kin kulashi tayi daga bisani ta koma
daki ta kwanta........

Typing din yau sai Ahankali wollah....
Kuyi maneji
[9/7, 12:37 AM] Xarah Bukar: Zuma Sai Da Wuta

~na~
©ӽaraɧ bųkaɾ
(Aunty Cute)
®NWA

Allahu akbar kulu'nafsi za'ikatu mauti, Allah yaji kanki da rahma Maman besty Yar ficika. May jannatul Firdausi be ur final destination.

Barin palon sukayi yarage Hajiya da Mujahid. Mik'ewa yayi kamar marar gaskia zai haura sama tace "koma ka zauna" fuska ba wahala ta fad'i hakan.
Komawa yayi ya zauna ba tare dayace uffan ba.
Hajiya tace "miya dawo dakai gidan nan ?
Nisawa yayi.
"Ba komai, kawai naga banda aikin yi ne"
Mugun kallo ta aika mai.
"Mujahid ka fita ido na, ka dauna banga sanda kasa mata kafa ta fadi ba, kuma nasan sarai saboda ita ka dawo gidan nan".
Sose k'eya yayi, murya kasa kasa yace "nifa ba ruwana da ita bamma san da zaman taba, infact ko ak'afa aka d'auramim ita bazan jaba"
K'wafa Hajiya tayi, ta shak'e abunda yace ba kad'an ba.
"Tashi ka bani guri kafin na kwashe ka da mari"
Dariya yayi ahankali ya mike hade da mata asubah ta gari ya haura Sama.
Washe gari yakama weekend, kowa sai sanda yaga dama yake tashi bacci, around 10 Salma ta tashi tayi wanka ta shirya cikin dogowar riga atamfa, fitowa tayi daka d'akin ahankali gudun karta tashi Hajiya, kitchen ta shiga had'a tea ta hango shi ta window yana playing basket ball, Murmushi tayi tace "perfect timing, yanzu miya kamata nayi mai" tunani tahau yi, can dabara ta fado mata, fridge ta bude ta dibi atarugu da yawa tasa a bowl ta jika da ruwa zafi Sannan ta sane ruwan a bowl, daukan ruwan tayi ta haurawa Sama da sauri. Dakuna Hudu tagani mai dauke da parlour, shiga na farko tayi babu alumun da wani ciki, tana leka na biyu ta hangi Jafar zaune gaban laptop yana dannawa, saurin komawa baya tayi, next dakin data shiga ya tabbar mata da dakinsane, daddadan kamshi da sanyi ke tashi ta ko wana lungu da sakon d'akin. Dariya tayi ta shige Toilet tadau shower gel dinsa ta bude ta zuba ruwan taragun sannan tafito da sauri tafara saukowa, kafin ta ida sauka Junaina ta fito daki wucewa kitchen, hada ido sukayi Junaina tayi saurin dauke kai bayan ta maka mata uwar harara. Salma kam bata damu ba, palo ta zauna hade da kunna Tv.

Kusan rabin awa Mujahid yayi yana playing b-b kanan ya koma cikin gidan, jikin sa sharkaf da zufa, so yake kadai yayi freshen up dan samun dadi jikinsa, Salma naji shigowarsa ta maida dubanta garesa, dogon tsaki taja ta hararesa hade da dauke kanta, bai ce mata uffan ba ya haye sama, aranshi yana fadin "bari nayi wanka na sauko zakici ubanki ne"
Toilet ya fad'a ya sakarwa kanshi ruwan shower mai dumi, shower gel din yadau ya matso hade da shafawa a fuska daidai kan idanunwa sa, runtse ido yayi sakamakan azaban daya ziyar ci idon, "wanna yajin daga ina kuma" yafa d'a aranshi, kara tasar gel din yayi yakuma shafawa dan wanke idon da kyau, raradi ya kuma ji yayi azama kashe warm water aganinsa yajin daga ruwan dumin ne, ruwan sanyi ya kunna ya kuma murza gel din a ido, azabar tafi ta daxu, wulli yayi da shower gel din yahau murza ido da ruwan sanyi saidai ina ko alamun sauki baiji ba banda radadi da idon suke, sosai suka sauya launi zuwa jajir. Ganin ba madafa yasa ya dau sabulun dake gurin yayi wanka adaddafa idanu a kulle.

Murumshi kawai Salma keyi ita daya, jira take taji ihun sa shuru bataji ba, jin taku ana saukowa yasata azama mik'ewa tsaye hade da kallon gurin. Jaafar tagani, laptop rike hannusa yanai

sakar mata murmushi.
Yace "har kin tashi ?
Risina tayi
"Yaya ina kwana ?
Lapia" ya amsa, aranshi yana mamakin bata kirashi da Habibi ba.
"Yaya fita zakayi"
Kai ya girgiza, "garden zan futa na zauna, akwai aikin da nakeyi nagaji da zaman d'aka"
"Muje na tayaka zama" Ta fada hade da daukar wayarta dake ajiye kan kujera.
Murmushi yay yayi gaba ta mara mai baya.

Duk akan Idon Junaina dake makale bakin kofa kitchen, haushi ne yakamata.
"matar nan sai shishigin tsiya wlh, da farar safiya ko miye nabinsa waje" ta fadi, tsaki taja wata zuciya tace kema kije gurin masoyinki Mujahid mana, kai ta girgiza tace aikuwa dai kila ma bacci yake bara naje na tasoshi muje waje. Da sauri ta haura saman.

Dakyar Mujahid ya iya bude ido, sosai sukayi Jajir, ko lotion bai iya shafawa ba ya shirya cikin kananun kaya, black shade yasanya a fuska ya koma toilet yadau shower gel din yana kalla cike da mamakin sabon al'amari.

Ahankali Junaina ta turo kofar dakin ta shigo, babu kowa ciki tayi tunanin koya fita, wayarsa data gani kan gado yasa ta karasa ciki hade da daukar wayar, camera ta shiga zata dauki kanta Selfi ya fito daga toilet. A tsorace ta dire wayar, cikin inda inda tace "Good morning".
Mamaki ne yakama shi, yaushe Junaina ta renashi haka harda shigomai daki batare da izinin saba.
Fuska ya murtuke "ke!!! Miya shigo dake nan..
Kaman marar gaskiya ta ware idanu, "dama wai kiran ka zan..."
Katse ta yayi da cewa "wato bincike kika zo yimin ad'aki harda daukan wayata, gayamin waya aikoki ?
Yadda yake magana yasa ta tsorota, bata ga alamun wasa tattare dashi ba, kaman zatayi kuka tace "wallahi yaya ba bincike nazo yi ba ?..
Cikin tsawa yace "karya kike, ni nasan halin ki  am sure kuma rahoto kikazo samu dan kaiwa gaba".
Kasa magana Junaina tayi, gabanta na dukan uku uku, ga kuma haushi  kalamansa daya turnuk'e ta, koda take nemo rahoto aishi take kawo wa shine kuma yau zaiyi turning tables around.
"Get down on your kneels" ya fada cikin harsh voice.
Kuka ta fashe dashi "yaya dan Allah kayi hakuri"
Rab'awa yayi ta gefenta ya wuce yana cewa "bari na dauko belt, yau sai kin gayamin ubanwa ya aiko ki"
Da sauri tayi kneel down tana rokansa, belt ya dauko ya tsula mata daya abaya, ihu tayi tace "na shiga uku, yaya wlh da akwai zafi"
Jinjina kai yayi yana tunanin anya ba ita tasamai abu mai yaji a shower gel dinsa ba, dan kuwa kafin yafita playing b-b yayi wanka da gel din baiji yaji ba.

Fuska ba annuri yace "wato daxun kin shigomin daki ko ?.
Ware ido tayi cikin rashin fahimta, yace "badake nake ba" daka belt yayi zai tsula mata.
Tace "yaya wlh yanxu nashigo, daxu dai naga Adda Ummi ta sauko daga stairs bansani ba konan ta shigo" kuka sosai ta fashe dashi
Cize Lab'a Mujahid yayi aranshi yace "lailai yarinyar nan ta cika yar daba" kallon Junaina yayi yace "b4 d count of three tashi ki bace anan"
Mikewa tayi ta fita da gudu tana sosa baya.

Nisawa Mujahid yayi yakarasa bakin mirror, cire glass dun fuskar sa yayi yanai kallon idonsa dayai jajir ya duru da ruwa, wani irin raradi da azaba yake ji.
Sunan Salma kadai yake ambata aranshi, shi kadai yasan rashin mutumcin dazai mata.

A can Garden kuma.....

To be continued......
[9/7, 12:37 AM] Xarah Bukar: Zuma Sai Da Wuta

~na~
©ɀarah bųkar
(Aunty Cute)

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION...

Allahu akbar kulu'nafsi za'ikatu mauti, Allah yaji kanki da rahma Maman besty Yar ficika. May jannatul Firdausi be ur final destination.

58

Acan Garden kuwa zaune suke kan d'aya daga cikin kujerun, Jafar kam duk'ufa yayi da danna laptop dinsa kasancewar wani babban aiki dayasa agaba, Salma kuwa wayarta kadai take latsawa, so take ta kira Mujahid amma tafasa gudun karya dago abun data mai, ajiye wayar tayi a cinye hade da sauke ajiyar zuciya.
"Kin gaji ne ? Jafar ya fad'a yana cigaba da aikin sa ba tare daya dube taba.
Dubansa tayi.
"Bakai ka shareni ba" ashagwabe tayi maganar.
Dariya yayi
"Kinga wani case nake bincike akai, mayb zuwa next week zanje Kaduna"
Dadi Salma taji aranta, idan ya tafi zata samu sararin yiwa Mujahid rashin mutunci.
"Murna kike zan tafi ko ? Ya jeho mata tambaya.
Kunya ce takamata, ta dake tace "yazaka ce hakan bayan kai yayana abun alfahari nane, ni wlh banso ka tafi kaine kaidai good abu arayuwa ta"
Murumshi yayi, ciki ciki yace "naga alama kam".

Bataji abun da yace ba, zatayi magana suka ji ana rangad'a uban horn daga can bakin gate, maida dubansu sukayi b'angaran, wata mota jeep ce ta shigo ta karasa maajiyar motoci ta tsaya.
Salma tace "suwaye ne..
Mikewa tsaye yayi itama ta mike suka fara tawaka gurin....
Wata kyakyawar tsohuwar matar ce ta zuro kafa daga motan ta fito, da ganinta kasan ta hada alak'a da masu gidan, da azama driver ya zagawo gurin ta hade da risinawa ya mika mata wani sliver walking stick, amsa tayi tanai karewa gidan kallon hade da sauke sanyayyiyar ajiyar zuciya.
Gaban Salma ne yafadi, tagane matar data gani a hoto ce, murya jafar taj yace "Granny dinmu ce, mahaifiyar Daddyn mu"
Yaken dole Salma tayi, kwakwata bataga alamun annuri a fuskar taba, shuru tayi suka cigaba da takawa gurin da take tsaye tana shakar sanyayyar iskar gurin.
Daga inda suke tagowa Jafar yace "wa nake gani kaman Annah." Karashe maganar yayi cikin zolaya.
Dariya Annah tayi har hakoranta suka bayyana.
Ga mamakin Salma taga Annah ta juya wani bangaran tana lalube, cewa take "Jafar kaine ko kuwa kunne na ne ?
Karasawa yayi ya rikon ta, yana dariya gani tanan".
Tace mikomin gilashi na yana mota, dauko mata yayi ta amsa tasa sannan ta kallesa "wato kun gurma ko ganin ku baa yi, tunda baku iya zuwa gurina gani zo gurinku"..
Dariya yayi.
"Kai Annah daga zuwa sai neman sababi ?
"Kaga ni bani guri" ta fada, wucewa zatayi Salma tace "Annah ina wuni ?
Kallon Salma tayi, bata amsa ba sai tab'e baki datayi ta wuce.
Jiki sanyaye Salma ta dubi shi.
"Bata gani ne ?
Alamun tayi shuru yayi mata, saida Annah ta masu tazara yace "zaki sha duka idan taji kinci mata bata gani, tana gani amma sai da glasses,
Ware ido salma tayi.
"Miya sameta halan
"Bakomai, ciwon idon gada sukayi gurin babansu, sai dai nata yayi worst, sau biyu ana mata operation"
"Allah sarki, amma naga ku yaran Hajiya baku gada ba"
Dariya jafar yayi, yace "inji wa, koda yake niban da matsalan ido, Aunty Bilki da Mujahid suka gado ta"
Mamaki ne yakama Salma bata ga alamun ciwon ido ga mujahid ba, dama ma Aunty Bilki tanasa glass.
Shuru tayi suka cigaba da tafiya ciki.

Side drawer Mujahid ya bude yadauko wani magana a tube ya diga a idon, wani mugun azaba yaji, maida black shade yayi ya fice daga d'akin.

Ta bangaran Junai kuwa kitchen ta shiga ta zauna matsar kwalla, koda Hajiya ta fito ta isketa a hakan ba tambayar da batai mata ba taki fad'a mata komai sai cewa tayi cikinta ke ciwo, Palo hajiya ta riko ta suka dawo tanai mata sannu.

Banko kofar Palo Annah tayi batare da Sallama ba ta kutsa kai ciki ta fadin "ba kowa agidan ne ?
Adan tsorace su Hajiya suka juya kallanta jin yadda aka banko kofar, bata yi samma nin ganin taba ba dan kuwa sunyi waya jiya bata ce mata tana tafe ba.
Dakyar Hajiya ta iya hadiyan yawu tace "Annah sannu da zuwa, aibansan kina tafe ba"
Tabe baki tayi ta kalli yadda palon ke haskawa da kayan alatu, tace "yanzu kin ganni ai
Shuru Hajiya tayi, Junaina ta gaidata, nunata tayi da walking stick din tace "kece haka kika girma ?
Magana Junai zatayi Salma da Jaafar suka shigo palon adaidai lokacin da Mujahid ya sauko daga stairs.
Zubamai ido sukayi, ko kallonsu bayi ba, fuska daure ya kama hanyar ficewa, dakatar dashi Hajiya tayi da cewa "bakaga Annah ba zaka wuce ?
Tsaye yayi chak yanai ma wani Annah mugun kallo ta Black shade din fuskar sa, aranshi yace "uhnm sai yadda ta yuyu kenan, nakuda ad'aki mayya"
Afili yace "mai makauniyar nan tazoyi agidan nan ?
B'ata rai Annah tayi ta k'arasa kusa dashi, bai ankara ba yaji ta fara kaimai Duka da Sandar hannu ta tana fadin "uwar ka nazo, dan tselan uwa kawai" ta ko ina tahau kaimai bugu, ihu kadai yarage baiyi ba tsabar yadda sandar keda zafi, Salma kam dariya tahau babbaka wa, ayayinda saura kuma suke kallon Annah cike da takaicin abunda take, Mujahid kam ganin ba bari zatayi ba yasa yayi hanyar waje da sauri, baima lura ba yaji ya buge kai da bango, da azama ya fice waje.

"Ni zai nunawa duniyan ci kamar wace ya samu sa'ar sa" Annah ta fada Masifa sosai tahau yi, Salma kam kasa daina dariya tayi, da sauri tabi bayan sa waje, Mugun kallo Annah takai masu, tace da Hajiya ke kuma muje ciki ina da magana dake, haushi biu ne yakama hajiya ba yadda ta iya ta marawa Annah baya suka shiga daki.

Ajiyar Zuciya Junaina ta sauke ta kalli Jafar dake tsaye yana jin haushin fitar Salma, tace "yaya Alhakina ya kaima ya Mujahid, dazu bakaga dukan da yayi min ba
Da mamaki ya kalle ta, "duka kuma, mi kikayi ?
"Daga daukar wayarsa, wai bincike zan mar, yahau ni da zagi da duka"
Dariya zancenta yabashi, yace "yayi maganin ki kenan ?
Turo baki tayi "aini yanxu ba ruwana dashi, he is so mean".
Murmushi yayi, Baice komai ba ya wuce ya haura sama, turo baki tayi ta tahau gungunin baice mata sannu ba.

Haraban Gidan Salma ta fito waigen inda Mujahid yake, daga can nesa ta ganshi gurin parking motaci zaune kan boot din motarsa, kansa daure bisa cinyar sa.
Karasawa tayi gurin tana mamakin miyake yi gurin. Yana jin tsayuwar ta gurin yaki d'ago wa,

hannu tasa ta d'ago da fuskar sa tana fadin "yaya badai dukan nan yasaka kuka ba" cike da zolaya tayi maganar, saidai ganin shatin dukan da yadda fuskarsa ta kumbura yasata ta shan jinin jikinta.
Hawaye taga ya fara gangarowa bisa kunci sa, yace "hankalin ki ya kwanta koh tunda kinga karshe na?
Cike da kidima da tsoro take kallan sa, gabanta sai faduwa yake..
Murmushin takaici yayi yace
"Am sorry nasan nayi hurting dinki, plz forgive me".
Tausayin sane ya kamata saidai bazata bari ya raina mata wayo ba, tace "miyasa sai yanzu zaka nemi afuwata ?
Ahankali ya zamo daga kan motar, suna fuskan tar juna, cikin sanyi murya yace "Salma i love you alot, dou nasan ba lailai ne ki yadda ba but tun ranar dana fara ganinki nakasa samin nutsuwa, kawai karfin hali da ego irin nawa yasa ban taba fahimtar hakan ba sai yau"
Kur Salma tayi mai da idanu, danson tantance gaskiar maganar sa ko kadan bata yadda dashi ba, saidai taji dadi i love you daya ce mata, kalamar data jima take son ji garesa, koda ace karya yake itadai taji dadi.

Dariyar rainin wayo ta saki sannan kuma ta daure fuska tace "do you tink am stupid, if i could recall, kwanakin baya haka kazo kace you liked me, ka bukaci friendship dina nikuma i was dumb nayi accepting, at last miya biyo baya, you wanted killing me, tnkx to Allah nayi surviving but still saida kaso ka kaini prison, gayamin wannan so ne ko kiyyaya or is it part of your egotistical behaviour ?
Hannuta ya riko, yace "nasan baza ki yadda ba, kin tsane ni, but plz find a place in your heart ki yafemin"
Dogon Tsaki Salma taja.
"You're not serious" ta fada hade da kawar da kanta gefen, sam ta kasa fahimtar inda ya dosa.
Gani tayi yayi kneeling down, da sauri ta kalle shi hade da ware idano.
Black shade din fuskar sa yacire yace " ciwon ido zai zama ajalina, i dont tink zan iya kaiwa jibi da irin azabar da nakeji, bazaki bani tym ko kadan ba ?
Tsoro da firgice ne suka kamata ganin yadda idonsa yayi jajir suna zubo ruwa, runtse ido yayi da sauri dan bazai iya barin su bude ba.
Tsugunna wa tayi gabansa,
Cikin rawar Murya tace "yaya miyasa me ka haka?
Kuka ya fashe dashi "i dont know, mayb kuma shower gel dina yayi expire nikuma nayi using yayi affecting dina, koma. dai miye ne ya illatani dayawa coz i cnt see clearly".
Na shiga uku na kasheshi, Salma ta fada aranta, sai yanxu tagane dalilin buguwarsa a bango daxu. Kaman zatayi kuka tace "plz yaya tashi muje asibiti, i cnt see you liked this"
Kai ya girgiza.
"karki damu nariga nayi using wani magani na, kuma banaso Hajiya tasan ina cikin matsala zata iya shiga tashin hankali"
Hannuta ya riko gabaya, "just tell me kin yafemin ko zanji dadi araina"
Sosai yabata Tausayi, wani irin haushin kanta take ji da muguntar da tamai, tace "yaya na yafe maka dukdai ban rikeka araina ba, but plz kadaina cewa xaka mutu, you cnt leave me"

Ajiyar zuciya ya sauke, ya zauna akasa had'e da zaunar da ita yace "kinga no secret between us, nafada mike zuciyata, do you have something to confess ?.
Shuru tayi, gabanta na faduwa, tanason gayamai itace silan komai tana tsoro.
Ji tayi yace taimaka min mu shiga ciki, kinsan yanxu na zama makaho.
Mikewa tayi jiki sanyaye suka fara takawa ciki, sun kusa shiga Palo Salma ta tsaya tace "yaya karsu Hajiya su ganmu tare, miza muce masu ?
Yace "hakane ga wayata ki kira Faiza tazo, tunda na makance bakya so aganmu tare, nasan ita komin rintsi she wil stand by me"
Cire wayar yayi aljihu ya mike mata, kin karba tayi tace "wasa nake fah"
Aranta kuwa tace "wana hauka ya kaini kirama wannan bazawarar"
Ciki suka shiga suka ci saa ba kowa a palon sai junai da hankalinta gabadaya yana kan Tv, ahankali ta taimaka mai suka haura sama.

Masifa Annah tahau yiwa Hajiya adaki, akan yara sun girma har zasu tsofe taki aurar dasu alhalin ga yammata har biyu a gida, Hakuri Hajiya tahau bata tace "Annah so nake Mujahid da ita Ummi su shirya kansu sai ayi auran, nafison su tare akan da Jafar, da dukkan alamu kuma suna son juna"
Tasaki Annah taja tace "zancen banxa kenan, ina ruwan wani da shirin su ko boyayyar soyayyar su, ni Ummi tafi kwanta min da Jafar, baki gansu dazun ba gwanin shaawa sun dace sosai, kuma da bakinki kika cemin Marikin Ummi yafi son ta auri Jafar".
"Annah gaskia hakan baiyi daidai ba"
Ware ido Anna tayi tace "toh uwata saiki dakeni ai, kinsan dai na fiki iko da yaran nan tunda ni uwar uban suce".
Hajiya tace "hakane, duk yadda kikayi daidai ne"
Washe baki Annah tayi tace "Dadina dake saurin fahimta, tunda yanzu nazo gidan yaushe zaki tafi Maiduguri yi masu albishir din bayyanar Ummi da kuma batun auran, bana so adau lokaci, gwara ayi buki tunda karfi na ".
Mamaki ne yakama Hajiya, sai kace tace mata zataje Maiduguri, kodayake dama tana da niyyan zuwa.
Tace "sai wani watan na shirya zuwa"
Ware ido Annah tayi, tace "nan da wata daya, lailai salamatu bakya so naga auran nan, tab aikuwa hakan bazai yuyuba gobe zaki tafi Maiduguri, dan kuwa ba zama nazoyi a garin nan ba, Buki ya kawoni, ki shirya gobe ki wuce kafin ki dawo kuma zan nemi Daddyn Ummi mu tsayar da rana"
Hajiya kam bata iya cewa komai ba tsabar takaici, tasan zaman Annah gidan husuma kawai zata hada ta tsangwamawa yaran gidan.
Allah ya kaimu gobe" hajiya ta fada, barin daki tayi ta koma dakinta tahau shirya kaya a akwati.

Daki Salma ta shigar da Mujahid, zama yayi gefe godon yace "i really need some sleep"
Jiki na rawa ta yaye comforter dake gado, kwaciya yayi ta rufa mai comfortee din sannan ta zauna gefe sa tana kallon kyakyawan fuskar sa, idonsa rufe, yana fidda numfashi ahankali.
Ta jima zaune harta lura bacci yayi gaba dashi, da sauri ta mike tsadaf ta shiga bandakin sa, showee gel din tadauka ta fito ahankali ta fice daga dakin, duk akan idonsa, abun da yakeson

Tabbatar wa kenan wato itace tamai mugun tar nan, yunkurowa yayi zaune hade da wrugi da pilo, dafe kai yayi yace "what should i do na huce abunda kika min, most annoying part shine ko kuka batayi minba ayadda taga condition dina"
Dogon Tsaki yaja, jin motsi kofa yasashi komawa ya kwanta hade da runtse ido, Salma ce ta shigo ta karaso da sauri ta zauna gefen sa, pilo data gani akasa tadauka ta runguma tanai aika mai kallon mai cike da so da kauna, batasan sanda bakinta ya furta I love you..., shuru tayi saurin yi hade da kama bakinta, Allah yasa bai jita ba tafadi aranta. Tafin hannuta tasa ta rufe fuskan ta.

Bude ido yayi ya kalleta hade da sakin Wani irin shuumin Murmushi wanda dashi kadai yasan maanar sa, lumshe ido yayi cikin jin dadin kamshi jikinta dayake shaka.
[9/7, 12:38 AM] Xarah Bukar: Zuma Sai Da Wuta

~na~
©ҳaraɧ bųkar
(Aunty Cute)

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION

Allahu akbar kulu'nafsi za'ikatu mauti, Allah yaji kanki da rahma Maman besty Yar ficika. May jannatul Firdausi be ur final destination.

59

Gidan shuru kowa lafe cikin turak'arsa, zuwan Annah sam bai d'ad'ara suba, ganin kowa ya batsar da ita yasa ta dunga saka da warwara rashin nasiha da zata shukawa yaran gidan.
Ta b'angaran Salam kuwa yuni ranar ita ta funte hajun Mujahid.

Washegari da safe yakama ranar da Hajiya zata tafi Maiduguri, zuge zip din akwatinta tayi sannan ta kalli Salma dake gyara gadon, kiran sunan ta tayi cikin wata murya bai abar tausayi, dubanta Salma tayi had'e da amsawa.
Hajiya tace.
"Mujahid ya tashi daga bacci ?
Kunya ce takama Salma, duk'ar dakai tayi k'asa sanna tace "bangan shi a palo ba, k'ila bai tashi ba"
Nisawa Hajiya tayi, ta karasa kusa gareta had'e da zaunar da ita kan gadon suna fuskan tar juna, tace,
"Salma burina bai wuce na had'aki aure da mujahid ba, dan Allah kiyi hakuri kuyi sorting difference dinku kafin nadawo, nasan kuna san junanku, i just dont know miyasa kuke nunawa juna k'iyayya"
Shuru Salma tayi tana wasa dayan yatsun hannayan ta.
Hajiya tacigaba.
"wani abu daya da mujahid ko yanasan abu hardly yake nunawa, saboda yadda ya d'auki

kanshi yafi karfi ko wana abu, amma deep down he really carez, sometimes saiki kiga dan hakkin daya raina yana neman tsone mai ido"
Murmurshi kawai Salma tayi, ganin haka yasa Hajiya tadan ji sanyi aranta, fitowa sukayi Salma biye da akwatin suka shiga dakin Annah, sallama Hajiya tayi mata suka fita haraban gidan.
Jafar da Junai tsaye bakin motar suna jiran Hajiyan, da ganinta Junai tahau kukan zata bita, dakyar dai Hajiya ta lallab'ata tayi shuru sannan ta shiga motar, Driver dake zaune ciki yajata suka wuce.
Sabon kuka junai tahau yi  ayayinda Jafar sai bata baki yake tana k'ara tunzura da kuka shagwab'a, Salma kam murmushi tayi ta juya ciki ta barsu nan ganin abun nasu bana karewa bane.

Kitchen ta nufa tadau Breakfast din Mujahid tahaura sama dashi cikin sauri gudun kar Annah ta cafketa, ahankali ta tura kofar Palon ta hange shi can nesa kwance kan 3 sitter yana kallon nta news. Mamakine ya kamata, mai ciwon ido da kallan Tv, Sallama tayi ta tsaya nan inda take.
Mikewa zaune yayi ya kalleta sannan ya amsa sallaman, takowa tayi ciki tana kallon idonsa, ba laifi idon ya koma normal said'an kumburi dabaza arasa ba.
Murmushi tace "yaya harka tashi ? Karashe maganar tayi tani kai mazauninta kan kujerar dayake zaune sannan ta ajiye abinci kan side table din gurin.
Murmushin kasaita ya sakar mata, irin murmushin nan dake fizgar zuciyan wanda akayi wa, kallon juna sukayi for some seconds zuciyoyin ko wanansu harbawa yake, kowa da abunda yakewa sak'awa cikinta, Dakyar Salma ta iya dawo wa duniyar ta, lumshe ido tayi tace "yaya ga abinci"
Jingine kansa yayi cikin kujerar yanai cigaba da kallonta, wani irin shaukin sonta ne ke ratsashi wanda shi karan kasan baigane hakan ba, abu daya ya fahimtar indai tana gurin baya tuna kowa bayan ita, cikin wata murya mai kashe garkuwan cikin bil'adama yace "feed me"
Wanni irin yir taji ajikinta da salon dayay maganar, hannuta na rawa tadau abinci dake plate din, kallonshi tayi taga yana kallon hannuta dabai bar rawa ba, "oh my God, kar mutumin nan ya gano weekness dina ko baa fada ba nasan nafi sonshi" ta fadi aranta.
Rike hannuta yayi, taji wani iri har cikin kwakwalwan kanta, da sauri ta mike kamar wace aka sikara, ajiye plate din tayi tace "na manta Annah ta sani aiki" ficewa tayi batare data jira cewar saba, Binta yayi kallo har ta fice. Aranshi mamaki yake anya shine kuwa, mike faruwa ne, daga pretending abu na neman zama gaskia, yasan yana son Salma kad'an saidai  baiso yafara having feelings sosai game da ita ba, asalima so yake ya mata rashin mutunci, inyaso daga baya saiya fara mata son gaskia.
Girgiza kai yayi yadau wayarsa dake gurin ya kira abokinsa Mubarak.
Bugu daya ya dauka, cikin zolaya yace "jobless man ka sauko daga fushin ?
Tsaki Mujahid yaja yace "kai banza ne, ana takai wayake ta kaya, ina cikin bigger problem"
Nutsuwa Mubarak yayi jin yadda yayi maganar in a serious tune, nan Mujahid ya kwashe komai yafa dimai sannan ya kara dacewa "inaga na fara sonta dagaske, jiya kwana nayi ina tunanin ta"
Nisawa mubarak yayi yace "yanzu toh ya zakayi, dont tell me kana kan bakanka na rama abun da tama"
Dariya Mujahid yayi

"bansan abunda zan mata ba, mayb hakura zanyi na rugumin sorry"
"dadai yafima, if not idan kace zaka kara mata wani mugun abu i dont tink zata cigaba da kula"
Shawara sosai Mubarak yayi tabashi, amma ayadda Fuskar Mujahid ya nuna banyi zaton zai bar Salma taci Bulus ba.

Tsaye Salma tayi bakin stairs, har yanzu jikinta baibar rawa ba, she need to be strong karya raina ta much less yanzu da take ganin ya riga ya gano sonshi a kwayar idanta, tanason Mujahid saidai wata zuciyar taki aminta dashi, tsoro take ya yaudari zuciyar ta datayi mugun kamu da kaunar sa. Muryar Annah taji a fito palo tana fadin "ba kowa agidan ne" leke tahau yi ganin babu kowa gurin, Tsoro ne ya kama Salma lafewa tayi gurin ba tare data iya k'wak'waran motsi ba. Jafar da Junai ne suka shigo, sai wani narkemai take shi kuma yanai biye mata.
Tsawan Annah sukaji akansu, afusace tace "wanan sabon salon fah, miye haka ?
Harara Junaina takai mata, Jafar yace "Miya faru ?
Nuna Junaina tayi da sandar hannuta tace "dan baki da kunya Mijin Yayar taki kike narkewa haka"
Ware idanu Salma da Junaina sukayi atare jin abunda tace, Junai tace "ban gane miji yayata ba?
Tsaki Annah taja tace "uwar taku bata fad'a muku ba, toh bari kiji dakyau ita Yayar taki data fiki nutsuwa itace matar Jafar, ke kuma da Mujahid da kuka raina ni tare zaku dauwama"
B'ata rai Junaina tayi, tahau gunguni hakan bazai yuyu ba, sandar Annah ta daga da niyyan kai mata tayi sauri fecewa hanyar dakinta da gudu.
Salma kam daskarewa gurin tayi, kallon ta Jafar yayi tayi sauri kawar da kai gefe kaman mai shirin yin kuka.
Duban jafar Annah tayi tace "muje daki, akwai abunda zan gayama" afusace ta juya yabita abaya yana mai cigaba da kallon Salma, jiki sanyaye Salma ta sauko ta wuce daki.

Adakin Annah kuwa abubuwa da dama tayi ta kimtsa wa Jafar akan lailai yaja Salma ajiki, shikam jinta kawai yake baice komai ba, bayan ta gama batun ta fita yayi daga dakin ya nufi gurin Salma.

Zama Salma tayi kan center carpet din dakin, kanta daure bisa gwiwar kafafunta, shigowa Jafar yayi ahankali ya zauna gefen ta, d'agowa tayi jin kamshin turararsa, kallon sa tayi yaga idanuwata mak'ale da hawayen dake kokarin zubowa, hannu yasa aljihu ya fiddo hanky ya mika mata, amsa tayi zatayi magana ya katse ta da cewa "shiiii...basai kince komai ba, i understand everything"
Shuru tayi tahau goge idanta sannan ta dubesa tace "Thank you"
Yace "you're most welcome, if you need anything, ko shawara game da brother na kina iya min magana, i'll alwayz be around to support you"
Cikin sanyi murya tace "yaya kana da kirki sosai, am sure kanwata zata ji dadin zama dakai"
Murmushi yayi, baice komai ba ya mike ya fice daka dakin. Ajiyar zuciya ta sauke ta shingid'e a gurin, tunani tahau yi daga bisani kuma ta mike ta fice Palo.

Junaina da Annah ta iske ana fadan kallon Tv, Annah hausa takeson kalla ita kuma Junai ta nace sai Disney channel, dariya draman yabata, sai kace babu Tv a dakunan su.
Ganinta Annah tayi tace yauwa diyar albarka zoki zauna nan" nuni tama Salma da tazo kusa da ita ta zauna.
Fuska ba yabo Salma takarasa ta zauna.
"ina kika baro jafar, aina dauka kuna tare". Annah ta fada tana washe hakori tamkar wanda akama albishir da abun arziki, Salma kuwa yaken dole tahau yi
Dogon Tsaki Junai taja tace "sai kace wani danta da zasu kasance tare, shifa yana study room yana wasu aiyukansa.." bata rufe baki ba taji sandar Annah abayan, mikewa tayi azabure.
"dan ubanki dake nake dazaki saki baki kina magana uwa an b'arka zani, hegiyakai tamulmule mai nono daya"
Turo baki Junai tahau yi, Annah taci gaba "niyau banma ga Mujahid ba, maza jeki kira min shi, dan tselan uwa wato bazai sauko gaida niba"
Junai kam ta gama kulewa, bakin stairs taje ta tsaya tana tunanin yadda zata doshi Mujahid.

Kallon Salma Annah tayi tace "ke kuma dauko min ruwa insha" mikewa Salma tayi ta nufi kitchen, da sauri Junai tabi ta abaya. Daukar ruwan Salma tayi ta juyo sukayi kicibis da ita tsaye gabanta tanai makamata harara.
Salma tace "lafiya ?
Tsaki Junaina taja tace "i dunno why kike claming kaman wata saint, kodayake ba wannan ya kawo niba, so nake kiyi using halinki nayan daba ko ma ince yar tasha, kisan yadda kikayi Annah ta sauya zancen ta na kokari lak'amin Mujahid da lak'amiki Jaafar"
Murmushi Salma tayi, sai kace ba rannan kadai Junai ke threatened dinta ta rabu da Mujahid ba, yau kuma table yayi turning kan Jafar.
Tace "abu mai sauki why not kicewa Annah bakya son ya Mujahid"
Ware ido junai tayi tace "so kike nasha duka kenan, muguwa kawai"
Salma tace "toh ya kikeso ayi, kinga ni am not complaining".
Mugun kallo Junai tai mata. "Ai dole kice haka, saboda jafar aka lak'amaki toh wlh baki isaba, yadda kike yar tasha da ya Mujahid kika dace, two devils"
Insult din yafara bawa Salma haushi, dakewa tayi tace "we have to work together idan kinaso musamu solution"
"Kaman ya kenan ?
Mika mata ruwan Salma tayi tace "ki kaiwa Annah ruwan, bara naje sama na kira Mujahid, ke idan kinje kice mata yana zuwa"
Amsan ruwan Junai tayi tace "idan ta tambayi ne kefa ?
"Datx your problem not mine" juyawa Salma tayi ta wuce tabar Junai tsaye gurin baki sake, dakyar ta tsaitseta kanta ta wuce gurin Annah, mika mata ruwan tayi tace gashi, harara Annah takai mata tace "akarambana waya aike ki, ina mujahid ?
Kaman marar gaskia tace "yana Zuwa, Ummi kuma ruwa ta zubar akitchen shine take gogewa tace nakawo maki ruwan".
Amsa ruwan tayi tanace mata "ja'ira harda kwantar da murya kamar gaske".

Da sauri Salma ta haura sama, tana shiga palon yana fitowa, yar gware sukayi kowa yayi saurin

matsawa baya, dafe gurin tayi tana kallon yadda yayi kyau sai zuba kamshi yake, kananun kaya jean da top ke sanye jikinsa. Gyara murya yayi yace "yau kuma kinzo fasamin kai ne ?
Bata gane inda zancensa ya dosa ba, murya shagwabe tace
"Kai yaya kodan sannu babu ?
Murmusawa yayi ya janyota wajan palon yana cewa "waya biyoki kike zabga uban gudu ?
Alamun yayi shuru tamai, murya kasa kasa tace "Annah na downstairs tana jiran ka"
Tabe baki yayi "muje ki rakani Shopping" hannuta ya riko suka karasa stair, da sauri ta zame hannuta tayi saurin rigashi sauka tana dariya kasa kasa.

Yana sauka ko kallan Annah bai yiba yace da ita sannu da zama, tagane da ita yake amman ta share. Duban Salma yayi da tuni ta zauna kan kujera yace "5min nabaki kisame ni waje bakin mota.."
Mikewa tayi kaman munafuka Annah tace "koma ki zauna, ke Junaina tashi ki sameshi awaje"
Galala Mujahid yabita da ido sannan yace "niba ita nace ba, ita wace na kira kasuwa zamuje da ita"..
"Aikuwa wace kakeso bazata bika ba.... Ke Ummi shiga ki kira Jafar yazo saiya kaiki kasuwan" nuna Junai tayi tace "dauko mayafi ki bisa" kaman bazata ba ganin Salma tai mata ido yasata dauko mayafin, takaici ne yakama Mujahid ya fice daga palon Junai ta bisa abaya kaman munafuka.

Fitowa Jafar yayi cike da taikaicin katse mai aiki da Annah tayi, jarabar ta yafara isanshi, so yake sati ya kama yabar masu gidan, fitowa waje sukayi su ukun, Annah sai washe baki take, saida taga ko wana couple sun shiga mota sunja sannan ta sauke ajiyar zuciya, tace "aifa dole kowanne taso hadin nan nawa, shegun yara kawai, Sannu-sannu ba ta hana zuwa, sai dai a dad'e ba a je ba" wani mahaukacin dariya ta saki tana cewa "muje zuwa, mahaukaci yahau kura".

Fuskar Mujahid daure babu annuri, tuki kawai yake har suka karaso babban titin, tsayar da motan yayi sannan ya kalli Junaina da tayi kicin kicin da fuska yace "zaki sauka ko saina bakin wawan mari "
Bude motar tayi ta fito tace "aiko baka fad'aba bazan bika ba, mugu kawai" rufe murfin kofar tayi da karfin gaske ayayinda shi kuma yake dariya, ba karamin dariya taba shi ba.

Motar Jafar nabiye dashi abaya, ganin ya tsaya shima ya tsaya, kallon Salma yayi yace "i guess ke yake jira"
Murmushi tayi, tana shirin bude kofar Junaina tabude afusace tace "malama saiki sauko mai guri tazo, sannan kuma awa biyu nabaki kidawo muyi exchange, kinsan Annah ba wasa, ban yadda tamin duka abanza"
Salma batace komai ba ta sauka, shiga motar Junaina tayi tana jan tsaki, bata rai Jafar yayi yace "idan kika sake tsaki zan ajiyeki nan nakoma gida kuma learn to respect your sister"
Okay, am sorry" Junai tafadi amaraice.

Motar Mujahid Salma ta shiga ta zauna, gani tayi sai fama murmusa wa yake, itama murmushin

tayi cikin sanyi voice tace "yaya whatx d good news?
Wani sexy look yakai mata, murya kasa kasa yace "muje miyu shopping daga nan sai muje mu gaishe da Aunty dinki, kwana biyu tana missing dina"
Kallon rashin fahimta tamai sannan tace "wace haka... ?
Bai kalleta ba yaja motar yace "Malamar ki mana, Faiza.."
Gabanta ne ya fada, murmushin da take dauke dashi ya koma bacin rai, "faiza" ta fadi aranta "Faiza dai, ko kin manta ta ? Ya fada jin ta kira sunan afili batare data sani ba.
Shuru tayi bata iya cemai kala ba, tunani tahau yi anya batayi kuskuren fadawa tarkon Mujahid ba, shida baya da lafiya ina ruwanshi da wata Faiza, kila ma shopping din ita zaai wa...surutai barkatai tahauyi azuciyanta.....
[9/7, 12:38 AM] Xarah Bukar: Zuma Sai Da Wuta

~na~
©χąraђ bųkar

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION (NWA)

Allahu akbar kulu'nafsi za'ikatu mauti, Allah yaji kanki da rahma Maman besty Yar ficika. May jannatul Firdausi be ur final destination.

*Wannan shafin naki ne ke daya Princess Sakhna (yar Gatan xarah bukar) thanx so much 4 ur love & support, Allah ya barmu tare, ILYSM*❤❤❤

ZSDW fans😘

60

Murmushin dole Salma tahau k'irk'iri kar ya gano wani abun dake zuciyar ta. Haka suka isa Sahad stores, abubuwan amfani masu kyau da tsada ya loda cikin lodoji sannan suka fito, ita dai Salma bata cemai k'ala ba suka zo shiga mota ta mak'e abakin kofar batare da niyyan shiga ba, alama yayi mata data shigo su tafi ta make kafada had'e da shagwab'e fuska, dariya ta bashi, ya zago gurinta had'e da bud'e mata k'ofar, k'in shiga tayi tace "nifa gida zan koma, bazan rakaka gurin taba" murya raunane tayi maganar.
Hannu ta ya riko, muryar kasa kasa yace "haba habibty malamar kice fah, ina laifin wanda ya karantar ka"
Turo baki tayi.
"ni ba abunda ta koyamin, mostly korata take a class, dan haka bazan je gidansu ta wulakantani ba"
"Toh ya kike so ayi yanzu, already na kirata awaya ina tafe.
Dadi ne yakama Salma jin sai yadda tace, daure fuska tayi tamau tace "muje gidan amma a

bakin gate zaku gaisa mu wuce"
Dariya yayi, ta shiga motar sannan ya zagaya ya shiga yaja zuwa gidan su Faiza. Awaya ya k'irata, ta fito ta iske shi waje, daganin Salma ta had'e rai, dukda ma Mujahid ya fad'imata Salma yar'uwa sa ce bai hanata jin haushin taba balle inta tuna yan daba dana aiko mata, ko kallon juna basu yiba ta k'arasa gefen da Mujahid ke zaune, sai wani yauki take mai tana mitar kwana biyu ya shareta, shikam lallaba ta yahau yi harta d'an hak'ura suka fara yar wasa da dariya, Iya k'uluwa Salma takai, wayarta sai ringing take takasa dauka tsabar takaici, sakon ne ya shigo nacewa "muna jiranku abakin gate" nanta gane Junaina ce, Gyaran Murya tayi had'e da kawar dakai gefe.
Kallon ta Mujahid yayi sannan ya maida dubansa ga Faiza yace "frndy ya samari, ko kuma dai nace ya bazawarai ?.
Annuri fuskar tace ta sauya, tahau wasa da yatsun hannuta, tace "tukun nadai"
Murmushi yayi ya d'auki ledar shopping din ya mika mata, yana fadin "gashi ama mai rabo kwalliya" cikin zolaya yayi maganar.
Harara tamai cikin wasa sannan ta amsa tace "niba wanda zanma kwalliya"
Magana zaiyi, Salma ta katse shi dacewa "yaya muje kunnena na ciwo"
Wani mugun kallo Faiza ta jefe ta dashi ganin yadda yayi saurin bata attention, ciki ciki tayi godiya ta wuce batare data jira abunda zaice ba. Idanuwan sa nakan Salma yanai mata sannu dukda ma dai yasan karya take, juyawan dazai yi yaga bata gurin, kallon tuhuma yama Salma sannan yaja motar sukayi gida.
Bakin gate suka had'e dasu Junaina nan sukayi canze, Jafar da Salma suka shige agidan atare, shi dariya ma abun ke bashi, Mujahid kam ko ajikinsa kota kan Junai bai biba suka shige gida, daganin su Annah tahau washe baki, aganinta sun daidaita kansu tunda taga sun jima da fita, albarka tahau shi masu tanai jinjina nutsuwa da hankalin Salma ganin yadda komai tace ayi Salma na mata biyyayya.

*****

Kwanaki sun ja, Soyyaya sosai Mujahid da Salma keyi babu wani ruwanshi da sa Idon Annah dukda ma dai Salma na kokarin kare kanta gurinta na nuna cewa ba ruwanta dashi, hakan kuwa ba karamin Dadi yama Annah ba aganinta dagaske Salma take, sau tarin yawa tafi bawa Junaina laifi akan bata kula Mujahid, ba kunya Junai kece mata ba sonshi take ba, dukda hakan Annah taki hakura ita adole zabinta kowa zaibi dan ta lura ma Jafar baya bi takan Salma, indai yana gida ta tare zata ganshi da Junaina, hakan na mugun b'ata mata rai.
Hajiya ma shuru bata dawo ba, akullum Annah saita kira tai mata albishirin yara sun daidaita kansu, da kuma yaushe zata dawo afara shirin buki, Hajiya dai jinta take tasan ba hakan bane, iya kaci tace mata ta kusa zuwa bada jimawa ba.

****

Gidan shuru kowa kwance dakinsa kasancewar ruwan da ake tafkawa tun bayan Magrib. Sanyi ne kadai ke ratsa ko ina, lamo Salma tayi cikin bargo tana lumshe idanu, hannu takai karkashin pilo tadauki wayarta ta duba lokaci, karfe goma da kwata na dare tagani . Murmushi tayi ta yunkuro zaune hade da dialing nambar Mom, sau biyu tayi ringing Mom ta dauka, idanta biyu, alokaci tana shirin shiga dakin Daddy, tana ganin call din Salma tasan bai wuce zancen Mujahid

ba wanda akullum sukayi waya saita mata zancen sa, ta rasa wana irin so Salma kema mugun yaron nan.
Gaisawa sukayi cike da fara'a, sannan Salma ta gangaro mata dacewa "Mom kin sanar da Daddy kuwa ?
Dariya Mom tayi.
"Yar gatan daddy kinsan duk abunda kikeso hakan zaai, amma are you sure he is the right man for you, nifah i dont like him"
Nisawa Salma tayi, kaman mai shirin kuka tace "haba Mom, wlh ya Mujahid nasona, bashi da matsala, trust me"
Mom tace "okay dear, dama Daddy yace na tambayeki tunda kinyi insisting sai shi, babu damuwa, your happiness is ours"
Farin ciki ne sosai yakamata Salma, sun jima suna hira daga bisani sukayi Sallama, sai sannan taga Miss call din Mujahid hudu ya kirata kusan mintin arba'in da suka wuce.
Da azama tayi dialing no dinsa ta jita akashe, mikewa tayi da sauri tana tunanin kilan wani abun yakeso takaimai ko kuma wani mugun abune yasame shi, cike da Fargaba ta fito daga dakin, jikinta sanye da sliky night wear riga da dogon wando ko dankwali babu kanta tayi saurin haurawa stairs, bata ma lura da Annah dake tsaye bakin kofar dakin Junaina ba. Mamakin ganin haurawan ta sama Annah tayi, kullum dare takan fito dan tabbatar da Yammatan kowanne  na dakinta sabod tsaro da kuma tarbiyan su, basu kadai ne agidan ba, shiyasa duk inda kake da yaran mata da baligi namiji a gida yazama dole kasanyan idanu saboda gudun shairin sheden dazai afko.
K'wafa Annah tayi ta juya dakinta dauko sandar ta.

Ahankali Salma ta tura k'ofar dakin ta shiga, can ta hango sa dunk'ule tsakiyar gadon kud'undine cikin bargo kansa kadai ke waje yana baccin sa hankalin kwance, ga wata sanyayyiyar kamshi dake tashi ta kowana lungu da tsakon d'akin. Karasawa tayi gefe gadon sannan ta kira Sunan sa ahankali, shuru bai amsa mata ba, tsoro ne yakamata kodai baya da lafia, rarrafawa tayi har tsakiyan gadon ta tsugunna daidai fuskar sa, hannu takai bisa goshinsa taji temperature dinsa is normal, ajiyar zuciya ta sauke ta zubawa kyakyawan fuskar sa idanu, murmushi tayi zata juya taji ya riko hannuta tafado jikinsa, cike da kid'ima ta kallesa,  gani tayi idanuwan sa bude yana mai mata wani irin kallo mai fizgar zuciyar wanda ake ma,  Saurin d'ago da jikinta tayi, suna kallon juna..
 Ganin tayi ya mika hannunsa zai taba jikinta tayi saurin rintse idanu, murmushi marar sauti ya saki, yasa hannu ya gawar da gashin kanta gefe daya zubo ya rufe rabin fuskar ta.
"Kin dauka na mutu ne ?
Ya fada cikin salon da bata taba ji garesa ba.
Bude ido tayi ta dubesa, murya shagwabe tace "naga miss call dinka"
Marairace fuska yayi yace "sanyi nakeji, i need your body to warm me up" karashe maganar yayi ya kuma janyo ta jikinsa.
Mintsini takai mai, tace "are you crazy ? Cikin salon wasa ta fad'i.
Dariya yayi yace "am crazy about you"
Chakwulkuli yahau yi mata, tahau rokonsa ya bari, wani mugun dariya ke cinta, kasa jure wa

tayi tadau karamin pilo tanai kaimai duka cikin salon kauna, tace "plz stop it..
Ganin ba bari xaiyi ba tahau kokarin sauka kan gadon da ya hargitse gaba daya, kowannan su dariya yake suka ji an bango kofar dakin da karfin gaske, atare sukayi surrender cike da tsoro.
Tsaye Annah tayi ranta na mugun tafasa da bacin rai, mugun kallon tama Salma tace "Miye hakan, nonuwa awaje, gashi a hargitse ?
Saurin karasa saukowa Salma tayi cike da kunya, adjusting hannun rigarta data zabulo kasa tahau yi.
Tsaki Mujahid yaja yace "waike Annah sa idon naki har dare ma kasuwa take ci"
Haushi ya kuma kamata, Salma kam tsuru tsuru tayi.
Annah tace "zakaci uwar kane, yarinyar mutane ka matse a daki, wayasan ma mikai mata, kaga yarinya shuru shuru".
Dariyar rainin wayo yayi yace  "ki tambayeta idan nina ce tazo"
Kallon ta Annah tayi tana jiran amsa, Salma kam ihu yarage bata yiba dan kunya, kuma abun haushi ma ita takawo kanta....bata ankara ba taji saukar Sandar Annah a ajikinta, kara marar sauri ta saki zabar azaba, da sauri Mujahid ya sauko kan gado ya amshe Sandar yaja Salma gefe, yace "Allah kuwa kika kara dukanta awaje zaki kwana".
Tafi Annah tayi tace "ubanka ma yayi kadan" nuna Salma tayi da hannu tace "keda nake yabonki Sallah ashe ko alwalar ma baki iya ba, nasan maganin ku, kafin ku b'arko abun kunya kwara na aurar daku cikin satin nan yan banza yaran kawai" warce Sandar tayi hannusa ta juya tafita.
Adan kidime ya kalli Salma yace "hope bata ji maki ciwo ba.?
Kai ta girgiza alamun a'a, sai kuma tace "yaya sandar akwai zafi ashe" kaman tayi kuka ta fadi hakan.
Sosai yaji tausayinta, dan kuwa yasan zafin sandar, zaunar da ita yayi kan gadon yace "am sorry, duk laifi na ne"
Murmushi tayi batace komai ba, sai kallan juna da suke, Annah ce ta kuma dawowa tana fadin "kina fitowa ko saina zo na kara maki ?
Da sauri ta mike, tace "Ya good nyt"
Kaman karta tafi yaji, lumshe ido yayi  yace "nyt dear, sleep tight"
Ficewa tayi da azama, yabi bayanta da kallo cike da tsatsan sonta, zuciyar sa sai kara tuna mai yake ya rama abunda tayimai kwanakin baya.
Labb'an sa nakasa ya ciza, sannan yace "i love you so much but dole nayi hurting dinki kema ki dandani azabar danasha" kwanciya yayi kan gandon yana tunanin hope he isn't making any mistake.

Saida Annah ta raka Salma har daki sannan takoma Palo tazauna tana huci, wayarta tadauka ta kira Hajiya, Hajiya kam duk ta tsorata ganin kira alokacin, tana dauka Annah tahau ta da Masifar akan lailai saita dawo gidan Gobe, dan kuwa cikin wani sati take so ayi aure tun kafin yaran Gidan su kasheta da bakin ciki.
Hajiya kam bata gane inda zance yado sa ba, saida Annah tayi mata bayanin abunda ya faru, Salati Hajiya tahau yi, tace bataga ta zama ba dawo wa gida yakamata.
[9/7, 12:38 AM] Xarah Bukar: Zuma Sai Da Wuta

~na~
©χaraɧ bųkar

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION {NWA}

Allahu akbar kulu'nafsi za'ikatu mauti, Allah yaji kanki da rahma Maman besty Yar ficika. May jannatul Firdausi be ur final destination.

61

Har wayewar garin Allah Annah bata bar jinini ba, ganin babu wanda ya tashi bacci a mutanan gidan yasa ta tusa Salma agaba akan lailai saita koma gidan su kafin ta janyo mata abun magana, ita kam dariya ma batun ya bata, had'a kayanta tayi cikin akwati ta fito, har waje bakin mota Annah ta tisa keyarta gaba tana kumfan baki, Salma kam ko ajikinta tafad'a mota Driver yaja maida ta gidansu. Ajiyar zuciya Annah ta sauke ta koma ciki tana magagganun ita d'aya kamar tab'abb'iya..

Salma na isa gida Momy taji dadin ganinta, dan kuwa ta jima da son dawowarta alkunya yasa kawai batai mata batun dawowa ba dan har Daddy taima zancen yace da ita karta manta Salma gidan yan'uwanta taje ba wani gurin ba.

Ta b'angaran Mujahid kuwa koda ya sauko kasa around 12 baiji duriyar Salma ba, sharewa yayi atunaninsa abunda ya faru jiya yahanata fitowa. Around 4 bayan ya dawo Masjid ne ya lura something is not right ganin yadda Annah kemai mugun kallon tana cika tanai batsewa, baibi takan taba ya leka dakin Hajiya, wayam yagani babu salma balle alamunta, ransa ne yabaci, atake ya ciro wayarsa daga aljihu ya kira Salma, dariya tayi dataga call din though she was expecting ya kira ta tun dazu, tana dauka yace kina ina ? Atakaice yayi maganar.
"Gidan mu" ta fada tanai cigaba da dariya, shikam haushi ma tabasa ya katse call din ya fito palo gurin Annah, fuska ba annuri yace "Annah miyasa Salma tabar gudan nan ba tare da izini nabaa ?
Harara ta watsa mai sannan ta d'auke kai tana fadin "Zancen kake so, wai ance da gwauro ya iyali"
Iya k'uluwa Mujahid yakai baima san mai kalamanta suke nufi ba, yace "bar ganin kin koreta kamar kinci galaba akanmu, ni yanzu gidan su zan nufa ganin ta, sai inga abunda kika isa yi" cike da karaji yayi maganar.
Dogon Tsaki Annah taja ta tab'e baki had'e da ware hannuwanta biyu, tace "Abu mai sau'ki, shan koko da matsami, kuje can ku karata badai agidan nan ba, idan kaga kuma ta dawo toh an shafa fatiha ne, jarababbun yaran kawai"
K'wafa Mujahid yayi ya fice waje afusace.

Salma tare da Momy a d'aki suna hirar su cike da annushuwa, Salma tace "Momy nikam ina ya Salim tunda na tafi bai kira niba ??

Tab'e baki Mony tayi tace "these dayx bansan maike damun saba, he is always indoors, dukya rame ba yadda banyi muje yaga Doctor ba yaki acewar sa kalau yake"
Jikin Salma ne yayi sanyi, sosai taji tausayinsa, ada bata da wani aboki sai Salim tanson shi sosai, halinsa kadai yasa take maintaining distance.
Wayarta ce tayi karar shigowar text, dubawa tayi tare da murmusa, kallon Momy tayi tace "sweetheart dina ya iso"
Dundu Momy takai mata tana fadin "marar kunya kawai" dariyar sukayi atare ta mike da azama taje dakin ta tadau veil tayafa akan doguwar rigarta sannan ta fita haraban gidan inda yake tsaye bakin motar sa, fuska murtuke.
Da fara'a ta karasa garesa, gaidasa tayi ya kuma tamke fuska ya dauke kai.
Rud'ewa Salma tayi, sam batason ganin one love dinta ahaka, kaman zatayi kuka ta shagwab'e murya da cewa, "yaya am sorry, wlh Annah ta tisa ni gaba shiyasa banma Sallama ba"
Sai sannan yakalle ta, cike da haushi yace "atleast you could have holla me on phone before leaving, bakiga yadda hankalina ya tashi da rashin ganin kiba"
Hakuri Salma tahau bashi shikam sai wani cin magani yake, dakyar tasamu ta lallaba shi haryayi dariya, hirar su mai cike da so da kauna suka hauyi daga bisani yaduba agogon hannu sa ganin lokaci, duban agogon Salma tayi hade da dariya tace "ya agogon nan yan nan ?
Murmushi yayi ya kalle ta yace "babu inda zaije tunda baki sace shiba"
Dariya ta kumayi tuna haduwar su ta biyu a club data zaremai agogon yabiyo ta ya kwace.
"Wlh i was only looking for your trouble ranar, amma yaya do you still smoke ?
Gyara tsayuwar sa yayi yanai kaimata wani shumin kallo sannan yace "har yanxu kina zuwa Club ?
Harara takai mai cikin salon wasa, bata bashi amsa ba tace "yaya inason agogon nan, ban taba ganin irin saba"
Kallan sliver agogon yayi yace "ba normal agogo bane, but i cnt tell you kona miye"
Ashagwabe tace "yaya kabani plz, inason agogon"
Dariya tabashi da yadda tayi maganar, zai iya bata amma yana tsoron karta batar mai dashi.
Cire ogogon yayi ya rike hannuta yace "promise baza kibari asace ba"
Kada kai tayi cike dajin dadi, yace "aro nabaki fa"
Kai ta kuma d'agawa cike dajin dadin, sakala mata yayi a hannu tana shakar kamshin sa dake fita daga agogon, sosai tajita cikin farin ciki sun kara jimawa agurin daga bisani sukayi sallama yabar gidan.

Bangaran Salim Salma ta nufa ta iske shi yashe kasan tsakiyar palo, da ganin baya cikin hayyacin sa, karewa ko ina kallo tayi komai kaca kaca, ga uban emty bottles na barasa, gabadaya ya gama muzanta. Ranta ne ya baci ta tsugunna gabansa inda yake kwance, afusace tahau kiran sunan sa, bude idanuwasan da suka sauya launi zuja yayi ya sauke su akanta, adan zabure ya mike zaune atunanin sa ko imagination dayasaba yine.
Fuska daure tace "Ya Salim miye haka, why are you trying to useless your life ?
Sauri riko hannuta yayi tabi gemai hannun da karfin gaske tana hararar sa, murya raunane yace "Salma yazanyi da sonki, duk yadda kika ganni da kuma duk abunda nake Sonki ne Sanadi (littafin Jiddah Aliyu)  na rasa ya zanyi da rayuwa ta" kuka ne ya kufce masa hade da sauri rungumarta, Haushi ne ya turnuketa ta turesa daga jikinta ta mike tsaye tanai mai mugun kallo

tace "ya salim kabar bata lokacin ka akaina, cox i dont love you, tayama xaai na soka jibeka so useless and irresponsible, the only gentleman i love is your Boss, get that in your dummy brain" ahasale ta karasa maganar, shikam kuka yaci gaba, tsaki taja tahau gyara ko ina na gurin sannan ta fita ta barshi cike da tausayin so maso wani dayake mata.

*****

Washe gari ne Hajiya ta dawo gida da yan'uwa birjit na fara shirin buki. Annah kam baki har kunne zata aurar da jikoki, sunyi magana dasu Daddy an tsayar da rana one week kacal.

Su Junaina kam sai sabon iyayi daya karu an kusa shiga daga ciki, sosai take jin dadin yadda Jafar yake nuna mata so da kulawa, itama baa barta baya ba dama gashi ta iya shishigi da ladabi a soyayyan shiyasa sukafi dacewa da juna.
Su Oga Mujahid da Salma baa magana soyayyan sosai suke ba kama hannu yaro, wataran har Mamaki Hajiya take da irin son da Mujahid yakema Salma dan kuwa bata zata ba..

Daddy ne ya amshe zamewa Salma da Junai Uba game da komai na auren, kafin satin auran sukaje Dubai yin siyayyan abubuwan amfani masu shegu tsada sannan suka dawo.

Satin Buki.

Gidan su Momy ya cika sosai da jamaa, yan'uwanta ma sunyi kara sunzo saboda son datake ma Salma, wasu yan'uwan Salma na dangin uwa duk can suka sauka, masu gyaran jiki irin irin kusan goma Hajiya ta aiko suke gyara Salma anan gidan, Junai ma acan gidansu gyara sosai ake mata, saidai har yanxu ba wani shiri suke da Salma ba.. Event ma da suka hade kin Amincewa Junai tayi suyi tare cewa tayi kowa yayi nasa daban a inda yakeso, hakan Sosai yabawa Hajiya haushi sharewa kawai tayi ta barta ahanka, mazan ma baa barsu baya ba sai nasu shirin suke.

Three Dayx to Daurin aure, kuma gobe ne zaai event din Arabian night.
Su salma ansha murja dakayan Dilka da turaran kamshi, duk inda ta ratsa shining take da kamshi, tayi kyau sosai, kayan tsumuwa na mata (Aunty Guarantee) ba wanda baa bata tasha ba, na cushe cushe ne fir taki amincewa dasu dan bata yadda dasu ba majority ma ovary cancer suke sanyawa.

Around 8 na dare ta fito wanka sai kyalli skin dinta yake, zama tayi gaban mirror ta murje jikinta da turaruka masu dama  sannan ta sanya night wear riga da wando cotton ta kwanta, agogon mujahid dake kan side drawer tadau tana shakar kamshinsa sannan ta makala a hannuta.
kaman jira take taji wayarta na ringing, da azama tadau ka ganin wanda ke kira.
Daga can bangaran yace "Angel am dieing" cikin wata irin salo mai rikitarwa yayi maganar.
Adan rude ta mike zaune "My love you're killing me, plz talk to me, miyasa meka ?
Lumshe ido yayi "am sick, cronic ciwon kai ke damuna"..
"OmG" ta fada adan kidime, ta mike tsaye.

Tace "yaya kana ina
Murya wahale Yace "ina gida, apart din Baki".
Ajiyar zuciya ta sauke tace "yaya plz stay calm, i cnt sleep idan banzo naga condition dinka ba, am coming right away" katse wayan tayi da sauri ta suri Hijab dinta tadau mukullin mota ta fita dakin, mutane sosai tagani palo anata hira, ta kitchen tabi ta fita waje batare da kowa yaganta ba. Mota ta shiga taja tabar gidan at 360.

Dariya sosai Mujahid yayi bayan sun gama wayan, zaune yake shida wasu cousin dinsa guda biyu a palon bak'i, duk wayar da yayi da Salma a speaker yasan ya suka ji komai.
Dayan mai suna Khaleel yace "Mjay kaci saa yarinyar nan na bala'in sonka, jifa yadda ta rud'e, dama nice nasamu Babe haka" dariya sosai yake yana maganar.
Murmushi Mujahid yayi yace "nima ina bala'in sonta, i cnt live without her, she is my everything but some scores have to be settle, Salma ta mugun wahalar dani ba kadan ba"
Harara Dayan mai Suna Abdul yamai yace "miye amfanin settling scores tunda nan da 3 dayx she is all yours, koma dai miye ka barta kawai"
Mujahid yace "aiko mi nayi mata bazata ji haushi na ba, she is madly inlove with me"
Dariya Khaleel yace "babaa wai wana irin wahala kake nufi tabaka?
Mikewa Mujahid yayi yace ina zuwa" fita yayi can bakin gate yayi magana da mai gadi sannan kuma ya dawo palon ya zauna. Labarin tun farkon haduwan su da Salma yafara basu, jifa jifa kuma yakan kalli wayarsa.

Salma na isowa Gidan wani mugun Horn tahau yi, da sauri mai gadi ya bude mata ta cilla motar ciki da sauri tayi parking ta fito... Sauri sauri, gudu gudu tayi tafara karasawa part din Baki dake can nesa da main house, takusa daf da gurin taji ana kyalkyalewa da dariya, tsoro ne yakamata tafara takawa da sauri, daidai bakin Kofar taji Muryar Mujahid na magana cikin dariya, gabanta ne ya fadi ta daskare gurin ba tare data iya kwakwaran motsi ba.

Cikin dariya Mujahid yace "kasan most funniest part of the story, bayan munyi plan da abokina nayi kissing dinta still bata bada kai ba, saida nayi fooling dinta na aika wasu Maza sukamin Duka atiti sannan fah ta waiwayeni"
Khaleel yace "gaskia kayi fooling dinta dayawa, ni yaushe zan yadda nasha duka abanza"
Mujahid yace "bayan ta fara kulani i had to pretend loving her duk dan na shuka mata rashin mutunci, kuma nasan itace same Ummi da Hajiya ta isheni saina nemo, niku kuwa na share naki nunawa Hajiya nasan wata Ummi. The next tin kawai naganta a gidan nan, kasan kuma miya faru ?
Haushi ne yakama Abdul, Khaleel kam dama player ne, kuma dadin labarin yake ji yace "what next ?
Mujahid yace "Could you imagine, yarinyar nan tasamin attarugu a shower gel dina, nikuma arashin sani nayi using, ranar ko i felt like strangling her to death"
Dariya sosai Khaleel yakeyi, abu sai kace a film, yace "Mjay gaskia ka wahalu, ya kayi kuma?
K'wafa Mujahid yayi yace "ya kuwa nayi, fooling dinta bashi da wuya, tricking dinta nayi into biliving ina sonta, ita kuma tayi saurin bada kai as usual .."
Khaleel yace "amma fa Salma ta hadu, koba laifi zaka huta da jikinta.."

Kaaa cigaba da Sauraro Salma tayi, hannu tasa kan kunnuwan ta tana fadin "innalillahi wa Inna'ilaihi rajun" hawayan Bakin Ciki data jima basu zubo mata ba suka hau ambaliya a fuskar ta, kuka sosai take tafara ja dabaya tayi tuntube tafadi kasa, ihu ta saki cike da tashin hankali.

Jin ihun Salma yasa Mujahid mikewa akidime ya fito waje, ganinta yayi zaune kasa tana rusa kukan daya jima yanason Ganin hawayanta. Da sauri ya karasa gareta yana fadin "Habibty yaushe kika zo ?

Wani sabon kuka tafashe dashi, jin sabon yaudarar dayake shirin yi mata, mikewa tayi tsaye tana kallon yadda duk ya gigice, rikota yayi cike da kulawa, wani irin feeling yaji ya ratsa jikinsa, ga kamshi jikinta sai ratsa mai gabobin jikinsa yake gabadaya.

Murya kasa kasa yace "sweetheart mi aka mike, plz stop crying, your tears are breaking my heart" janyota yayi zai rungumeta tasa hannu da karfi ta turesa baya.

Cikin kuka ta nuna shi da yatsa tace "dont you dare lay your filthy hands on my body, banza macuci, dan iskA, Allah ya isa tsakani na dakai, i hate you..", kuka sosai ya kufce mata, rike kanta tayi dake mugun sara mata lokaci gudu.

Hankalin Mujahid ne yatashi baiyi tunanin Salma zata dau komai da zafi ba ayadda takeson shi.

Matsowa yayi kusa da ita tayi saurin ja baya, kaman zaiyi kuka yace "plz forgive me, i was only joking, nasan kinji komai wlh ina sonki Salma"

Wani mugun tsanan shine taji ya diru azuciyan ta, she has never been humiliated like this in her life, kuka sosai take cike da tausayin kanta, tarasa miyasa Mutane biyu nan Abbanta da Mujahid datafiso arayuwan ta suka fi kowa kuntata mata. Innalilahi kawai take ambata aranta.

Kallon shi tayi tace "ko kana sona ko baka sona i dont give a fucking damm about it, cox ko kaine autan maza na hakura dakai, na gwamma ce na kashe kaina akan na aureka balle na zauna dakai" sautin kukan tane ya karu ta juya da gudu ta koma gurin motar ta, binta yayi shima da gudu yana kiranta, bata saurare sa tashige motar taja ta wuce ta gabansa wanda kiris ya rage bata kwashe saba, bai damu ba yabi motar da gudu amma tuni ta fice daga gate din.

Hannu Mujahid ya daura akai cike da tashin hankali yace "Am died...

Muryan Abdul yaji abayan shi yace "in life you rather learn leason the easy way or the hard way, da dukkan alamun i don't think she will ever accept you back".

Kuka Mujahid yahau yi cike da haushi abunda ya shirya dan rama abunda tamai, gashi komai ya fado kanshi.

[9/7, 12:38 AM] Xarah Bukar: Zuma Sai Da Wuta

~na~

©χaraɧ bųkar

(Aunty Cute)

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION {NWA}

Allahu akbar kulu'nafsi za'ikatu mauti, Allah yaji kanki da rahma Maman besty Yar ficika. May jannatul Firdausi be ur final destination.

63

Daran ranar Mujahid bai samu rintsawar arziki ba, ta b'angaran Salma kuwa bata san duniyar da take ciki ba, Salim kam yafi kowa farin ciki ranar, kodaya koma gida kwanciyar sa yayi yana hagon yadda rayuwarsa zata kasance tare da abun kaunar sa.

Washe gari babu wanda ya lura da Salma bata gidan, sai kuwan azahar da Kulchumi mai gyara mata jiki ta shiga dakinta yi mata wanka turare, wayam tagani babu alamun Salma tayi kwanan dakin, bandakin ta leka bata nan ta fice da azama ta fad'i ma Momy rashin ganinta. Ran Momy ne yabaci, shiga d'akin tayi dan tabbatar da zancen kulchumi, mamakine ya kamata gasgata zancen, da sauri tahau kiran nambar salma da wayar dake hannuta, ringing take bamu mai dauka.
Fitowa tayi waje ta hangi motar Salma a parke, mamakone ya kuma kamata toh ina salma ta shiga by this tym, karasawa tayi bakin motar hade da lekawa ciki ta hangi wayar Salma ajiye kan seat, bude motar tayi tadau wayar hade da duba dawa tayi waya last, sunan Mujahid tagani, ranta ne ya kuma b'acci, atunanin ta ko Salma na gidan su Mujahid, afusace ta koma cikin gida, batare da bata lokaci ba ta kira wasu yan'uwanta uku suka shiga mota zuwa gidan Hajiya.

Mujahid kam duk ya figi dare daya, tun yana jiran Salma tadau kiran wayarsa harya saduda ya zubawa wayarsa ido karshe yanke zuwa gidan su yayi Abdul ya hanashi da cewa ba lailai ne ta saurare shi balle yanzu da gidan ke cike ana hidimar buki, kumai ai Salma bata fasa auran saba tunda har yanzu basu ji bayanin komai daga bakin hajiya ba. Da wannan kalaman Mujahid yadan ji sanyi aranshi.

Annah baki har kunne, Jallabiyo yi ne matsu tsada gabanta tana zaban nasawa yau adaran Arabian nights, dakin makil yake da wasu yan jikokonta da yan'uwan ta, sai zolayar ta suke tana masu tsiya, Hajiya ce ta shigo dakin adan birkice taja Annah suka fito haraban gida kasancewar ciki makil yake da bak'i yan buki.
Cike da kidima Momy tace "Annah kinga Salma gidan nan ?
Tsaki Annah taja tace "dalilin katsamin jin dadi kenan.
Mom tace "yanzu momyta ta kirani ta tambaye ni, nace mata bata nan, da alamun kuma ba lafiya ba"
Gaban Annah na yafadi, aranta fadi take "sabon tuggu kuma yaran nan suka kulla dan karna rakashe abukin nan, toh wlh baku isa ba"
Magana zatayi sukaga an bude gate motar su Momy ya shiga da gudu, parking tayi duk suka sauko fuskar su dauke da kunci.
Babu ko gaisuwa Momy ta dubi Hajiya tace "kun mamaki wlh, a tunanin na Salma bata da wata uwa data wuce ni shine zaku rabani da ita sannan kuma kice min ke baki ganta ba, kuma ni nasan tana gidan nan"

Tashin hankali ne ya mamaye Hajiya, nanta hau kokarin fahimtar Momy da kwatakwata ta kasa gamsu wa da kalaman ta, Annah kam binsu tayi da ido tana tunanin indai dagaske Salma guduwa tayi ko sace ta akayi ba lailane ayi buki budiri ba, itakam bazan lamunci a bata mata bojet ba ayadda ta shirya juya mazauni wanga bukin. Kamar an tsikareta ta fashe da kuka hade da daura Hannu akai, duban ta su Momy sukayi adan tsorace.
Cikin kuka Annah tace "Kuyi hakuri duk laifi na na, nice na tura Salma Kano amso min may an in ciwon idona, batayi niyyan zuwa ba saida nace idan bata jeba zan hanata auran Mujahid, ba shiri ta kama hanya batare da bata lokaci ba" kuka sosai Annah ta kara fashewa dashi.
Ran Momy ya gama bacci, kasa magana tayi ta juya tace da yan'uwanta su tafi, yaukam taga matsayin ta gurin Salma da danginta.
Kirata Hajiya tayi ko kallan ta batai ba suka shiga mota yaja. Takaici ne yakamata Hajiya ta dubi Annah da har yanzu kuka take, kasa ce mata uffan tayi ta koma cikin gidan. Dariya Annah tayi tare da debo rawan shoki tana fadin "yo ina dalili kura da daukan kayan kare dashan bugu, ai baima yuyuwa ne dan ita baa ganta ba nasan halin hajiya sarai sai afasa bukin".

Da bacin rai su Momy suka komo Gida, gurin Daddy ta nufa ta tsara mai abunda ke faruwa, shikam baidau komai da zafi ba yace ba komai karta damu aci gabata kudanar da buki, inayaso ranar da Salman ta dawo shi yasan yadda zai nuna mata rashin kyautawar sanar dasu da batayi ba.
Jiki sabule Momy ta amince da hakan, ba yadda ta ita tunda shi daya kawo Salman ma baiji haushi ba.

****
Da daddare aka fara shirin Arabian night, su Mujahid kam suna zaune tare dasu Abdul harda Mubarak ba yazo, hirar su suke basu da damuwa banda Mujahid dayayi sukuku dashi, yasan ko karan hauka ne ya cize Salma bazata fito arabian nights ba, wayarta ya kuma latsawa kira tana ringing ba'a dauka ba, babban matsalan shi ma yarasa wa zai tunkara da maganar dan yasan duk wanda yaji maganar a iyayen saidai kuwa afasa auran..wata zuciyar tace miye zaka damu tunda kaji shuru kila ta hakura ayi auran, murmushi yayi zuciyar sa nagasgata masa hakan.

Arabian nyt kam yayi shagali da maana, su Junaina da Jafar ansha kyau, jamaa sai tambayan Salma suke ba kunya Annah ke dankaro karya, hajiya kam ba wata walwala tattare da ita, sam bataji dadin Abunda Annah tayi ba, ganin Mujahid bai tunkareta da zancen ba yasa bata cemai komai ba, shikam gogan baisan da wata tafiyar Salma Kano ba.

****
Bayan Kwana Biu.

Tun Ranar da Salim yakai Salma Gidan bai kara komawa ba gudun kar a zargeshi, saidai yadda yaga anata cigaba da hidimar buki yasa shi mamaki, dabara yayi ya kira momy yace zai karbi mukulli mota a hannun Salma, ita kam bata kawo komai aranta ba tacemai Salma na Kano.
Dadi yaji yafara kiciniyar hada mata passport dan guduwa da ita Ghana.

Tsoron Allah ne yakama Annah bayan an gama shagalgulan Buki, daurin aure ne kadai ya rage daza ai gobe, kullum tambayar ta ake ya labarin salma saidai tace mai magani bai gama hada magani ba, Hajiya kam taso tagano Annah karya take saidai rashin damuwan mujahid yasa tayi tunanin bakin su daya, da Yamma Annah ta fita zuwa bangaran dasu Mujahid suke, gabanta sa faduwa yake tana tsoron rashin Mutuncin zai mata, ta window ta hango su zaune da abokai suna ta hirar su tare dashi kaman babu abunda yafaru, tace "kai Mujahid fito muyi magana"
Dafe kai yayi cike da takaicin mai matan nan takeso, fitowa yayi yanai aika mata mugun kallo.
Kamar munafuka ta sinne kai tace "dama batun Salma ne, baa ganta ba nace nina aiketa kano dan kar acinye min shagali, yanzu kuma naga buduri ya k'are yasa na gayama"
Agigice yake kallon ta dan kuwa bai gane inda zancen ta ya dosa ba, "wana kano taje, bata gida ne? Ya jaho mata tambayoyin.
Tsurewa tayi tace "bansani ba, kaje ka nemo ta"
Zare ido yayi in shock yace "Annah ina take ?.
Kara tsurewa tayi tace bansani ba, bata jira cewar saba ta rugu gida da gudun dani kaina bansan yar tsohuwa ta iya ba.
Innalillahi Mujahid ke ambata, bai koma palon ba ya rugu gurin motar sa yabude ya shiga, mukullin na jiki ya kunna yaja yabar gidan.

Salma bata farka ba sai washegarin daya kaita da daddare, juyi tayi taji ta tim tafado kasan, arazane ta bude ido, wani mugun ciwon kai ke dawainiya da ita, dakyar ta mike tsaye tana karewa dakin kallo, kasa gane dakin tayi ta dafe hannu jikin bango ta fito palon, tsoro ne yakamata bata gane komai na gidan ba, wani mugun jiri taji ta fadi kasa sai bacci.
Saida tayi kusan 4 hours a gurin sannan ta kuma farkawa, so take ta tuna wasu abu amma takasa, data fara kokarin tunanin saita yanki jiki ta fadi sai bacci.
The next day ne ta kuma farkawa, da sauri ta mike koma toilet din dakin, ruwa ta kunna tasha sannan ta kirkiro wa kanta amai, saida tayi amai sosai sannan ta dawo hayyacin ta abubuwa suka dawo mata, ya Salim ta fara ayyanawa aranta, wana mugun magani ne haka yabata daga ciwon kai, ita bataji saukin ciwo ba sai hallaka da magani yasoyi, tasan kuma shi kawo ta gidan, ranta ne ta baci ta mike wani jiri ya kuma dibarta, saurin dafe bango tayi, ga wata uwar yunwa nacinta, adaddafe ta fito kofar palo taji kofar a rufe kasa jure tsayuwa tayi ta rarrafa zuwa kitchen, komai na abinci akwai, tea na ruwan sanyi kadai ta iya hadawa tasha ta kuma rararfa zuwa dakin.
Sai sannan tahau neman wayarta ta tuna a mota ta barta, kwaciya tayi akasa tana tuna Betrayal din Mujahid bata sanda kuka ya kufce mata ba, agogon shi dake hannuta ta duba taga karfe biyar na yamma. Mikewa tayi ta koma toilet, dakyar ta iya watsa ruwa tayo alwala tamai da night wear din jikinta da hijab dinta tahau rama sallolin dabata yiba. Bayan ta ida ne kuma wani mugun baccin ya kuma sace ta.

Parking Salim yayi a haraban gidan ya fito rike da ledan abinci daya kawo mata, ahankali yasa mukulli ya bude kofar sannan ya shiga, kasa ya ganta kwance a dakin ta kudundune cikin Hijab, Murmushi yayi aranshi yace wato tayi kokarin yaki da maganin.

Sunan ta ya kira ta bude ido ahankali ta kallesa, bakin magana kawai take dashi amma babu wani karfi  Tattare da ita.
"my love kin tashi" ya fada yana shafan fuskar ta, murya sanyaye tace "yaya why, miyasa zaka kawonin nan ?
Murmushi yayi ya dagota zaune suna fuskan tar juna, yace "Salma ina matuka sonki, bazan iya hakura ki auri mujahid ba, cox nafishi sonki"
Dakyar ta iya sakar mai harara, tace "miyasa kace ka fini sonshi
"Salma biliv me, akwai certain time danayi confronting mujahid akan ki nace mai kin zubar da cikina, inda yana sonki dagaske bazai nemi wulakanta ki ba harya yayi kokarin daura miki kisan daba ke kika aikata ba"
Kallon mamaki Salma tamai dajin shairin da yayi mata, amma toh yaushe akayi hakan Mujahid bai taba gayamata ba, wata zuciyar tace ba sonki yake ba tayaya zai gayamaki, Ajiyar zuciya ta sauke, tana son Mujahid bazata bari Salim ya nemi aibata saba.
Bata rai tayi tace "wanda kema son gaskia baya binka da shairi, no matter how bad Ya Mujahid yayi treating dina i still love him, kaga tashi ni kamaida ni gida"
Daura fuska Salim yayi yace "keda gida har abada, you're mine, Ghana zamu tafi gobe"
Mugun kallo tamai sannan ta mike tsaye da kyar tace "you're crazy, no wonder kayi drugging dina dan ka gudu dani, toh wlh baka isa ba" afusace tayi maganar, wucewa zatayi gefensa ya fizgo ta tafada cikinsa, matse ta yayi gam yana shakar kamshi jikinta, batasan sanda wani karfi yazo mata tasa hannu ta turesa hade da kai masa kyakyawan mari.

Kallon mamaki yayi mata sai kuma ya kwashe da dariya uwa tababbe, hannu yasa cikin aljihun sa yadauki wasu kwayoyi gudu biyar ya watsa a bakin sannan ta kalleta
"Ni kika mara ?
Harara takai mai.
"Dont you dare touch me, banza marar hankali"
Murmushi yayi hade da lasar labb'an bakin sa, ya karasa daf da ita ya  shako wuyanta tare da hijab dinta, zare idanuwa tayi da already sun canza launi, magana take sonyi takasa tsananin yadda taga ya koma mata uwa zaki, harshen sa yakai kan fuskar ta yana lasa, da sauri tasa k'afarta ta ture sa hade da matsawa, yawu ta hada abakin sannan ta tofa mai a fuska tace,
 "wanna ba so bane, rashin hankali ne" akufule yace ni kika tofawa yawu ?" Ba tsoro tace "eh kai din, niba kare bace da zaka na lasar min fuska."

Haushi da takaici ya cika sa, ya tako gabanta tare da bata k'akk'aywan mari guda biyu a fuska, ihu ta sakani dan azaba, bakinta ya fashe yana zubda jini, yace "zan nuna miki kare ya fiki daraja"
Daukar ta yayi tsam ya wurga ta kan gado.

Ihu take tana kiciniyar kwace kanta, shikam ko kallon baiyi ya yage wuyan hijab din ya cire, danne mata hannuwa yayi yahau kai mata kisses ta ko ina ajikinta, kuka tasoma tana rokansa, bai saurareta ba yahau kiciniyar cire mata riga, ringing din wayarsa a aljihu ne ya katse mai

hanzari dubawa yayi yaga Mom ce, gabansa ne ya fadi yayi saurin dagawa daga jikinta, itakam Salma kuka take, kallon ta yayi duk ta firgice, yace "zanje na dawo inci gaba daga inda na tsaya"
Sauka yayi kan gadon tayi saurin rikosa "yaya kayi hakuri, na yadda zan auraka, dan Allah karka cuci rayuwata, ka kaini gida plz"
Yace "saboda kin raina ni ko, na maida ki gida dan ki auri wacen banza ko ?
Kai ta girgiza, tsaki yaja ya tureta da karfin gaske har tana bugewa da gadon, yayi gaba ya fice yabarta nan dafe da kanta.

Gidan su Salma Mujahid ya nufa, dakyar ya iya samun ganin Mom a haraban gidan saboda yawan mutanen dake cikin gidan, fuska daure tamai iso saboda haushin su Hajiya da Annah da takeji.
Hankali tashe yahau tambayar ta ko Salma na gidan, ranta ne yakuma bacci da sabon rainin wayon da takeji, banza tayi dashi saida yace mata Annah tacemai batasan Inda Salma take ba sannan Mom ta saurare shi, mamaki ne yakamasu, Mom ta kwalla kiran maigadi ta tambayase ko yaga fitar Salma, yace tunda ta dawo baiga fitar taba. Hakalin sune ya kara tashi Mom ta kira Salim awaya, koda ya iso tsaye yaga Mujahid da Mom akidemi, cike da tashin sense Mom ta tambayashi koya ga Salma, ware ido yayi kamar gaske yace bai ganta. Salati Mom tahauyi. Mujahid kam kallon banxa ya aikawa Salim dan kuwa bai yadda dashi ba, karasawa kusa dashi yayi da niyyan mai magana yaji kamshi Salma ya ajikinsa, kaman jira yake ya damko wuyan sa, cikin huci da haushi yace "ina ka kaimin Salma ?
Bata rai salim yayi ya turesa, Mujahid yakai mai naushi, nan dambe ya chakwade, Hankalin Mom ne yatashi gudu kar yan ciki su fito, mai gadi ta kuma kwallawa kira, yazo ya shiga tsakanin su dakyar.
Saurin jan Salim tayi gefe ta kalli Mujahid, tace "yanzu ba lokacin fada bane, nemo inda ta shiga yakama ta kayi, tun kafin Daddy yasan cewa b'ata tayi, kuma kai kasan Hajiyar ku bazata so jin wannan mugun labari ba, duk inda aka shiga kaine main suspect saboda dakai tayi waya last kafin na nemeta na rasa" tana gama maganar taja Salim sukabar gurin tanai bashi hakuri.
Fuzgar da Iska Mujahid yayi ya juya ya fice daga gidan ya tsaya nan waje bakin motar sa, yasan cewa indai Salma is missing bashi da haufin cewa babu hannu Salim ciki, amma yazai yi bashi da evidence da zaa yadda dashi, duk Annah ta kara wuta cikin lamarin, inda tun asali batai karya ba da tuni ya binciko inda Salma take.
Haushi ne yakamasa baima san ta ina zai fara ba, wayarsa ya ciro a aljihu ya kira Mubarak, sun jima suna waya sannan ya katse ya shiga motar sa yaja yabar gurin.

Masoyana kuyi hakuri da typing din yau sai ahankali...bana jin dadin jikina kwana biu, yanxu haka am on medication.
[9/7, 12:38 AM] Xarah Bukar: Zuma Sai Da Wuta

~na~
©χarаɧ bųkaɾ

62

Gabad'aya Mujahid ya gama birkicewa, cike da kid'ima yahau laluban mukullin motar sa dake aljihun wandon sa.
Saurin rik'osa Abdul yayi yace,
"kabar tayar da hankalin ka, koka nufeta ba sauraran ka zatayi ba ayadda ka mugun b'ata mata rai"
Dafe kai Mujahid yayi cike da tsantsan tashin hankali, duban Abdul yayi da rinannun idanuwan sa da suka sauya launi zuwa ja.
"Ya kakeso nayi, dole naje na fahimtar da ita".
Hannu Abdul ya daura bisa kafadar sa.
"ka bari ba yanzu ba, she need some time"
Shuru Mujahid yayi batare daya iya cewa uffan ba, sun d'an jima nan tsaye kaman sanduna daga bisani suka koma ciki. Wayarsa dake ajiye kan kujerar palon yadauka ya kira Salma, saidai ba bugun duniyar dabai yiba fir taki dauka.

Akan titi kuwa wuta sosai Salma take bawa motar ayayinda take zubar da hawayan bak'in ciki, dakyar ta iya karaso da kanta gida, Afusace ta bude motar ta fito batare da ta tsaya bi takan wayarta ba, wani mugun juwa da azababban ciwon kai ke barazanar barar da gabobin jikinta. Adaddafe tafara takawa zuwa bangaran Salim wanda ayanzu ta tabbatar shi daya ke mata son gaskia, sab'anin da datake mai kallon wawa, soko marar hankali, yaudai gashi wanda take ma kallon zinare yazame mata bak'in gwarwashi.
Kuka take sosai ta k'usa kai cikin palon, kwance ta iske shi bisa doguwar kujera duk jikinsa mace, da alamun ma cikin zufin tunanin yake, sunansa ta kira cikin sheshek'a tare da fad'awa jikinsa, Atsorace ya dagota ya yunkuro zaune yana kallon ta, duk ta gama birkice sa da kamshin jikinta, tunda suke gidan bai taba ganin ta cikin mugun yanayi aka ba.
Cike da firgita yahau tambayan ba'isin kukan ta, kasa magana tayi saima sautin kukan ta daya tsanan ta, hankalin Salim ne yatashi, dakyar ta iya cewa
"Yaya kaina ke ciwo"
Janyota yayi ta kwanta bisa kirjinsa yanai mata sannu hade da bubbuga mata baya cike da lallami, sosai yaji dadin yadda suke makale da juya, aransa sai aiyanawa yake dama tazo mai yanzu yakamata ya mayar da Salma tashi ta har abada.

Salma kam kukan ta take, ko tuna abunda ya faru bata sanyi, yadda zata gayawa Daddy ta fasa auran Mujahid kadai ne matsalan ta, tunda tun farko ita tace tagani tanaso bawai tursasa ta akayi ba.
Dagota yayi ahankali ya jingine ta jikin kujerar, cikin sanyi murya yace
"bari nadauko miki maganin ciwon kan"

Kai kawai ta daga mai, ya wuce dakin sa, side drawer ya bude ya dauko wani magani dani kaina bansan na miye ba sannan ya fito yadauki bottle water dake ajiye center table ya karasa gareta..
Salma kam bata kaunar magani, dakyar da lallami ta yadda tasha pills guda biyu daya dauko, ubansa tayi ido jajir tace, "nagode"
Aranta kuwa danasani take dama tun farko shi ta baiwa soyayyan ta, koda yake bai baci ba zata fadi ma Daddy shi takeson aura ba Mujahid ba. Shingid'e kanta tayi kan kujerar, Murmushi Salim yayi yahau goge mata hawayan fuskar ta, bayan kaman minti biyar tafara ji nauyin jiki da kasala, mikewa tayi tace
"yaya sai da safe"
Yace "Allah ya kaimu" aranshi kuwa yace keda ganin safiya badai a gidan nan ba.
Taku tafarayi ahankali taji mugun hajijiya, abubuwan dake palon biyu uku tafara ganin su, bata aune ba taji ta ta fadi kasa wanwas.

Farin cike ne yakama Salim, mikewa yayi ya tako inda take ya tsugunna yanai mata shuumin kallo sannan ya mike ya leka waje ta window, shuru babu kowa, daukar ta yayi suka fito haraban gidan ya nufi inda motarsa ya bude yasata sannan ya shiga yaja yabar gidan @ 360...
Ba zaice ko ina ba sai Badoo Quarter, agaban wani gidan mai kyau madaidai ci yayi parking ya fito ya kuma daukar ta suka shiga ciki, palon mai shima mai kyau yasha kayan alatu, dakin ya bude yashiga ya ajiyeta kan gado sannan ya fito ahankali ya kulle gidan, Ajiyar zuciya ya sauke ya koma motar sa yaja ya koma gida.
[9/7, 12:38 AM] Xarah Bukar: Zuma Sai Da Wuta

~na~
©χaraђ bųkar
(Aunty Cute)

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION {NWA}

Allahu akbar kulu'nafsi za'ikatu mauti, Allah yaji kanki da rahma Maman besty Yar ficika. May jannatul Firdausi be ur final destination.

64

Kuka sosai Salma take yi, duk yadda taso fita gidan kasawa tayi kasancewar duk kofofin tamke suke da mukulli, ganin ba sarki sai Allah yasa ta lallashi kanta tadau abuncin daya kawo taci ta kwanta nan kasan dakin cike da tausayin kanta. Salim kuwa ganin yadda Mom bata zarge shi da komai ba yasashi samun karfin gwiwa, dakinsa ya nufa ya shirya kayansa tsaf cikin akwati cike da murnan gobe zai fece zuwa kasar Ghana da salma koda kuwa baa fasa daura mata aure da wanda yafi tsana a duniya ba, shine kawai ya gudu da Salma shine muradin sa.

Gida Mujahid ya nufa duk jiki amace, tunanin yake da amincewar ta tabar gidan tabi salim ko kuwa dai sacen ta yayi dagaske. Dafe kai yayi cike da tashin hankali kwata kwata yarasa ta yadda zai bullowa lamarin, wayarsa Da mubarak sunyi dashi cewa karya damu gobe zai baza yan sanda a gari neman duk inda take, for now ya ya bari ayi daurin auren ba tare da tashin hankali, dan kuwa muddin hajiya taji labarin abunda ake ciki saidai kuwa afasa auran. Da wannan shawarar Mujahid yadan samu nutsuwa kadan.

***

Washe gari Mom bata nunawa kowa abunda ake ciki ba, yaken dole kawai take ana buduri, ita duk atunanin ta ba bata Salma tayi ba aganinta su Hajiya suka dauketa dan su nuna mata iyakar ta, babu abunda tace da Daddy har aka daura auren su kowanne abisa sadaqi dubu hamsin, bayan Daddy ya dawo ne yace da ita tama su Hajiya waya yakamata ace Salma ta dawo, yafiso  ya mikata gidan miji dakansa. Toh kawai Mom tace dashi saida taga yabar gurin tadau wayar Salma kiran nambar Mujahid.

Gidan Mubarak su Mujahid dasu Abdul suka nufa bayan an daura aure, ko wanne su sanye da tsadadsiyar shadda sunyi kyau barin ma Mujahid dayafi su kyau da kwarjini, da ganin fuskokin su babu walwala tattare da ita saidai ango duk yafi shiga kidima ganin tun safe samun inda Salma take yaci tura kasancewar yan sanda kusan ashiri da aka baza nemanta basu ganta ba.
Nisawa Mubarak yayi yace "Mjay kasan abunda zamuyi ?"
Kallonsa yayi ido yajir, Mubarak yacigaba "kawo namban ta muyi tracing Gps device din ta dan sanin exact location nata"
Tsaki Mujahid yaja yace "wannan idea din is of no use, wayarta na gida gurin momcy dinta, nifa am sure dan Iskan nan yasan inda take y not kayi kama shi kayi torturing dinshi tunda ni am out of the force"
Dariya Mubarak yayi.
"Taya zan kama Salim without concrete evidence, you're crazy sai kace nina aikeka ka kwafsa"
Abdul ne yace "anyi mai wuyan ai, auran"
Harara Mujahid yakai ma, aranshi yana fadin ina dadi babu matan.
Mubarak yace "kaga there is nothing i can do, addua zamuyi Allah ya bayyana ta, kuma dole su Hajiya susan abunda ke faruwa"
Magana Mujahid zaiyi wayarsa tahau ruri, dubawa yayi yaga namban salma, da azama ya dauka, Muryar Mom yaji tace "ina fatan dai ka fito da ita aduk inda kuka boyeta ?
Ruwan ne ya cinyesa, kasa magana yayi sai kuka daya fashe dashi, haushi ne ya kamata ta katse wayan.
Kallon yayi cike da tausayin kasan, Azabure kuma ya mike daga inda yake zaune ya kalli Mubarak yace "na tuna akwai agogona na office gurinta saidai bazan iya accessing gps din device dinba saboda password dinsa na office is blocked, i need your password da tab dinka"
Mamakine ya kama Mubarak, ya zaai yabata agogon shi na office wanda manyan maaikata kadai ke da acces dashi, kuma ma ai yakamata ace yayi submitting agogon tun randa Sir Ahmed ya bashi suspension, kodayake yanxu agogon zai iya amfani indai tana tare dashi, tsaki Mubarak yaja yace kai banza ne wlh, mikewa yayi yadauki tab dinsa dake kan table sannan ya

mika mai yana kaimai harara, su Abdul kam dariya abun ya basu.

Lekowa haraban Gidan Salim yayi, saida ya tabbatar babu kowa sannan yaja akwatin sa ya fito waje, bakin mota ya tsaya ya karewa gidan kallon karshe, sannan ya bude boot yasa akwatin ya zagaya yazauna cikin motar, tagumi yayi yahau tuna yadda Daddy ya taimake sa lokacin da bashi da kowa yq dauko shi daga tsumma ya kawo sa gidan tun yana karami harya girma ya zama wani abun, Saidai soyayya Salma ta ruguzamai rayuwa kuma baiga zai iya hakura da ita ba. Hawayene ya zubo mai cike da tausayin kansa, atake yaji wani irin ciwon kai ya tsiga reshi, da sauri yasa hannu cikin aljihun rigarsa ya ciro wasu jajayan kwayoyi kusan kuda takwas ya afka abaki hade da hadiye su, wani irin buguwa yaji cikin kwakwalwaraa sannan kuma alokaci guda yaji sa ya dawo normal, Ajiyar zuciya ya sauke ya kunna motar ya fice daga gidan.

****

Wani dattijo mai kimanin shekaru hamsi da hudu ne zaune cikin motar sa dake fake bakin gate din gidan Hajiya, yafi minti talatin zaune yana saka da warwaran yadda zai shiga gidan, idan bai manta ba last haduwan su da Hajiya kusan shekaru goma da suka wuce, rannar da suko gidanshi a gombe ya masu rashin mutunci akan karsu kara zuwan mai gida yanzu kuwa gashi ya dawo cikin hayyacin sa yaran kawai yake son gani ya nemi gafarar su, musamman Salma daya yayi mugun bakan ta mata. Kukan nadama ne ya kufce masa, saida yayi mai isar sa sannan ya fito ya tunkari gate din gidan, gaisawa sukayi da Mai gadi sannan yace mai yamai iso gurin Hajiya, maigadi kam ganin mutumin yamai yanayi da yaran gidan yasa shi cemai ya shigo ciki bara yaje ya kira mai Hajiya.

Hajiya kuwa sai hidima take da bakin da suka zo daurin aure, su Aunty Bilki na daki tare da Junaina da wasu yan uwa suna ta zolayar ta, ita kuwa sai wani kuka da langwabewar shagwaba take, Annah ce ta leko dakin jiki ba laka, ganin Hajiya bata ciki yasa ta komo palo ne manta, jamaa sai janta suke ta hira batako kalle su ba,
Bata ganta ba, daga can kitchen ta jiyo muryar ta, da azama ta shiga kitchen taja ta suka fito waje inda babu jama'a.
"Annah lafiya kuwa ? Hajiya ta fadi tanai mata kallon tababbiya, ta lura jiya zuwa yau Annah bata cikin wani walwala.
Kuka Annah ta fashe dashi tana fadi mata karyan aikan Salma da tayi da kuma sanarwa mujajid gaskia da tayi, Salati Hajiya tayi cike da tashin hankali, right under her nose abubuwa sun faru bata da labari, wayarta da hannuta tahau kiran Mujahid dashi, shuru no amsa. Hakalinta ne ya kuma tashi, bata sanda tahau Annah da masifa ba tsabar takaici, Annah kam kuka take tana fadin "wlh duk laifi nane, kila ma yan yanke suka kamata, ashaa tama mutu kila"
Ran hajiya ne ya kuma bashi, magana zatayi taga mai gadi ya kusanta gurun su, da sauri ta karasa garesa tana tambayar sa ko yaga Mujahid, shikam bai amsa tambayar taba yace "Hajiya kinyi bako, wai Alhaji babangida daga Gombe ?
Ras gabanta ya fadi, Annah ta gane waye hakan, kallon Hajiya tayi baki wangale.
Daskarewa sukayi gurin ba tare dasun san ya karaso gurin ba, sai jin muryar sukayi cikin Sallama, atsorace suka kai dubansa garesa nan take annurin fuskan Hajiya ya dauke.

"Babangida ina fatan dai ba daurin aure kazo ba, dan tuni madaurin auren uban yaranka ya daura"
Jikin sane yayi sanyi, baiyi mamaki ba tunda yasan yammatan sunkai aure, kuka ne yazo mai ya tsuguna baiwa Hajiya hakuri, bata sauraresa ba ta juya zata koma suka ji muryar Junaina ta fito da gudu tana kiran Hajiya, da gudu ta karasa gurin cikin haki tana fadin "hajiya kinji su Aunty biliki wai dole sai anmin kitso kanana nikuma bana so" karshe maganar tayi tanai bin ko wannen su da kallo ganin bama fahimtar abunda take fadi sukayi ba.
"Yar auta ta haka kika girma" babangida ya fada yana kallonta, kallon shi tayi kaman taso gane shi a hoto, Annah ce ta katse mata kallon da cewa "ke Abban kune"
"Abban mu" junai ta fada cike da murna, ita kan burinta bai wuce taga Abban taba, da sauri taje ta rungume shi cike da farin ciki, kuka sosai Abban su yafashi dashi, Shuru Hajiya tayi tana kallon su idonta cike da hawaye tunanin ina Salma ta shiga take aranta.

Gidan Salim

Salma bata samu runtsawa ba sai bayan sallah Asubah wani mugun bacci ya sace ta, sai after 1 ta tashi da matsanan cin yunwa, ruwa kadai ta iya sha tayi  alwala tayi salllah azahar sannan ta koma kan gadon ta kwanta, wani red light taga yana blinking jikin agogon hannuta bata damu ba ta share tahau Tunanin Abbanta da gidansu a Gombe da yadda tayi zaman kanta a gudin tun bayan da abba ya rabu da Amminta sanadin Aunty jamila daya aure ta mallakesa da sai yadda tace zaiyi karshe ma Abba dakanshi yace mata tabar masa gida taje ta nemi dangin uwarta, shine ma dalilin zuwan ta Abuja, bata san kowa agarin ba Allah ya hada ta da Daddy ya taimake ya riketa amatsayin yar cikin sa, Nisawa tayi tace "Allah ya kare ka Abba daga shairin Aunty, nasan bayin kanka bane" shuru tayi tana ayyana idan tasamu hanyan guduwa Gombe zata koma gurin Abbanta.
Around 3 taji motsin ana shigowa, mikewa tayi zaune adan tsorace, Salim ne ya shigo, farar fuskar sa jajir, da ganin sa ba cikin hankalin sa yake ba, cike da karaji yace "ke tashi mu tashi, flight din 5pm garemu"
Tausayin sane ya kamata ganin yana yinsa, tagane yayi high da yawa, cikin sanyi murya tace "yaya you need a doctor, na yadda zan bika amma kabari muje aduba ka, you're really sick"
Wani mugun kallo yakai mata da saida taja baya, Bindigarsa dake aljihun bayan rigarsa ya ciro afusace ya nunata dashi yana dariya yace, "i won't allow you take me for a fool, Get out out.."
Atsawace ya karashe maganar.
Dan ihu tayi ganin dagaske zai iya pulling Tigger, tace "yaya zan bika Ghana, amma dole muje asibiti"
"Yarinyar nan wasa kike dani" ya fada, deawer ya bude ya ciro wasu drugs daban dake cikin wani white container ya ciro pills da dayawa ya apka abaki sannan ya kalle yace "Get out, before i pull d trigger.."
Haushi ne yakamata, dan kuwa tsoron ma ta daina ji, tace "babu idan zani, kuma nasan you wont try killig me kaida ko kwaro banga ka taba kashe wa ba".
Kecewa yayi da mugun dariya sannan yace "salma it all your fault you made me become a killer, saboda ke na kashe Babanayaro mistakely, dan haka you wll be stock with me foreva"
hannu yasa ya fizgo ta batare daya damu da state of confusion data shiga ba, innalilahi kadai

Salma ke ambata sai yanxu tagama gane ba sonta yake ba he is only obsessed with her.
Ihu tahau yi yana janya waje, gate din ya bude ya jata bakin mota taki shiga, kokarin turata ciki yayi ta gantsara mai cizo, wani mugun mari yakai mata saida ta fadi kasa hade da zakin razanannan ihu, hannusa yasa zai damko wuyanta ya lura da agogon hannunta dake blinking Red light.
Ware ido yayi in shocked, ya daga ta tsaye afusace yana fadin "gidan uban wa kika samu agogon nan?
Yawu ta fota mai a fuska, tace "you're insane" sannan tayi kokarin warce kanta ta ruga da gudu zuwa bakin gate din dake hangame, saita ta yayi da bindigar yace "dont you dare leave this house".
Stand still tayi gabanta na faduwa, takowa ya farayi gurinta suka ga motocin Yan Sanda ya diro gurin, motar dake biye dasu kuma Mubarak da Mujahid ke ciki, da sauri suka fito daga mota akidimi.

Salma na gani Mujahid ta rugu ta fada jikinsa tana kuka, shima rungemeta yayi yana kukan yana kara bata hakuri.
Salim kam is shocked, da abunda idansa yagani, ransa ne yabaci aganinsa Salma ta kara yaudaran sane ta hanya fada masu inda ya kawota, bai lura da jinin daya fara zubowa daka hancin saba ya kuma saita bindigar kansu.
Yan sanda dake gurin ne suka ce yayi surrender, ko kallan su baiyi ba balle yayi surrender.

Hankalin Salma ne ya tashi, tayi saurin saki Mujahid, kallon Salim tayi, hanci sa na bleading sosai tace "ya you need so help, plz stop acting crazing muje asibiti plz..." Kuka ta fashe da dashi tana rokansa, amma ina shikam bata kansan yake ba, so yake kawai ya harbe Mujahid dan kishi, takowa Salma zatayi garesa Mujahid yayi saurin rikota yace "he is crazy, dont move further.."
Kallan sa Salma tayi, murya kasa kasa tace "he is my brother, i dont wanna lose him"
Dariyar dayafi kuka ciwo sukaji Salim yayi yace "indai shi kika zaba na gwammace ki mutu kowa yayi asara" harba bindigar yayi saitin Salma ayayinda yaji karfin jikinsa ya kare ya fadi nan kasa, jini ta hanci da kunne, cikin zafin nama Mujahid ya tureta bullet din ya same shi, nan take ya fadi kasa wanwas babu rai ai jini dake ambaliya ta baki, Ihu Salma tayi, Mubarak yayo kansa gadangadan, sauran yan sanda kuma sukayi kan Salim.

Ihu Salma take tana kuka tana jijiga Mujahid, amma ina bai ma san tana yiba, halinkali tashe Mubarak ya ba yan sandan oda aka dauke su biyu cikin Mota, Salma sai kuka take tana rokon mujahid Gafara, duk itace sanadin komai, kuka sosai take har suka isa asibiti aka wuce dasu Emergency.

Salma kam kuka jikinta ya gama gayamata Mujahid dinta bazai farfado ba, dakyar Mubarak yahau Lallaba ta rage kuka, wayar Mujahid dake motarsa yadauka ya kira su Hajiya ya shaida masu suna asibiti, sannan ya karbi namban mom gurin Salma suma ya sanar dasu abunda ke faruwa.

Baa fi minti 30 ba kowa family ya hallara agurin, tsabar Kidima Salma bata ma lura da Abbanta dake tare da Junaina ba, Jikin Momy ta fada tana kuka mai tsuma Zuciya, Kowa kallan ta yake cike da tausayi, Annah sai ihu take tana fadin shikenan Jikana ya mutu tun banga tattaba kunne ba, haushi ne yakama Hajiya tahau rokonta tayi shuru saboda asubiti ne kuma ana iya koronta.

Doctor ne ya fito cike da tashin Hankali, da sauri Jafar da Mubarak suka karasa gurinsa, hankalin sauran kuma ya koma kansu.
Zufa Doctor ya share yace "Allah yayi dayan su rasuwa tun kafin ma su iso asibiti.."
Salati ko wanne su dauka cike da firgici.
Dakyar Salma ta iya sakin Mom, bakin na rawa tace "Doctor waya rasu cikin su ?
Dogon Ajiyar zuciya Doctor yayi sannan ya kalli Mubarak yace "Suwaye Family din wanda aka Harba ?
"Gasu nan" Mubarak ya nuna su Momy da sukayi wiki wiki da ido, tuni jikin Salma yahau rawa.
Girgiza kai Doctor yayi yace "Am sorry....
Bai karasa maganar Salma ta saki wani irin ihu tayi tangal tangal zata fadi Abbanta yayi saurin taro ta hade da kwalla kiran sunanta da "Ummi"
Hade ido sukayi, zatayi magana ta fadi jikinsa sumammiya.

Happy Sallah in Advance😍

Last page ya rage mana, Insha Allah.
[9/7, 12:38 AM] Xarah Bukar: Zuma Sai Da Wuta

~na~
©χaraɧ bųkar
(Aunty Cute)

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION {NWA}

Wannan littafin Gabad'aya na Sadaukar dashi ga kawar arziki *Aynarh Dimples* Allah ya barmu tare, LYSM😍
Ana Bahebak ❤❤

Allahu akbar kulu'nafsi za'ikatu mauti, Allah yaji kanki da rahma Maman besty Yar ficika. May jannatul Firdausi be ur final destination.

Last page

Hankalin kowannan su kara tashi yayi, akidime su Hajiya sukayi kanta tare da Salati, saurin dakatar dasu Doctor yayi ganin suna neman maida gurin kasuwa, Nurses biyu ya kira suka shiga da Salma wani daki dan samun nutsuwa da dawo wa hayyaci, Annah kam kuka take rusawa tana ihun jikanta ya mutu. Takaici goma da ashiri ne ya kama Doctor yace dasu Jafar da Mubarak su iske sa office dinsa, da azama suka mara mai baya suka shiga suka zauna cikin kaguwa dason sani abunda zaice. Duban su Doctor yayi cikin nutsuwa da hankalta, yace "Alhamdulilah dan'uwanku yayi surviving gunshot din, thanks to Allah komai yazo da sauki mun samu mun cire bullet din, but he is still unconscious"
Ajiyar zuciya na relief su Jafar suka sauke, Mubarak yace "Salim fah, miye condition nasa ? Nisawa Doctor yayi yace "am sorry we lost him tun kafin ku karaso asibiti saboda drugs dayay using, he died of a heroin overdose,"
Mubarak kam baiyi mamaki ba dan kuwa yasan Salim baya rabuwa da harka miyagun kwayoyi, Jafar kam jikinsa ne yayi sanyi yadda komai ya faru acikin kankanin lokaci,
Doctor yace "yanzu dare yayi, sai zuwa gobe zamu saki jikinsa"
jiki sabule suka koma gurin su Hajiya dake tsayuwan Jimami, nan suka zayyane masu yadda Doctor yace, duk da bawani sanin Salim sukayi ba mutuwar tai mugun girgiza su (sabon Kabari mai karasa tsoron Allah), Mom kam kuka tahauyi abun gwanin tausayi, su Daddy da hajiya suka hau bata baki. Haka suka bar asibitin jikin sanyaye banda Hajiya da junaina da suka zauna jiran fardadowan Salman da mujahid. Washe gari aka mika Salim gidan gaskia. Da yamma Salma ta farka cikin matsanan ci tashin hankali, dakyar Hajiya ta kwantar mata da Hankali dacewa mujahid nanan kalau, saidai fadi mata rasuwar Salim yasa ta kuka matika, sosai Junaina taji tausayinta sai yanxu tagane tanason yayarta haushi abunda tayi mata yasa take nuna mata kiyayya, Suna cikin haka Abban su ya shigo, mikewa Hajiya tayi ta fice dan basu guri, kuka shima Abban ya fashe dashi yana neman gafarar su, atake suka ce sun yafe dan kuwa hannuka bai rubewa ka jefar, cikin shesheka Salma ta tambaya shi ina aunty Jamila, yace da ita ya jima da rabuwa da ita tunda yagano asiri take bashi cikin abinci. Sosai yaran sukaji tausayin abbansu, dan family reunion sukayi a dakin cike da farin ciki.

Bayan kwana biyar.

Acikin kwana kin kullum Salma makale take adakin Mujahid tana jiran farfado warsa, kusa dashi zata zauna tayi ta kallon kyakyawan fuskar sa dake sanye da robar oxygen, wataran tayi kuka wataran kuma tayi ta zuba mai murmurshi kamar wata zautacciya. Zuwan Faiza Uku duba Mujahid, saida ba dawata manufa take zuwa ba face amatsayin daya bata dan tunda ya mata zancen auran Salma yasa ta kame kanta tafara nemawa kanta bazawari, yanxu kuwa Allah yasa tadace wani chairman na karamar hukumar Tafa ke nemanta.
Yau Doctor yayi assuring dinsu Farfadowan Mujahid dan kwana biyu kenan da ciremai oxygen, lafiya kalau yake mayar da sauke numfashi, babu kowa adakin sai Salma dake zauna kan gefe gadon tana dubansa, murmushi ta saki takai hannu bisa gashi kansa ta shafe zuwa

fuskarsa aranta tunanin ranar dazai tashi, bata taba expecting xai yi risking life dinsa to save her ba, Murmushi ta kuma saki tace "am sorry, it all my fault" kanta ta daura a fadadan kirjin sa tanai jin heart beat dinsa dake fita, lumshe idanu tayi, cikin dogon bacci da yake yaji dumin ta jikinsa ahankali yayi bude ido ya daura ta kansu, saurin runtse ido yayi saboda yadda yaji wani irin yanayi, left hand dinsa dake ajiye gefe ya daga ya daura bisa kanta, adan tsorace ta zabure zaune ganin tayi idonsa kulle, hannusa ta janyo ta rungume tana kallan sa, cikin sanyi murya ta kira sunan sa, bai amsa ba, kaman zatayi kuka ta cigaba da dubansa, kofar dakin aka turo yasata saurin mikewa tsaye cike da kunya ganin Hajiya ce, "Ya tashi ne ? Hajiya ta tambaya cikin kota kula da yanayin ta...
Sinne kai Salma tayi sai kuma ta dago ta dubi Mujahid taga Idansa bisa kanta, kunya ce ta kuma kamata, batace komai ba tafice a dakin da sauri har tana harde kafa.
Murmushi Hajiya tayi ta karasa gurinsa cike da farin ciki ya farka, magana zatayi taji yace "miyasa ta gudu, plz kice ta dawo bangaji da ganin taba" awahale yayi maganar.
Dan duka Hajiya takai mai cikin wasa tace "marar kunyar banza, saika bari ka murmure ai" dariya yayi ciki ciki yace "ina sonta alot".
Tsaki Hajiya tayi
"Ka manta sanda kace ko akafa aka daura ma baxaka jaba, toh kasani koka warke babu kai ba ita" in serious tone Hajiya tayi magana.
Tsurewa Mujahid yayi, yahau bata hakuri, banza tayi dashi ta zauna kan kujerar dake gurin, saida taka yana neman kuka sannan tace mai wasa take.

Agurguje filis.

Bayan kwana hudu ne Aka sallemi Mujahid gida, duk haduwan su da Salma babu mai cewa juna uffan, ya lura wata sabuwar sarar jin Kunya Salma ta tsiro dashi wanda tun abaya bai santa dashi ba, wataran bacci karya ma yake idan yaji shigo wanta dukda yaji kalaman soyayyan da take rangwada mai amma daya runtse take mazewa tamkar ba ita ba.

Gidan su Mom Salma ta koma da zama, hakan bai damu Abbanta ba, dan kuwa yaji dadi yadda Daddy ya riketa tamkar yar cikinsa, Su Junaina tuni su Aunty Bilki suka kaita gidan Jafar kaduna, hankalin su kwance basu da wata matsala.
Satin Salma uku agida Daddy yace zaman ya isa haka, dama abunda take jira kenan dukda ma ba waya suke da Mujahid ba amma ta matsu ta ganshi, ta bangaran Mujahid shima hakan ne akullum sai yama Hajiya Magiyan yaushe zaa kawomai Salma saidai kawai ta share shi taki tanka shi, sauki daya samu ma ya koma bakin aikin sa.
Daddy da kanshi ya kaita Gidan Mujahid bayan tasha fada da nasihohi iri iri da uban kwarai kema diyarsa.. Komai na gidan saida aka canxa sabo, Daddy da abbanta sunyi kokarin zuba mata tsadaddun kayan alatu. Bayan daddy ya tafi zaman shuru tayi da kadai ci koda Mujahid ya zo ya isketa babu wata magana dana shiga tsakanin su face gaisuwa, kowanne su dar dar yake da juna gudun kar ran wani ya bacci azo ana yar ramuwar gayya, dakuna daman uku ne agidan ko wanne da nasa dakin, haka sukayi ta zaman babu ruwan wani da agidan, idan Mujahid ya tafi aiki haka zata zauna tayi ta kewansa, da dare kuwa yana dawowa zata gudu daki ta zauna, daya shigo yaji kamshin ta a palon yasa barin palon tayi, murmushi kawai zaiyi ya wuce dakin

sa.

Bayan wasu kwanaki, yau dawuri Salma ta tashi ta fita palo jiransa fitowar sa, so take tacemai sun koma skull zata fara fita, kamar munafuka ta takure da zumbulelan hijab.
Hankali kwance ya fito daga daki yana adjusting hulan sa na uniform din police, sai ganinta yayi jugum zaune, baice komai ba zai wuce tayi saurin mikewa tsaye hade da risinawa gaidasa, fuska ba yabo ya amsa, wucewa zaiyi yaji tace "uhmm zan fara zuwa skull gobe, munyi resuming"
Dariya ma tabata shi, wai uhmm yau kodan yaya babu, kallonta yayi, sosai ta bashi dariya da Hijab din, tuna sanda take sa kayan dake bayyana gaba daya jikinta yayi, kwafa yayi baice komai ba ya fice yana tunanin wai Salma da yakeso ta taba zubar da ciki, kodayake koma miye i still love her like dat.

Ajiyar zuciya Ta sauke ta koma ta zauna, tana son Mujahid saidai tafiso yafara sauraran ta kafin ta iya sakin jiki dashi, dan har yau takasa manta abunda Khaleel ya fada nacewa koda mujahid bai sont zai ji dadin hutuwa da jikinta, she need to know ko yana sonta dagaske.

Washe gari around 9 Salma ta shirya, yauma hijab din tasanya, Mujahid dakanshi ya kaita skull sannan ya wuce office, by 6 ne zai dawo daukan ta, mis taje tayi registration sannan ta tafi faculty dinsu taga time table harya fito kuma alokacin ma lecture garesu, hankalin tane ya tashi dan anyi 1 hour da farawa, da sauri ta nufi Hall din, ganin Faiza ke masu Lecture din yasa bata shiga ba ta tsaya bakin kofar, daga ciki taji Faiza tace mata ta shigo, jiki ba kwari tafara takawa ciki atunanin ta dizga ta zatayi sai kuma taga sabanin haka, direct gurin da mata ke zaune taje ta zauna, yan aji sai mamaki suke dan sunsan bata da gurin zama saida maza, su shehu kam so suke kadai suji ko dagaske tayi aure dan sunji labari a gari, Around 6 suka gama lecture da sauri ta fito ta tsaya inda Mujahid zaizo ya dauke ta, saiga su Shehu da habib su karaso gurin da fara'arsu, Shehu ne yahau tambayarta ko dagaske tayi aure, Daure fuska tayi, aranta tana rokon Allah kar Mujahid yaganta saidai mi bata gama adduar ba saiga motar sa ya iso gurin.
Habib yace "Salma kinyi shuru.."
Gabanta ne ya fadi gani ganin Mujahid ya fito daga motan, su Shehu kam saurin barin gurin sukayi ganin wani mugun kallo dayake watsa masu.
Fuska ba annuri yace da ita "kinyi auran ma bazaki fita harkar suba"..
Kuka ne ya kufce mata, cikin rawar murya tahau bashi hakuri, bude motar tayi ta shiga tana sharar kwalla, shima shiga yayi yaja motar, bamai yiwa wani magana har suka isa gida, da sauri Salma ta fito ta fada ciki.

Kowa dakinsa ya wuce cike da tunani kala kala, around 10 yana kwance kan gado rabin hankalinsa nakan Salma, sam baya son zaman da suke kamar ba masoyan juna ba, mikewa yayi ya shiga dakinta, can karshe gado yaganta zaune da nitie, da alamun ma kuka take.
Tana ganinsa ta diro kasa, cikim kuka tace "yaya kayi hakuri, wlh ba harkar su nashiga ba, tambayana suke ko nayi aure"
Hannusa yasa ya dago ta suka zauna kan gadon, cikin wata sanyin voice yace "ya isa haka, banason kuka"

Kukan ta cigaba dayayi ya janyo ta jikinsa yana lallashi ta, fuskar ta yadago suna fuskan tar juna, yace "it okay"
Kai ta girgiiza alamar toh, suka cigaba da staring at each other, ganin tayi idanuwan sa sun fara canxa wa yasa tayi sauri matsa da jikinta da kawar da fuskar ta, janyota ya kuma yi, kaman zaiyi cry yace "i know i hurt you alot, plz forgive me"
Hawaye ne ya zubo mata, tace "yaya nayafe maka, kuma bakamin komai ba, saidai.." Shuru tayi.
Yace "saidai mi"
Tace "yaya you dont love me, according to ya Khaleel i tink jikina kakeso danka huta"
In shocked ya kalle ta, yace "ke kinsan datx a big lie, you know i love you alot, plz biliv me".
Kuka tafashe dashi ta fada cikin kirjinsa, tasan kam Mujahid ba karya yayi ba yana sonta amma kawai takasa gasgasta hakan, shikam gabadaya ta gama Rikita shi da kamshin jikinta, kissing wuyanta yafara yi tayi sauri dago jikinta jin wani irin yanayin, kafin ta ankara taji lips dinsa anata yana kissing da sauri ta zabure tsaye gabanta na faduwa, cikin kuka tace "plz go, bacci nakeji"
Murmshin daya fi kuka ciwo yasaki yace "you still dont trust me ko, kin dauka jikinki nakeso, ba komai i wont dare touch you until d day you trust me" atakaice yayi maganar ya mike zai fita, jikinta har wani rawa yake, sam bataso taga ran shi ya bacci, da sauri ta sha gabansa hade da fadawa jikinsa tace "yaya I trust you with all my heart"
Kallon ta yayi sonta na kara ratsa mai gabobin jikinsa, riketa yayi suka shiga toilet yace tayi alawa, ma masu tayi, shima yi yayi suka gabatar da nafila game da yiwa Ubangiji godiya, Jikinta sai bari yake, hannuta ya riko suka koma kan gadon, tausayi tabashi ya mike zai fita tayi saurin rikon sa tace "plz dont go"
Zama yayi hade da janyota jikinsa yana shafar bayanta, daga nan kuma dan peck yakai mata a goshi yafara kissing dinta, itakam kuka kawai take, tuni ya fara shigar da ita wata duniyar da zafafan salon wasa da hot kisses daya ke kai mata ta ko wana angle na jikinta, hannusa taji yakai kai kan boobs da sauri ta runtse ido, cikin wani salon marar misaltuwa yahau rubbing dinsu kafin daga bisani yakai bakinsa yana....
Gabadaya ya gama birkita kukan tane ya tsananta tahau kokarin turashi, shikam ina yayi nisa baya jin kira dan kuwa baima san tana yiba sama tsananta abunda yake mata yake, rokanshi tahau yi akan ya barta nan haka nan, shikam yayi nisa, addaur saduwa da iyali yayi yafara luluwa duniyar da ba kowa ke zuwa ba sai ma'aurata.

Tun Salma na kuka har saida sautin kukan ya daina fita kasa saurara mata yayi saboda yadda yaji ta zamzam dukda baiyi tunanin samunta haka ba, wani irin dadi ne ya ziyar ceshi, ga ruwa niima na ambaliyo mata yakara sashi fita hayyacin sa, saida suka kwashi lokaci da dama sannan ya sarara mata, hhh su Salma anji maza.

Agigice ya mike kanta ganin aika aikan daya aikata mata, "omg" ya furta yana taba jikinta daya dau zafi sosai, ba bacci take ba amma daganin ta yasan idanta biu, tausayinta ne ya shige sa hade da haushi kansa da yayi tunanin ta xubar da mutuncin ta awaje, mikewa yayi ya shiga toilet ya hada ruwan zafi, ya fito ya dauketa like bby ya kaita ciki ya tsunduma, wata yar kara ta saki, lallaba ta yahau yi ayayinda sai zuba mai shagwaba take, saida yaga ta gasu sannan ya diba mata wani ruwan ya fita dan tayi wanka, komawa dakinsa yayi ya fada toilet yayi wanka ya

fito ya koma dakinta, kwashe ya ganta a akasa kudundune cikin towel, da sauri ya karasa ya dauke ta zuwa dakinsa, sai kuka take mai kasan ta ciwo, magani na pain relief ya ballo ya bata tasha..
Ranar kam tasha gata, dakyar ta samu suka runtsa, shikam Mujahid har kuka farin ciki yayi yana shi mata albarka, wani sonta marar misali yakeji game da ita a zuciyar sa.

***

Life goes on, zaman soyayya da mutunta juna suke, duk wani abun dazai batawa juna rai kawar wa suke, yau da wuri Mujahid ya dawo gida saboda Salma na laulayi, asibiti ya kaita aka bata magani sannan suka dawo gida, sai wani langwame mai take yana biyeta, kwance take bisa kirjinsa yana shafar cikinta da yayi kusan 6 month.
cikin wani salo ta kalle shi tace "yaya i have a confession"
Murmushi yayi yace "basai kin fada ba, nayafe"
Dariya takai hannu side drawer tadauko pink bag dinta data bari a motan Jafar da dadewa, daga baya ya bata jakan, ta boyesa bata cire hoton mujahid data dauke a office din Faiza ba Bude jakan tayi ta ciro hoto tace "yaya ka tuna da pic dinnan ?
Kallon hoto yayi, yasan Faiza ya taba ba hoto, saidai baiyi mamaki ba dan kuwa faiza tace mai batagani ba.
Tace "before i met you, pic din nafara ganin office din Malama, i tot ko matar kace first tym da muka hadu"
Chakulan ta yayi a kumatu saida tayi dariya, yace "no wonder ranar you were angry ashe kishi kike bansani ba, oya bani hoton na maida mata abunta" hannu yasa zai karbe tayi saurin boyewa karkashin ta, bata rai tayi tace "ban yadda ba, naji ance ma tayi aure shine baka gayyace ni bukin taba, naga kai babban abokin ta"
Dariya sosai tabashi, shi tunda faiza tayi aure ma basu kara magana ba, yace "toh tashi muje mu gaishe ta"
Make kafada tayi hade da turo maki tace "ni bazani ba kuma kai baza kaba"
"Ai baki isaba sai muje" ya fada cike da zolaya, ita kuwa sai salo take zubamai, wayarsa ce tayi ringing ya mike tsaye ya amsata, Hoton ta ciro tana kallo tana tunanin inda bata Hadu da Mujahid ba da har yanzu tana nan as Salma ta ada wanda ubanta ya sallama taso sallama kanta a duniya, su shigar banza nan da hulda da maza yan daba, da rashin mitunci da take ketawa yau gashi Allah ya shiryeta duk da ma dai ta wahalu hannun Mujahid amma ta godewa Allah Dayasa shine masoyinta.
Hannusa taji bisa nata, dubansa tayi fuska shagwabe, murya kasa kasa yace ajiye hoto tunda gani kusa dake.
Turo baki tayi "Nifa bakai nake kalla ba"
Kwakwayan maganarta yayi yana dariya, mitsini takai mai ta fada cikin sa tana gunguni, murmushi yayi ya tallafo ta yana shafar cikinta yace "i love you both"..
Lumshe ido tayi ta kuma shigewa jikinsa, cikin sanyi murya tace "we love you more..."

Su Annah ana can sai dirgan lokacin zuwa Suna take, murna take zata samun tattaba kunne dan kuwa Junaina na ma tsohon ciki gareta, haihuwa yau ko gobe.

*End*

Alhamdulilah, kurakuran dake ciki Allah ya yafe min.

Bana jin Dadi Jikina, ku tayani da Adduaa.

Sai kun jini a sabon littafina *Alhaji*

Godiya gareku masoyana, Allah yabar kauna.
Ameen.